Compiled By Umar Dalha Funtua.

♦♦♦
*SANGARTATTCE*♦♦♦

Maman Abd Shakur

1...
Free page

Da Sunan Allah Mai Rahama Mai Jinkai.

"wayyo Allah na Baba mutuwa zanyi, wayyo Mama huramin cikin" mata biyune suka zagayeta akan tabarman dawasu yara mata guda biyu dake tsakar gidan dayasha simenti kal kal dashi duk sunyi zuru zuru, kana ganinsu kaga tashin hankali kwance akan fuskarsu, chan ta gefen tabarman kuma wajajen inda kafanta yake wani dan tsohone haka dake sanye da babbar riga dakuma yar hula daya zagayeta da rawani irin na malamai dinan ya rike kofin silver yakara abaki yanata addu'o'i aciki anatse, ihu takara yi ta dage rigarta sama tabude daidai cikinta dake nan kaman bata tabacin abinci ba, ta gefen haggun cikin ya dan kumbura idan kaga wajen saika rantse wani irin babban kurjine yafito ya kumbura haka yay ruwa zai fashe, ihu tasake yi tariko hannayen matan dake kanta tace "wayyo Allah Mamammu na shiga uku, azaba Mama wayyo, azaba yakemin" tasaki hanunsu tana ihu "Baba Baba baba kiranka nakefa, wayyyo Allah na ba banu ni" wani irin ihu take ta rirrike hannayansu gam tana nishi, wajen ciwon cikin kuwa sai balbal yake yanda kasan halita mai rai ne acikin wurin, duk ihun ta yacika gidan, tsabagen takaici ma daya daga cikin matayen wacce itace mahaifiyarta taja tsaki, hakan yasa dayar ta goge zufan datake yi agoshi, takamo fuskarta da hanunta tarike tace "haba Balkisu, iye mai gadon zinare, ki daure mana baga baban kinan namiki addu'a aruwaba, kefa mai dauriya ce, jaruma, kinga Layla da Raiyana zasuce ke raguwa cefa gashima sai kallonki suke" girgiza kai tayi tawani irin kece da kuka da ihu harda shesheka tace "ni kukiramin Baaba wlh, Baaba tazo, Baaba kizo ki taimakeni" tafara shure kafa idanun nan sunyi jajir tace "Baba, Baba, Muji, wayyo Allah na Mujittapa kuzo kutaimake ni, Shato kuzu dan Allah na shiga uku, wayyo Mama dubamin kiga kodai barkewa cikin yakeyi ne?" tawani irin buga ihu hakan yasa mahaifiyarta dake kanta ta buge bakinta da karfi tace "kewai baki iya kiran sunan Allah bane banziya kawai" daidai lokacin Baba ya cire cup daga bakinshi ya kalli Uwargidan yace "dagomin ita Zainaba" dagota tayi ahankali sai wani uban nishi take tana cije baki tace "tsaya tsaya uhmm" tsayawa tayi tana kallonta cike da tausayi, hannu budurwan tasa akan kafadar matar tareda runtse ido

da karfi tana nishi tace "tona shirya" har Mama saida tasa hannu suka dagota zaune ahankali wani irin ihu tayi kaman zata mutu "ya isa, ya isa, yayi" suka jinginar da ita ajikin bango, kafamata kofin Baba yay abaki ta kurbi ruwan sosai tasha tana kara dage rigar atampan jikin ta sama, ragowan ruwan Baba ya debo yay addu'a zai shafamata akan kullutun da sauri tarike hanunshi tana ihu tana kuka tace "Baba wlh azaba yakemin, in kanama Allah karka tabamin, kaji dan yarasulullahi" hanunta Mama dake kanta ta buge tana wurga mata wani mugun kallo, hakan yasa Baba ya girgiza kai ya shafamata ruwan awajen tana wani irin shegen ihu da duk yacika musu kunne, tashi Baba yay ya kalli mahaifiyarta ya mika mata cup din yace "bayan awa daya kikara bata Amina, bari nakoma zaure wajen dalibai" jiki asanyaye ta karba tace "to malam" juyawa yayi yay hanyar zaure bude kofa yayi sanan ya daga asabari dazai sadashi da zauren yafita, almajirai ne cike a zauren sunata karatu da alo, ga wasu manya akansu dake rike da bulala suna lura dasu, bangon zauren duk jakunkunan almajiran ne dakuma taburmai dasuke kwana akai dan zauren nada girma sosai, daliban na ganinshi suka kara karfin karatun dasuke, fita yayi daga zauren zuwa kofar gida nan ma wasu almajiran ne akan simentin kofar gidan dayawa sunata karatu da alo, anyi babbar runfa daya kare kofar gidan sabida koda ana ruwan sama dan wasu almajiran anan waje suke kwana, ga robobin almajiran cike akan dankali dan dazaran karfe biyu tayi zasu tsaya sai ayi salla kowa yatafi bara, daga chan gefen kofar gidan kuma lungu ne dayasa suka gineshi dajar kasa aka zagaye suka maida bayi, anan almajiran suke wanka suke dai komi nasu sanan a kofar gidan akwai rijiya da guga dasuke diban ruwa, zama yayi akan tabarma da aka wareshi musamman tashi ce dan akwai yar dadduma mai taushi akai ya zauna tareda yin bismilla yanajan chasbaha, yana bin kowani dalibin dake wurin yana karatu da kallo, wani dalibi babba dan yana daga cikin wayanda ke kula da sauran almajiran ne yazo kusa da malam ya zauna tareda tankawshe kafa yadan dukar dakai yace "Allah taimaki Malam, Allah gafarta ma Malam, Allah kare mana Malam" ahankali Baba ya ijiye charbin ya kalli yaron yace "sun biya karatun da kyau Isyaka?" "i sunbiya Malam, na muhammadu ne kawai bai kawo da kyau ba amma nakara maimaita mai" murmushi Malam yayi tareda kishingida da bango yace "masha Allah to, daukomin Al Qur'ani na nabarshi a zaure saika biyamin naka inji" dan kallonshi matashin yayi saikuma ya sunkuyar da kai yace "Malam ya jikin Balkisun?" ajiyar zuciya Malam ya sauke yace "da sauki namata addu'a zata sami lpy nan bada jimawaba" cike da damuwa Isyaka yatashi yabar wajen zuwa zauren dan dauko abinda Malam ya aikeshi.

Gyangyadi tafara yi anan wajen a zaune, hakan yasa duk suka sauke ijiyar zuciya, Uwargidan dasuke kira da Umma tamike ta kalli Maman Bilkisun tace "sha biyu tayi bari na daura girki Amina" kallon yaran daduk sai kallon Bilkisu dake nan zaune tana gyangyadi suke tace "ai sai atashi aje ataya Umma aiki ko" hijabi Raiyana ta cire wacce ita kebin Bilkisu shekaran ta 15 tamikama Layla hijabin wacce take auta shekaran ta 8 tace "ungo kaimin daki" karba Layla tayi ta wuce dakin su ta ijiye tafito suka karasa kitchen din jajjage Umma tasa Raiyana itakuma Layla Umma tace "tahura mata wutar ta kama" tafice daga kitchen din zuwa tsakar gida dan tankaden tuwo.
Layla dake fifita wuta ne ta juyo ta kalli Raiyana dake jajjage, ajiye maficin tayi tazo kusa da Raiyana ta tsaya kaman zatai kuka tace "Anty Raiyana maisa Baba bazai kai Anty Baby asibiti ba, kinga ko koyau a makarantar mu anmana primary science fa, ance idan abu yafito acikin ka

yay babba har yana motsi operation akeyi, Allah kuwa, Baba kuma yanata mata karatu tanasha da dafa mata ganye maisa bazaice aje asibiti ba" tunda take maganan Raiyana ta tsayar da jajjagen tana kallonta, Umma ne ta shigo kitchen din ta kallesu tace "surutun me kukeyi ba aiki nasaku ba?" baki Layla tabude zatai magana Raiyana ta girgiza mata kai hakan yasa tai shiru takoma gaban murhun tacigaba da fifita, abinda Umma ta shigo dauka ta dauka tafice daga kitchen din, hakan yasa Raiyana tadawo wajen murhun ta tsugunna tace "karki kara fadin maganan nan, Baba bai yarda da maganin asibiti ba kuma idan yajiki kinsan sauran, karki karayin maganan kinji" ahankali Layla ta gyada mata kai kowaccen su tacigaba da aikin da aka sakata.
Wuraren sha biyu da rabi ta farka azabure ta mike Mama dake zaune gefenta tana dama ma malam fura ta kalleta tace "ya cikin" hanyar dakinsu tayi ta daga labule ta kalli agogo sanan ta kalli Mama tace "Mama nakusa lattin makaranta shine baku tasheni ba" turo baki tayi tai gaban rijiya tadau botiki zataja ruwa, tabe baki Mama tayi tacigaba da dama furan ta, agurguje taje tayo wanka tafito daure da zani a kirji tashiga daki da gudu, uwar dakan su ta shiga dake nan agyare ko ina dan gado ne madaidaici sai ledan daki da aka shimfide, tsugunnawa tayi tajawo ganamasgo daga karkashin gado ta bude taciro kayan makarantar ta dake nan agoge, purple dogon wandon tafara sawa sanan tasaka rigar dayakai har gwuiwa fara tana dan bata fuska sabida yanda cikin ke mata ciwo kadan kadan yanzu ba kaman dazu ga, gaban madubi taje ta shafa farar hoda tasaka kwali, basilin ta lakato ta shafa akan pink and black lips dinta, dan lips dinta daga tsakiyar su pink ne sosai sai kasan kuma baki kaman ta shafa janbaki haka suke gashi sunwani irin tattare gwanin kyau and sexy, idan ka kalla kaman nama, komawa gadon tayi tasanya farin hijabin daya wuce gwuiwa, ta maida ganamasgo karkashin gadon tadau yar jakarta da litattafan ta keciki tafito ta zauna adakalin bakin kofa tana kokarin saka safa da takalmin makaranta Umma da fitowar ta daga kitchen kenan tace "Baby yaushe kika warke dahar zaki tafi makarantar allazi boko?" dan murmushi tayi daya bayyanar da beauty point dinta tace "Umma yafa dena fa wlh, kuma kinga nice monitor aji chalk natare dani dole nakai" baki Umma ta kama tace "su manito manya" dariya Balkisu tasaki harda fadawa jikin Mama dake kan tabarma tace "ana monito kina manito Umma" tacigaba da dariya kaman ba ita ke ihu dazuba, rankwashi Mama tasakin mata akai tace "tashi min akan jiki kafin na juye miki furan nan akan kayan makarantar nan" ahankali ta tashi kaman zatai kuka ta zauna kusa da ita Umma ta bude kullin zani taciro naira hamsin ta mikamata tace "gashi kihau mota, daga fillin mallawa zuwa dogon bauchi da shegen nisa keda baki da lpy" karba tayi cike da murna tace "nagode Umma na Allah barmin ke" komawa tayi kusa da Mama tana kallon furan, kaman zatai kuka tace "Mama dan sammin kinga ba'a gama abincin rana ba karnaje makaranta haka da yunwa" hararan ta Mama tayi tace "kwadayayya" dariya tayi tace "eh naji Mama kidan ban" da sauri ta shiga daki ta dauko karamin kofin roba Maman ta tsiya mata dan daidai ta shanye harda saka yatsa tana kakkale kofin ta lashe tass sanan ta ijiye kofin tana goge baki tace "nagode Mama natafi" da sauri tadau jakarta ta leka kitchen taga su Raiyana na kwasan tuwo tace "natafi" atare suka mata addu'a, Mama tace "salla fa?" "a school zanyi Mama" tabude kofa sanan ta daga asabari tafita.
[7/15, 12:17 PM] Ummi Tandama: ♦♦♦ *SANGARTATTCE*♦♦♦

Maman Abd Shakur

2 - 3
Free page

Zaure tawuce tana bin almajiran wajen da kallo kafin ta fita kofar gida tai wajen Baba da tunda tafito ita yake kallo, tsugunnawa tai agabanshi tawani kwaye fuska kaman zatai kuka ahankali tace "Baba natafi makaranta amma ni banci komiba ba'a gama abincin ranaba" girgiza kai kawai Malam yayi sanin halin yar tashi, hakan yasa ya saka hannu cikin aljihun babbar rigar dake jikinshi yaciro dari yabata da sauri ta karba tana murmushi tace "nagode Babana, Allah biyaka natafi" "ya cikin?" ya tambayeta anatse, tashi tayi tana kokarin saka kudin ajaka sanan tace "yadena Baba tundazu, natafi" "adawo lpy" tajuya ta fita tana waige waigen zauren, fitowa tayi tafara tafiya a layinsu daya yawaitu da bishiyoyin dogon yaro, dadan sauri take tafiya sabida takai bakin titi tahau boss dazai kaita school, wani gida dan madaidaici dake nan cikin layinsu ta shiga harda dan gudan ta dan sauri take wata matace yar dattijuwa haka, tana zaune tana tuyan waina anan tsakar gidan ahankali kaman wacce kwai ya fashewa aciki ta karasa kusa da matar wacce batama lura da itaba saidai kawai taji mutum akanta, fashewa tayi da kuka kaman wacce aka doka hakan yasa matar ta rike baki tace "mekuma aka miki iya shagwaba iya sonjiki Bilkisu" kara fashewa tai da kuka tana buga kafa akasa cikin kukan tace "tun safe banda lpy kokizo ki dubani kinata wainar saidawa abinki ko Baaba" arude matar tace "ni? Haba tagidana ai kema kinsan inda nasan bakida lpy tuni xan ijiye wainar nan nazo, dena kukan keko, halan cikin ne yatashi?" gyada kai tayi tana share hawayen Baaba tace "shiga daki ki dauko kular ki nasaka miki wainar ki kitafi kinga yau kinyi latti" da sauri tashiga dakin Baaba tana kokarin daukar kulan tace "Baaba ina Muji?" daga tachan waje Baaba tace "yafita da Keke napep waiko zai sami fasinja, saiyau ya daukota daga gareji" daidai nan tafito tamika ma Baaba kular, karba tayi tazuba mata wainar dayawa sanan ta baza mata kuli dayawa akai ta rufe kulan tabata tareda ciro hamsin tace "gashi adawo lpy" karba kulan tayi tace "kibar kudin Baba yabani, natafi Baaba saina dawo" "adawo lpy yar albarka banda wasa a aji kinji yar gidana" fita tayi tana murmushi tana mugun son Baaba, yayar mamanta ne haka suke kiranta, bayan tai aure data haifi Mujittapa (Mustapha) danta na farko shine Maman su lokacin kafin tai aure tazo tayata raino aiko malam yana ganin Maman su ya like mata ya nace yanaso, bayan wani dan lokaci fa suka tafi kauyen su dake chan hanyar gombe kauyen bojude lokacin tun kafin iyayensu su rasu akai bikin aka kawota gidan malam, Umma bata da matsala hakan yasa malam ya hade kansu suna zaman lpy, yayan malam 8, Umma yaranta 5 duka maza wanda duk malam yatura su nijar wajen wani babban abokin shi malami yin karatun addini awani babbar makarantar shi, yanzu ma watan su daya da tafiya kenan sai bayan shekara biyar zasu dawo dan makarantar har certificate ake badawa inka gama, sai kuma maman su data haifi su uku Balkisu, Raiyana da Layla, dukan su malam yasasu a government girls secondary school ne Raiyana da Layla na safe suke zuwa, itakuma dayake SS ne rana ne nata.

Karasowa bakin titi tayi ta tsaya tana jiran Bus wata makauniya tagani ita da yarta suna ta bara a shagunonin kan hanya wai tun safe basuci abinci ba, ba karamin tausayi suka bataba, tana kallonsu suka koma kan dakali suka zauna yarinyar nata kuka, jakarta ta laluba taciro naira

darin da Baba yabata ta karasa kan dakalin datagа sun zauna, yarinyar nata kuka  wai yunwa takeji maman na lallashin ta, ahankali ta duka darin ta mikama yarinyar tareda mata murmushi tace "dena kuka gashi" karba yarinyar tayi tana fadama maman ta bakaramin dadi matar tajiba tace "mungode yar nan, ubangiji Allah ya miki albarka ya raya miki yaranki" dariya Bilkisu tayi sosai tace "Ameen amma nibanyi aure ba mama" washe baki makauniyar tayi tace "to ubangiji Allah ya baki miji nagari wanda zai saki farin ciki sama da wanan dakika samu" ahankali tace "Ameen nagode" ta dagama karamar yarinyar hannu sanan tajuya ta tare bus din dake zuwa ta shiga har lokacin yarinyar nata dagamata hannu itama daga mata hannun tayi har bus yawuce ta daina hangosu.
Allah yasota koda ta shiga school ana gab dafara taran latti, da sauri tafara yin masallaci tai salla sanan tafito tai aji lokacin duk yan aji sun zauna ana ganinta akai tsit kowa nata kallonta hakan yasa tasha jinin jikinta, kujeran layi nabiyu ta wuce ta tsaya agaban sit din ganin duk su Aisha Shehu sun cike Walawa ta zauna awurinta, daure fuska tayi ta kalli Walawa tace "wlh kitashin min daga wuri ai chan ne sit dinki" tanuna kujeran bayan nasu, hararan ta Walawa tayi ta cigaba da zanen flower datake yi a paper, su Aisha Shehu dai sai dariya suke kasa kasa dan dama dagangan Walawa tazauna neman tsokana ne, ganin ko kulata Walawa batayi ba yasa taji abin ya mugun bata mata rai hakan yasa ta fizge byron hanun Walawa afadace tace "badake nake magana ba, kinga kitashi" kaman jira Walawa takeyi ta mike tsaye fuska a daure ta kalli su Fateema da Fa'za dake kusa da ita suma duk suna dariya kasa kasa tace "ku matsamin na fitan ma almasifatu daga wuri" gyaggyara kafa sukayi Walawa tafara tafiya hakan yasa Bilkisu tazo daidai bakin sit din tana jiran Walawa tafito itakuma ta shiga fuskar nan nata adaure fitowa Walawa tayi, saida tazo gab da Bilkisu tasa hannu ta taba mata nono, atsorace Bilkisu ta tsugunna a wurin tareda fasa ihu "wayyo Allah" ta kankame jikinta, aiko duka ajin sukahau ihu da dariya, su Aisha Shehu dasu Fa'iza harda buga benci suna dariya, Walawa ko hanyar kofa tayi ta tsugunna tana dariya harda rike ciki, gabaki daya ajin dariya ake Aisha Shehu tace "babu wacce ba'a tabama nono a ajinan ba, kece kullum kiki yarda yar malam, yaudai an taba dama gasu manya manya" aikuwa kowa dariya suna bubbuga benci irin abun yay musu mugun sugar dinan, saida ta goge hawayen datake yi sanan ta mike tazo gaban Aisha Shehu tace "eh aini kinsan ba yar iska bace irinku ba masu wasan taba nono a school" tana fadin haka tai hanyar kofa wurin Walawa, Aisha Shehu tabita da harara tace "to uban waye yan iskan, ba wasa bane kowa ajin nan an taba nashi saike, koba hakabane?" ta tambayi su Fa'iza da Fateema suma duk dariyan suke harda kama ciki danba karamin dadi abun yamusu ba yau yanda aka kama na Bilkisu yar malam yau, dan ita kadaice bata yarda amata wanan iskancin a aji gashi yau an shammaceta anyi kowa dadi yakeji. Kan Walawa Bilkisu tayi wacce tun kafin tazo kanta tahade hannu tana dariya tace "haba Billy yar malam, yakuri mana kawas ai bankama ba tabawa kawai nayifa dan nasan bakiso wlh bazan karaba, yakuri" kamota Bilkisu tayi ta durma mata duddu abaya daidai lokacin wata malamar english dinsu ta shigo aji hakan yasa duk suka koma wajen zamansu kowa ya natsu.
(oya name abunda kukayi zamanin secondary school?? Barinma wayanda sukayi girls school kadai😂)

Wuraren 4 suka fito break da salla, bayan sunyi salla duk tare suka tayata cin wainar dan dama sune kawayen nata Aisha Shehu Walawa da Fa'ixa saikuma Fateema, bayan sungama

ciyeciyen su sanan suka koma class, sai wuraren biyar da rabi aka tashe su duk suka fito suna tafiya har suka gangaro bakin titi suka shiga bus kowacce tai gidansu.
Gidan Umma tafara biyawa ta ijiye kulan sanan tafito akofar gidansu tahadu da Isyaka yana alwalan sallan magriba, murmushi tamai hakan shima yamata murmushi da sauri ta shiga gida ta gaida Baba sanan tawuce cikin gida. Babu kowa a tsakar gidan duk sun shiga daki hakan yasa taja ruwa tazuba a buta tai bayin su bayan tafito ta tsugunna a makwarara tai alwala sanan ta shigo dakinsu, salla taga Mama dasu Raiyana nayi hakan yasa ta zauna akan kujera tana kokarin kunna fitila, kunnawa tayi ta ijiye daidai lokacin sun sallame Layla ce tafara tasowa Raiyana tabiyo ta abaya duk suka zauna kusa da ita Layla tace "me kika kawo mana daga school Anty Baby?" murmushi tayi ta bude jakarta gwaiba taciro da topi ta basu duk suka karba cikeda jin dadi Mama ta ballamata harara tace "aikin kenan" dariya tayi ta tashi tasaka hijabi tai sallan magriba tana idarwa ta daura kanta akan cinyar Mama ahankali tace "yunwa nakeji Mama sosai" mika hannu Mama tayi ta dauko kular tuwo dake gefenta tace "gashi nan zuba muku kuci keda kaninki to" tashi tayi ta dauko faranti ta zuba tuwon tasa miya asama ta kalli su Raiyana tace "ku sakko muci" sakkowa sukayi zasu sa hannu Mama ta harareta tace "bazaki je kicire kayan makaranta bawai" kaman zatai kuka ta tashi tawuce uwar daka tacire kayan ta fito daure da zani akirji ta zauna tana turo baki sanan suka saka hannu duka suka faraci.

Dr ne akan wani magidancin da akalla zaikai 75 years sa'an Baba buhari😂 acikin wani katafaran falo sai sumbatu yake yana "Dr Ayaan dina zaka kawomin, Ayaan" shiru yayi sabida alluran da likitan yamai daidai lokacin wani security dake sanye cikin uniform ya tsaya agaban falon yana sallama, izini matar dake falon cikin shiga ta alfarma tamai, hakan yasa ya shigo hanunshi rike da wata ipad, Karasowa yayi gefen Baba Sule wanda shine kanin magidancin dabaida Ipy, cike da girmamawa yace "Alhaji wanan shine CCTV footage din natun ranan da Ayaan yafara rashin Ipy abangaren shi, da lokacin daya fita daga gidan" ya kalli matar datai tagumi tana kallon fuskar mara Ipy yace "Hajiya akwai bukatar kema kizo ki kalla dan wata da kayan yan aikin gidan nan ne tafara kawomai abinci lokacin yana garden tace kece kika aikota takawo mai, to ayanda dai CCTV footage din yanuna yanacin abincin yafara rashin lafiya saikuma..." yadanyi shiru cikeda damuwa yace "zodai ki kalla dakanki wata kila ki gane yarinyar dan munemo ta dole zatasan wani abu kan batar shi" tashi matar da aka kira da Hajiya tayi ta dawo gefen Baba sulen ta zauna jiki asanyaye tana kallo, tunda tafara kallo ta dafe zuciyar ta tana buga salati saikuma tafashe da kuka sosai ta kalli Baba Sule tace "Baba Sule ina dana yayi? Yanzu adai yanda yafitar nan a ina zamu ganshi, innalillahi wa innalillahi raji'un wanan wace irin musib.." shiru tayi ganin mara lafiyan yakara farkawa yarike hanun Dr dake kanshi yace "ina Ayaan dina? Eh Ina ka kaimin shi?".
[7/15, 12:17 PM] Ummi Tandama: ♦♦♦ *SANGARTATTCE* ♦♦♦

Maman Abd Shakur

5...
Free page

Iska da kiraye kirayen sallan magrib ne yashiga kunnenta yana ratsa har brain dinta, ahankali take bude ido ganin inda take yasa ta mike tsaye a firgice tana karanto ayatul kursiyu ko ina na jikinta na rawa, karan buga abu dataji shiya kara firgita ta hakan yasa mahaukacin kara juyowa ya kalleta, baya tafara komawa jikinshi ko ina rawa yake, juyar dakai mahaukacin yayi yacigaba da bubbuga kular nata abango yana dariya kafin yakamo bakin rigar shi ya cusa abaki yana ci, hannu tasa tarufe bakinta tacigaba da komawa baya sadaf sadaf, haushin kare taji abayan ta yasa ta buga wani irin mugun ihu ta shiga cikin gidan da gudun bala'i dan ta tsani kare, karan yazo ya tsaya ta bakin kofan yanata haushi, zuciyar ta kiris ne yarage bai fitoba, mahaukacin ya dena buga kular dayake yajuyo dakai yana kallonta, yanda ta makale jikin bango tana kuka kaman zata suma, rigar shi yakara turawa abaki yana kallonta yana wani irin lankwasar dakai yana taune rigar hakan yasa ta tsugunna awurin tareda runtse ido da karfi tana cigaba da karanta ayatul kursiyu, wani irin mugun kuka da haushi karen yasake yi "wu wu!" hakan yasa mahaukacin ya juyo daga dena buga kulan abango ya kalli karen, zare rigar yayi daga bakinshi ya fashe da dariya sanan ya tsugunna shima yace "wu wu" da karfi sosai, haka yadinga wu wu yana matasawa kusa da karen yana tsalle har karen yabar wajen, shirun dataji yasa ta dago kanta ta kalli hanyar fita taga ba karen littafin ta dake watse akasa taga mahaukacin ya dauka yanata yayyagawa yana kara da wasu gwalangwalan yanaci, jikinta har rawa yake tana kallonshi ganin hankalin shi nakan litttafin yasa ta ruga aguje tafita daga wajen, haka ta dinga gudu harsai da takai bakin titi, machine ta tsayar tahau sai goge hawayen dasuka ki tsayamata take tayi, saida suka kai anguwar su daidai kusa da gidansu ta sauka malam tagani tsaye yanata kallonta da alamu dama ita yake jira, kallon mai machine din tayi tace "bari na amsoma kudin" ahankali ta karasa wurin Baba tana share hawaye anatse yace "meya faru? Ya akayi kikai datti haka daga ina kike?" fashewa tai da kuka tace "faduwa nayi Baba akan karfe kaina zafi yake yi ma" hannu yatura a aljihu yace "sannu kidinga yi ahankali nawa zaki bashi?" "naira dari" tafada batare data daina kukan ba, mika mata yayi taje tabashi sanan tadawo ta shige gida hada Ido sukayi da Isyaka dake biyama wasu almajirai karatu ya mata alamu da hannu na sannu ta gyada mai kai asabari ta daga tareda bude kofa ta shiga cikin gida. Babu kowa a tsakar gidan hakan yasa tawuce dakinsu su Raiyana tagani tareda Mama suna bata haddan dazasu bama Baba gobe da asuba yaji, zama tayi akan kujera tana share hawaye Mama ta kafeta da ido tace "daga ina kike Bilkisu? Kin kaima Balaraba kudin nata?" wani irin racing heart dinta ya shiga yi hakan yasa takara fashewa da wani sabon kukan tace "Mama wlh faduwa nayi namaji ciwo akai?" kallo Mama tabita dashi gashi tayi wani irin mugun datti hakan yasa tace "a ina kika fadi? Ina jakan ki? Ina kudin dana aikeki dashi?" tashi tayi a tsorace tai hanyar kofa hakan yasa Mama ta bita da kallo, a tsorace cikin kuka tace "kudin nacikin jakata nabarta a inda nafadi amma gobe da safe zancema Muji yakaini na dauko saimukai mata" hawaye takara sharewa tana kallonta tace "kiyakuri dan Allah Mama" da sauri ta juya tafita daga dakin danba karamin aikin Mama ba ta maketa dan akwaita da saurin hannu, dakin Umma ta shiga aiko duk hankalin Umma yatashi anan ta kwana.

Wuraren takwas da rabi ta shigo dakin nasu lokacin su Layla harsun dade da tafiya makaranta, Mama tasamu tana linke kaya afalo adan tsorace ta wuce uwar daka doguwar riga ta dauko daga ghanamasgon ta na atampa kore sanan ta ciro milk hijabi daya kaimata har kusan kasa ta saka tafito tasami Mama a inda ta barta ahankali tace "Mama zanje gidan Baaba daga nan sai

Muji ya kaini na dauko jakan na kai kudin" batare data kalleta ba tace "saikin dawo" fita tai daga dakin koda tafita waje gidan Baaba tacema Baba zata hakan yasa baihanataba. Samun Baaba tayi agaban murhu tana dafa dafadukan shinkafa da wake "Baba ina kwana, naga keken Muji a waje ina yake?" kallon fuskar ta Baaba tayi tace "ya zaga bayan gida yanzu zaifito, maiya sami idanunki sukai jajir haka" zama tai gefen Baaba ta goge hawayen dataji ya gangaro mata tace "faduwa nayi nabar jakata wurin kuma akwai kudin Mama aciki datace nakaima Balaraba dillaliya" cikeda damuwa Baaba ta kada kai tace "to Allah dai yasa kisami kudin ajakan yanda duniya tabaci yanzu, kai Muji ina kake ne fito ka kaita kafin rana tayi kowa ya fito ayi gaba da jakar, a ina kika fadin?" ahankali tawani narke ma Baaba tace "ahanyar makaran tarmu jiya da yamma" daidai nan Muji yafito daga bayi tareda ijiye butar hanunshi nan gaban rijiya Baaba tace "oya zoka kaita ta dauko jakarta" ta kalli Bilkisun tace "kin Karya?" girgiza mata kai tayi Baaba tace "karya to saiku tafi" girgiza kai tayi arude tace "a'a nidai samin akula naci acikin keke napep" tashi Baaba tayi ta dauko wani kula adaki ta fito ta bude tukunyar ta deban mata shinkafa da waken dayawa ta rufe tabata tace "ki tabbata kincifa kinsan cikin ki baison yunwa" ta kwalama Muji daya shiga daki abinshi kira "wai mekake yi aciki ne?" fitowa yayi rike da key ya kalleta yace "muje" tashi tsaye tayi rike da kular ta suka fita waje keken suka shiga ya tada yace "a ina ne kika yarda jakan?" tagumi tayi gabanta na faduwa tace "chan ta wuraren school dinmu, tafiya suka dingayi har sukakai wurin suka shiga layin har zuwa karshen layin adaidai ta bakin bolan tasa yay parking duk suka fito, komawa bayan Muji tayi ta labe hakan yasa ya juyo ya kalleta yana nazarin fuskarta yace "me wai? Ina jakar to? Uban meme kikazo yi anan wajen bola wakika gani anan?" nuna mishi ginin tayi tace "yana cikin nan jakar kuma wani mahaukaci ne aciki, ni tsoro nakeji ka shiga ka daukomin" tafashe da kuka, tsaki Muji yayi yajuya yana kallon ginin yay hanyar shiga tana biye dashi abaya ko ina na jikinta narawa, tsayawa Muji yay abakin kofa yana kallon mahaukacin dake sanye dawani bakin riga t-shirt daduk ta barbarke dakuma dogon wandon jeans dashima dukya barbarke, sai yago fallen littafin ta yake yana turawa abaki yanaci, jin Muji ya tsaya yasa tadan leko ta bayan shi dan taga meyake kallo, sosai taga mahaukacin yanata tura paper abaki yana taunawa daga gani kasan yunwa yakeji wani irin mugun tausayin shine taji ya shigeta saisa ashe jiya yaje ya sato buredi, da sauri ta juya takoma keken ta dauko kulan abincin da Baaba ta bata dabata tababa tadawo tabi ta gefen Muji ta shiga ciki jikinta na rawa, nesa dashi ta tsaya ta bude kulan abincin tana bashi amma ko kallonta baiyiba saima tauna takardan dayake yi abinshi, kara matsowa tayi ta mikamai har lokacin bai kalleta ba, tunawa datayi jiya yanata buga kula a bango yasa ta buga marfin kulan a bango yay kara sosai, da sauri taga yadaga kai yana kallonta wani irin faduwa gabanta yayi dum! Amma duddu haka saida ta mikamai abinci tanadan kwanto da kulan sabida ya hango abinda ke ciki, baiyi ko motsi ba saima kallonta dayake tayi yana sosa kunne, ahankali tadan tsugunna taga yabita da kallo takara nunamai kulan amma baikarba ba kaman ma baigane metake cewaba hakan yasa ta daga hannunta na dama ta nunamai sanan tasaka hannun a kulan ta debo abincin ta nunamai sanan ta kai bakinta tasaka aciki tana taunawa tanamai murmushi atsorace, da sauri taga yataso yayo kanta da gudu ta matsa baya ta jingineni da bango kaman zata shige zuwa yay gabanta ya fizge kulan da karfi harsaida abincin yadan zube ya zauna nan gabanta ya daga hanunshi shima sama ya nunamata kaman yanda tayi sanan yasaka akullan ya debo yakai bakinshi yafaraci da sauri da sauri murmushi taga yayi daya bayyana dimples dinshi daduk jikakken paper ya makale akai yacigaba daci kaman zai hada da

kulan sai kallonshi take a tsorace jikinshi fatar jikinshi duk baki baki kaman mai aiki a gareji. Shigowa Muji yayi yazo kusa da inda take a makale a bango ya tsaya tareda rike kwankwaso yana kallon mahaukacin hakan yasa mahaukacin ya ijiye abincin yayo kan Muji yana daga hannu zai dakeshi da sauri Muji yakoma baya yana kakkare fuskarshi da hannu, dariya mahaukacin yayi sosai sanan yay wani irin tsalle ya dira agaban kulan yacigaba dacin abincin, da sauri ta mike tsaye kudin Mama dake tsakar wajen ta tsugunna ta dauka tareda tattare littafan ta tasaka ajakar ta kalli Muji daketa kallon Mahaukacin tace "mutafi" hararan ta Muji yayi yace "sannu to kulan Baaba fa" kallon Mahaukacin tayi taga yanda yakecin abincin rabi na zuba ajikinshi "Ke kalli wuyanshi" maganar Muji ne yasa ta janye idonta akan mahaukacin ta kallai ya nuna mata wuyan mahaukacin yace "jibi wanan ba sarka bane a wuyanshi ba, rigar jikinshi tadan rufeshi" yay maganan yana dan matasawa kusa da mahaukacin tareda dan tsugunnawa yana leken wuyanshi dake cikin chain daketa sheki da sauri Muji yace "innalillahi ke Balkisu wlh sarkan zinare ne, zokiga, zomu ciremai naje kasuwa na saida Allah yabamu, munyi kudi" hararan shi tayi tareda jan tsaki bata tanka maiba saima tsugunnawa datayi tana kokarin daukar byron ta dake kasan wurin, Muji ya kalleta kafin ya maida dubanshi ga mahaukacin yace "Allah kadaima yasan meya haukata shin, halama irin yan iskan yaran nanne inbahaka ba meyake yi da sarka yana namiji, yan iska kesa sarka fa irin mawaka da yan party dinan" cikeda masifa tace "nidai baruwana na, baruwan ka da sarkan shi kasan ko garin hauka yasamo, kokuma ya fizgema wasu" hararan ta shima yayi yace "tunda baki da hankali ba, ta ina mahaukaci zai iya saka sarka da kanshi? Eh fadamin ta ina zai iya saka sarka harma ya boye ta tacikin riga, nidai cirewa zanyi? Dan nasan karshen ta wasu su kwacemai" "sata fa kenan Ya Muji ittakulla" karan yarda kulan da mahaukacin yayi yasa Muji yatashi da sauri yakoma baya itakuma tai hanyar waje tafice da gudu, tashi tsaye mahaukacin yayi yafara tsalle tsalle yana gudu yana zagaye wajen da sauri Muji yadau kulan yafita yana waigen mahaukacin.

*wai meke faruwane a novel dinga?*
*waye wanga mahaukaci?*
*waye mutumin nan da Dr ke kanshi*
*waye sangartattcen?*

Wanan shine last free page, idan har kanason cigaba da karanta wanan labarin dake kunshe da abubuwa da dama mai nishadantar da kayatar da zuciya zaku iya tuntubana ta watsapp number na kaman haka 07012181461.
Hanyoyin biya biyu ne kota kati wanda zaki tura MTN 200 ta number nan 07032934950 kokuma ta banki 3107021073 first bank aisha Muhammad.

Labarin ga kuwa yanxu bama komi akeyiba kudai kubiyoni kucigaba da karatu❤
[7/15, 12:17 PM] Ummi Tandama: ♦♦♦ *SANGARTATTCE*♦♦♦

Maman Abd Shakur

4...

Free page
Alluran bacci Dr yasake mai sanan yay bacci, matar takara fashewa da kuka, Baba Sule da Security suka fita daga dakin dan zuwa police station danjin ya ake ciki.

Layla ne ta shigo dakin ta kalli Bilkisu dake kwafe note tace "Anty Isyaka na falon Baba yana jiranki" satan kallon Mama dake tsefema Raiyana dogon gashin ta tayi taga ko kallonta batayi hakan yasa taidan murmushi tadau dogon hijabin ta tafita daga dakin, dakin Baba tai sallama ta shiga, daki ne mai fadi wanda kusan littatafan addinine suka cikashi, koina agyare ga kamshin turaren wuta, daga gefe kuma isyaka ne dayaci gayu cikin normal shadda abinshi sai kamshin turaren duri yake yanata kallonta akunyace ta zauna nesa dashi akan tabarman tana wasa da hijabi tace "ina yini" kara gyra zama yayi tareda lankwashe kafa ya hade tafukan hanunshi yana murzawa yana murmushi yace "barka da zuwa Bilkisu gimbiyata, gimbiyan duka matayen garin nan, gimbiyar dake mulka zuciya ta, saurayinyar mata mai gadon zinare" dariya tayi ta kawad dakai dan ba karamin kunyan shi takeji ba, Isyaka amintaccen almajirin Baba ne, tun yana karamin yaro aka kawoshi almajiran ci wajen Baba harya girma, shekaran shi 25 yanzu, yanada aikin hannu dan ya iya aikin hula da aikin su shadda, Baba yariga yabashi Bilkisu tun tana yar yarinya, yanzu haka ita yake jira dazaran ta zana jarabawa za'ayi auren su yakoma da ita kauyensu nachan hanyar sokoto.
Dan gyara murya yayi yace "bakice komiba mar'autul saliha? Ya karfin jiki" anatse tace "Alhamdulillah na warke ai tun dazu" wata torchlight phone yaciro daga aljihun rigar shi yazo gabanta ya ijiye mata akan hijabi yace "gashinan ki rike inaso mudinga waya tanan" da sauri ta kallai sai kuma ta make kafada ta kwaye fuska kaman zatai kuka, ashagwabe tace "a'a nidai bazan karba ba, Baba bayason muna amfani dawaya Allah kabarshi nagode" tunda take maganan yakafe ta da ita hakan yasa ta dukar da kanta kasa, dan ajiyar zuciya ya sauke kafin ahankali yace "har yanzu kinki dena shagwaban nan ko, dan Allah kidena mini ji nake kaman zan mutu idan kinayi, ina kaunar ki dayawa Bilkisu, yanzu dai Baba yariga yaga wayar ai yama yarda nabaki saisa nakawo miki, gwara munayi munadan taba waya ko? Muma muyi soyayyar yan gayu" gyada mai kai tayi tana murmushi daya bayyana fararen hakoran ta tace "nagode" dariya shima yayi cike da murna yace "bari namiki waka" dan zaro ido tayi tana kallonshi yamata wani irin kallo yace "dukda ina malami ai dole na koyo waka nama gimbiyata dan na faranta mata rai" dariya ta sake yi harda rufe fuska, dan gyara murya yayi hakan yasa ta tsayar da dariyar tana kallonshi, yawani kalleta yana nuna ta da hannu yace "Bilkisu na yarda dake, dauki amanata ki rike, kin dace da zama dani, Bilkisu gimbiyar raina, Bilkisu hasken idaniyata, Bilkisu ina kaunarki, Balkisu taurarawan raina, Bilkisu abun kaunataaa" bakaramin dadi wakan yayi mata ba sosai ta dinga dariya tareda boye fuskar ta cikin hijabi, "ya isa haka dariyan to yawan dariya baida kyau a addinin mu, tashi kije ki kwanta akwai school gobe" addu'a yayi sanan ya mike tsaye yace "saikuma gobe ko, kiyi alawa kafin ki kwanta zan kiraki tawaya cikin dare sabida kitashi kiyi salla ko" gyadamai kai tayi yafita daga dakin yana mata murmushi, hakan yasa itama ta tashi sanin Baba nadakin Umma yasa takoma dakinsu ganin Mama tai bacci da Layla aka gado, yasa ita tadawo falo ta kwanta kan dagon kujera 3 sitter wacce dama anan take kwana itakuma Raiyana 2 sitter take kwana kokuma wani zubin su kwana akasa.

Da asuba bayan sunyi salla duk dakin Baba sukaje karatu ya koya musu Qur'ani, hadisi da

fiqhu, bayan sun biya wanda yabasu jiya harsai wajajen karfe shida sanan suka fito, kitchen ta shiga dan hura wuta Raiyana kuma taja ruwa dan wanke bayi da makwarara, itakuma Layla tadau tsintsiya sharan tsakar gida, suna gamawa duk suka diba ruwan zafi sukaje wanka sukaci dumamen su da kokon da Bilkisu ta dama sanan suka tafi makaranta. Gyara dakin Mama tayi fess ta kunna turaren wuta sanan tawuce dakin Baba ma ta gyara tana gamawa yafito daga dakin Umman hakan yasa tawuce nan ma ta gareshi Umma sai shimata albarka take, dakinsu ta dawo tadau hijabi tasa ta kalli Mama dake shan koko tace "indanje gidan Baaba Mama?" dari biyar din kan kujera Mama ta dauka ta mikamata tace "gashi nanma daganan kibata kice nace kudin zubi na nayau" da sauri tafita saida takara gaida Baba da wasu alamajiran data gani taredashi sanan ta wuce ta tafi, akofar gidan ta hango Muji yana kokarin tada keke da sauri ta karasa wajen ta daure fuska tace "biyani dari biyuna yaya Muji" saurayin wanda da kadan yafita tsawo da jiki ya dago kai tareda daure fuska har zaiyi magana saiya ga wayar hanunta da sauri yasa hannu yakar ba yana jujjuyawa yace "iyye waya saimiki waya dan aramin?" make kafada tayu tace "bindi salon kaje kabata min, jiya jiyan nan fa Ishak dina yabani" tsaki yayi yace "yarinya anjima nan nima zan dawo da tawa sabuwar wayar yau xan bada karamar tawa na siyo mai camera ma, soft touch, tunda hakane bazan baki daniba, kuma bazakimin hoto dawayar ba" tabe baki tayi tace "kai Yaya Muji Karya kasa, a ina kasami kudin siyar irin wayar nan daka kira wurin dubu ashirin fa ake sayar da irin wayoyin nan?" dariya yayi yace "kinga tafiya ta nidai, kuma bazan biya daribiyun ba" yana fadin haka yaja keken shi yay gaba, fashewa tai da kuka ta shiga gidan tafada jikin Baaba daduk ta rude tana tambayan ta lpy cikin kuka tace "ba yaya Muji bane yaki biyana kudina ba" share mata hawayen Baaba tayi tace "bari yadawo saiya baki dan gidansu, tashi kitayani wanan wankin dama dukna kosa kizo" karban wankin kayan tayi tama Baaba tsaf tana gamawa Baaba ta zubo mata shinkafa da miya zama tayi ta cinye harda kari kai Bilkisu badai ciba wolla.

Wuraren shadaya da rabi tabaro gidan ta dawo gida wanka tasake yi sanan tafara shirye shiryen school Mama tamika mata dubu biyu tace "idan zaki dawo daga makaranta ki sauka a tudun wada ki kaima balaraba dillaliya kudin samiran ta dana siya, ki tabbatar ita kika bama kudin ba yayanta ba, karki manta fa kinga ta dameni nakawo mata saiyau babanku yaban kudin" karban kudin tayi ta cusa chan kasan jaka tace "bazan manta ba Mama" sanan tafita daga dakin tareda mata sallama tana karban kudin mota, wurin Baba ta tafi bayan tabiya gidan Baaba ta karbi wainarta a kula.

Tana shiga aji tasami su Walawa na wasan nonon su as usual, tsaki tayi takoma ta zauna hakan yasa suka dinga ihu Fa'iza tace "yar malam haba mana ki bari muji naki manyan nan" ko kallonta batayi ba saima bude jakarta datake yi tana kokarin ciro littafin biology dan sake karanta wa danyau sunada test, Aisha Shehu tabude jakarta cingum taciro guda shida ta mika mata tace "kinji share Fa'iza Billy, ga cingum din bikin Fateema" dan zaro ido tayi ta kalli Fateema daketa sussune kai tace "dama aure zakiyi koki fadan mana" Walawa tace "toke kin fadan mana nakine da Ishak dinki?" raurau da ido tayi tace "to ai ni sai mun zana waec tukunna za' ayifa ba yanzu bane kuma ainafada muku" hanunta Aisha Shehu ta chapke ta sakamata cingum din aciki tana kallon tafin hanun nata yanda yay zufa sosai sabida taushi tace "kedai kin more Billy jikinki taushi kaman na jaririya wai wani mai kike shafawa ne, jibidai fatar hanunki taushi kaman auduga" yatsine fuska Bilkisu tayi tareda zuba cingum din cikin jaka tace "yaushe

ne bikin" "ran Saturday, amma fa 4 cingum ne naki, biyu na Raiyana biyu na Layla muna gayyatar su" murmushi tayi tace "aiko zamuzo in sha Allah" zasuyi maganan wani malamin dake musu physics ya shigo hakan yasa duk sukai shiru suna sauraron karatun, koda aka tashi break goruba tasaima su Raiyana guda hudu da topi duk ta zuba ajaka, sanan tawuce wajen su Walawa tare sukaci wainar nata sanan suka koma aji. Wuraren biyar da rabi aka tashe su, tareda su Walawa suka jero suna dandarawa zuwa bakin junction inda zasu sami mota, daidai wajen wani mai shayi sukaga wani mahaukaci yazo da gudu yadau biredin kan table ya gudu gefe kan wani dakali ya bude yawani yago kato yakai baki yanaci yana sosai kai, dariya su Aisha Shehu sukayi sukace "Allah sarki yunwa mahaukacin yakeji, amma nasan idan mai shagon nan yafito yakama shi wlh bazaiji dadadi ba, innine shi yanda Allah ya ciyar dashi dinan yagudu kawai" gani sukayi ya yayyago biredin ya tura baki rabi yazube akasa sanan yakara tashi ya koma shagon da gudu ya kara dauko biredi har biyu yana yayyaga ledan jikinsu yana kokarin yago buredin daidai lokacin mai shagon yafito daga cikin dakin shagon yana ganin mahaukacin yafito daga shagon tareda daukan katon iche daya riga yakama da wuta yayo kan mahaukacin daya zauna akan dakalin yanata cin biredi zai kwalamai da gudu Bilkisu tai wurin hakan yasa Fa'iza tace "ke Bilkisu maizakije kiyi a wurin Allah sa mai shagon yahada dake, mudai mu wuce mutafi ba ruwan mu" juyawa duk sukayi sukai tafiyan su suna maganganu, fizgo mahaukacin mai shayin yayi azuciye ya chakumo rigarshi yana jijjigashi yace "dan uwarka kasan buredin nawa kaci yanzu nan dari shida fa, kowani daya naira dari biyu ake saidawa, dan kaga jiya kazo ka dauka na barka sabida tausayi" shidai mahaukaci ko kallon fuskarshi baiyiba saima cin buredin yake kaman an aikoshi hakan yasa wani zuciya ya dauki mai shayin ya daga itchen zai bugamai Bilkisu da isowarta wurin kenan tace "dan Allah malam ka yakuri karka dakai zan biyaka nawane biredin?" ture mahaukacin mai shayin yayi ya kalleta yace "dari shida" jakarta taciro ta kwaso duka yan kudinta ta kirge su tass harda na motan ta dari uku gareta nakanta ta mikamai kaman zatai kuka tace "dan Allah ka yakuri karbi dari uku ga makarantar muchan karka dakai kaga baida lpy baimasan mekake cewaba gobe idan nazo zan kawo ma ragowar kudin" tana maganan ne tana rataya jakar tata ahannu akan saman hijab, karban kudin mahaukacin yayi yace "wlh kin taimakai dayau wlh namai lilis hakanan zaijamin asara ba gyara ba dalil..." kasa karasa maganan yayi sabida fisge jakar Bilkisu dayaga mahaukacin yayi ya ruga aguje yay kasan layi arude Bilkisu tace "na shiga uku jakata Malam" tabe baki mai shayin yayi yajuya yace "aisai ki bishi awani gida da ba'a gama ginewa ba naga mahaukacin yake kwana anan kasan layi, kije tun kafin ya salwantar miki da jakan school" shigewa shagon shi yayi yacigaba da aikin gabanshi, sosai jikinta ke rawa tabishi da kallo yanda yake gudu yana tsalle yana wulla jakar nata sama, arude ta dafa kirjinta ta kwalalo ido tace "na banu kudin Mama" da gudu tabishi gashi yay mata nisa, hangoshi tayi ya shiga wani gida da ba'a gama ginewaba, karasawa wajen ginin tayi jikinta na rawa tana kuka arude tana bin ginin da kallo ganin anma maida wajen wurin bola, ahankali ta tsallake bolar da bismillah tadan leka cikin ginin dakai tana goge hawayen dake zuba, hangoshi tayi ya zauna akasa ya zazxage jakan nata ya barbazar da komi naciki yadau cingum yana cusawa abaki batare daya bare bawon ba, ga kudin Mama agefe akasa suma iska sai kadasu yake, kasa shiga ciki tayi jikinta sai kakkarwa yake tana goge fuska, shiko baima lura da itaba cingum dinshi yakeci yadau goruba yanata jujjuyawa yana kallonshi yana kaiwa baki ya yatsine fuska ya jefar, ya dau kulan wainar ta yanata jujuyawa yakasa budewa, jijjigawa yahauyi yana karawa a kunne yanajin karan

dayake yi hakan yasa yafara bubbuga kulan abango yana dariya kaman an aikoshi, babu inda baya rawa ajikinta ita bama ta damu da littafan ba note ne xata iya kwafewa kudin Mama ne kawai takeso hakan yasa takara fashewa da kuka mara sauti tana share fuskar jikinta na bari, gani tayi ya tsaya chak da dena buga kular a bango yadena dariyar haukan dayake yi, lokaci daya kawai taga yajuyo dakai ya kalleta hada ido sukayi, wani irin faduwa gabanta yayi dasuka hada idon gashi yaki dena kallonta, ahankali tafara komawa baya tana daddafa bango jikinta na rawa, turgude kafa tayi, tai mugun faduwa kanta ya bugu da karfe dake kan bolan hakan yasa ta buga ihu daganan bata sake sanin inda kanta yakeba.
[7/15, 12:17 PM] Ummi Tandama: ♦♦ *SANGARTATTCE*♦♦

Maman Abd Shakur

6 & 7

Keken suka shiga yatada sukabar wajen saida yadanyi nisa da tafiya sanan yace "tayaya jakanki yazo nan Bilkisu?" maida kanta kan titi tayi tana kallon yanda motoci ke gudu abunsu tace "jiya nefa damuka taso daga school na hango wani mai shago zai dakeshi sabida ya daukomai beredi yaci, wlh ba karamin tausayi yabani ba kana ganinshi kasan yunwa yakeji kato dashifa shine mai shagon dakokaika baiyiba yawani chakumo shi zai daka, wlh inda ace Ipy shi lau ai daga ganin mahaukacin nan bazai dakun maiba, mutane basuda kirki da tausayi, shine nikuma nabashi 300 nace zan cikamai 300 yau danwai bread din 600 yaci, shine shikuma mahaukacin ya fizge jakana ya gudu" shiru tayi kafin ta share hawayen daya dan zubo ta kalli Muji da shima ita yake kallo ta madubin keken tace "wlh ko, da'ace ni wata mai kudi ce dana kaishi asibitin mahaukata da wanan gararin dayake tayi agari ba abinci, aita dukan shi dan sunga shi baya dukan mutane" saikuma tafashe da kuka tana goge fuska da hijabi, wani dogon tsaki Muji yaja yace "wlh bantaba ganin banziya wawiyar mutum irin kiba, aisai ki kaishi tunda kanin ubankine, irin kune kesa kanku a bala'i da sunan taimako, nidai inane gidan balaraban kafin haushin ki yasa na wuce ban bansaniba" nunamai gidan tayi yay parking tafito tabarshi akeken ta shiga ciki, yabita da kallo yana girgiza kai.
Yanada shekara uku aka haifi Bilkisu kusan tare suka taso, Bilkisu akwai tausayi ko minti yaganta dashi lokacin suna yara idan ya tambaye ta hanshi to karyan rashin Ipy zaimata yafashe da kuka, hakan zaisa cike da tausayi tabashi tace yama shanye duka taitamai sannu. Wuraren shadaya da rabi suka koma gida hakan yasa ta shiga wanka tafara shirye shirye shabiyu da rabi nayi tawuce tatafi.
Wuraren biyar da rabi ta shigo gidansu tana yin salla ta dauko wayar da Isyaka ya bata ta kunna "Balkisu" Mama takirata dake uwar daka ajiye wayar tayi ta tashi ta shiga dakin akan gado taga Mama a zaune rike da kofi karasawa wajen tayi tace "gani Mama" kofin ta mikamata tace "Malam ne yamiki wani sabon addu'a sha saiki rage na shafa miki akan ciwon" karba tayi ta sha da bismilla sanan ta mikama Mama kofin, kaman zatai kuka dan batason abinda zai taba ciwon nan nata danko ta tashi wanka bata ma zuwa wajen balle ta wanke, hararan ta Mama tayi tace "dagamin rigarki" ahankali ta daga rigar tana kallon fuskarta ganin yanda ta daure yasa ta natsu,

debo ruwan addu'an Mama tayi takai hannu zata shafa akan ciwon da sauri ta dafe hannun Mama tareda zaro ido atsorace tafashe da kuka tace "Mama wlh kina tabawa zai faramin zafi ne, kinga tun ranan nan baisake min zafi ba yawarke dan Allah kiyakuri" hannun nata Mama ta kabar ta shafa mata ruwan ahankali sanin mugun rakin ta, ihu tayi wanda saida yasa su Layla da Raiyana dake falo suna home work suka shigo dakin da gudu, tsaki Mama tayi bayan tagama shafawa tarufe cup din ta ijiye agefe ta kalli yanda ta zube awajen tana kuka tace "wlh Balkisu kibi asannu fa inba hakaba zan cimiki mutunci dama kinsan taraki nake ko, yarinya sai iskancin banzan dako kanninki basayi zan mugun saba miki, tashi ki fitanmin daga daki" tashi tayi ahankali da taimakon Raiyana suka fita daga dakin tana kuka, yanda ta tsani mutuwa haka ta tsani abinda saisa ataba mata ciwon nan, suna kowama falon ko kallon wayar bata karaba tacigaba da kuka ahaka taci kukanta bacci yay gaba da ita, koda Isyaka yazo saidai Layla taje dakin Baba tacemai tariga da tai bacci.

******************

Banko kofar dakin da akayi bako sallama yasa duka mataye biyun dake bedroom din zaune kan katafaren gadon dakin dago kai, wata matace tashigo tadan mayyanta dan akalla zatai 55, ta kalli daya daga cikin matayen afusace tace "haba Firdausi daga tafiyata biki yau duka duka kwanana biyar bana gidan nan shine zan dawo na tarar da wanan mummunan labari Ayaan ya bata ba'a ganshi ba, sabida nimai kula dashi baninan, ke wace irin uwa cewai? Kin haifi yaro kin kasa janshi jiki, kullum tsakanin ki dashi kyara ce da fada, ba so ba lallami, halama bayan tafiya na fada kikamai shine yabar gidan" tafashe da kuka saikuma ta nunata da yatsa tace "wlh inhar ba'a ganoshi ba wlh saina mugun saba miki nidake zamusa kafar wando dai ne, kuma bari Alaji ya warke za'asan nayine, muguwar mata mai bakin hali kawai" tafashe da kuka tafita ta bugo mata kofa, tagumi wacce aka kira da Firdausi tayi hakan yasa matar dake kusa da ita wacce kawarta ce tazo mata jajen abinda yafaru ne taja tsaki ta kalleta tace "keda danki dakika haifa da cikin ki har wata step mum ta isa tazo tana gayamiki magana haka? , Ita tasan yanda kikeji ne shine kekuma kika mata shiru iya hakuri" wani handky mai kyau dake gefenta ta dauka ta goge kwallar daya zubomata ta ijiye sanan tai murmushi ta dafa kan hanun kawartata tace "Ummu Haneef bahaka bane ai abin dadine wanda ba ita tahaifi yaronka ba hartazo tana fada dakai akan danka, wanan alamune na soyayya yanzu kinga ko bayan raina nasan Hajiya Ashferh nason dana hankalina ya kwanta" tabe baki Ummu Haneef tayi tace "lallai ni bansan irin zuciyar kiba Firdausi, anfa kiraki muguwar uwa da sauran su shine kike wani yabonta haka ai yayi kyau kicigaba" murmushi tamata tace "bahaka bane kokema kinsan halin Ayaan da Hajiya da Alhaji sun mugun bata yaron, ya lalace, sabida ina yawan mai fada da kokarin gyrashi shine suke ganin ina takura mai" handky takara dauka tasake goge wasu hawayen kafin ta kalli hadadden agogon dake bangon dakinta tace "lokacin maganin alhaji yayi bari naje nabashi ina zuwa" tashi tayi tafita daga dakin Ummu Haneef ta bita da kallo cike da tausayin yanda dukta lalace.
Tana dawowa bayi ta shiga ta dauro alwala tafito Ummu Haneef tace "sallan mezakiyi warhaka?" Ahankali tace "addu'a zanyi dukma inda Ayaan yake Allah ya tsaremin shi, ya

bayyanar dashi, ya kulamin dashi, yakuma dawo dashi lpy" tashi itama Ummu Haneef tayi ta daura wayarta akan gado tace "bari nima nayo natayaki".

*********

Wuraren 12 tafita daga gidan Baaba bayan ta karbi wainar ta data saka mata akula, mota tahau zuwa school dinsu sai tunane tunane take har aka kawo ta sauka tafara dandarawa, kallon layin da mahaukacin nan yake tayi taji takasa cigaba da tafiya ta tsaya chak, kulan wainar da Baaba tabata ta kalla saikuma ta kalli layin jitayi takasa wucewa ta tafi makarantar hakan yasa tai layin tana tafiya ahankali danji take kaman wani abu na fizgarta zuwa kaimai abincin nan, ahaka har takai ginin da mahaukacin yake tsayawa tayi chak tanabin bakin kofar wajen da kallo ganin dige digen jini da sauri ta shiga cikin ginin tanabin trace din dige digen jinin, hango shi tayi a tsakar wajen ya zauna yanata hura iska akafar shi dataga yana jini sosai kaman wani abune ya yankeshi, yanata yarfe hannu,  yana cije baki, yana jijjiga kafar da dayan hanunshi alamun abun namai ciwo sosai, dena jijjiga kafar yayi yadebo kasan dake wajen ya kwarara akan ciwon yana huhhurawa da baki dan har miyau yake fita yana yarfe hannu yana runtse ido kaman xaiyi kuka, da sauri ta karaso gabanshi kaman tafashe da kuka dan mantawa ma tai da tsoron datake ji tayi ta tsugunna tana kallon kafar tace "yanama zafi?" dago kai yayi ya kalleta suka hada ido da sauri ta dauke kai jin gabanta yakara faduwa ta kalli kafar yanda kasa kebin jinin dake fita tace "kadena saka kasa to zaikarama zafine" jakarta tabude taciro dan ruwan data zuba a goran fanta dan dashi take alwala a school taciro da sauri tabude saikuka take ta kalleshi gani tayi ita yake kallo hakan yasa ta karanto addu'o'i aranta, kaman yana gane abinda take cewa tace "bari na wanke ma ciwon" tsiyaya ruwan tayi akan ciwon hakan yasa yaja kafar arude danhar yana buge mata hannu, ahankali tace "sannu da zafi?" tai maganan tana share kwallan dataji yazubo mata, kara dan matasawa kusa dashi tai kadan tace "kawo nakara sa wanke ma kasar saina shafama rob inada rob ajaka" ko kallonta baiyiba saima juyamata baya dayayi yanata pipita duka hanunshi akan kafar dakuma hurawa da baki, kana ganinshi kasan yanajin azabane, hawaye takara shareware dasuka kasa tsayawa sabida tausayi da sauri taciro kular wainar da Baaba tabata tunawa dayana son abinci ta bude ta zagayo ta gabanshi ta mikamai tana murmushi aiko ya fizge kulan da sauri yafaraci yana sosa kunne, hakan yasa ta dauko rob ajakan nata da ruwan tadawo ta gaban shi ta tsugunna ta tsiyaya ruwan kan ciwon tsayawa yay dacin wainar yana kallonta atsorace tadan koma baya tace "yakuri" ganin yacigaba dacin wainar yasa ta karasa wankewa tass ta ijiye ragowan ruwan agefe sanan ta lakato rob ta shafama ciwon tai tagumi tana kallonshi dan jira take yagama tadau kulan ta tafi, cinyewa yay tass kafin ya wurgar da kulan yana dariyan mahaukata saikuma yay shiru yanata kallon ruwan data ijiye gefenta kallon gefen nata tayi ganin abinda yake kallo yasa tadau ruwan ta mikamai da sauri ya fizge danhar saida ruwan yakusa zubewa ya kafa abaki yana sha yanagama sha ya wurgar yana dariya saikuma taga ya buga kanshi akasa ya baje awurin yay wani katon hamma kafin ya lumshe ido sai bacci, tagumi takarayi ta bishi da kallon tausayi tana share hawayen dataji yazubo da bayan hannu "to baida iyayene dasuka barshi shi kadai sai wahala yake? Ashe ciwo yaji saisa Allah ya turota ta kula dashi? In sha Allah daga yanzu kullum saina kawoma abinci kaci, Allah yabaka lpy". daukar kulan da goran tayi tarufe ta saka ajaka sanan tabar wajen tana

waigenshi.
[7/15, 12:18 PM] Ummi Tandama: ♦♦ *SANGARTATTCE*♦♦

Maman Abd Shakur

8 - 10

Tafito tawuce school, tun daga gate tahango Sargent na dukan latti. "innalillahi wa innalillahi raji'un" kasa shiga tayi ta tsaya anan gate tana kuka har saida Sargent yagama dukan duka yan lattin sanan ya dago kai suka hada ido tana kuka yace "ke bazaki shigo amiki naki bane ko komawa gida zakiyi?" girgiza kai tayi ta shigo tana hawaye ta mikamai hannunta tana kokkomawa baya tana kuka, Chau! Ya zuba mata daya wani irin ihu tayi tana tsalle wanda yasa harshi Sargent din saida yakoma dabaya yana kallonta "ke Ipyn ki kuwa?" ko kallonshi batayiba saima sosa tafin hanun take dayay jajir tana kuka kaman zata mutu, "kawo hannun saura uku" yafada yana matsowa kusada ita, hijabi tasa tana goge fuska ta makale ajikin bango. "dan Allah ka yakuri karka karamin, dan Allah" kanta yayo hakan yasa takara makalewa ajikin bango tana ihu daidai nan principal dinsu tafito tace "Sargent bar dukan turota ta gyaramin office" tun kafin Sergent dinma yay magana ta tashi da gudu tabi bayan principal tana kuka haka ta gyara office din kafin takolma aji lokacin har angama first period, ranan haka takaraci zamanta a aji tana kuka gashi a ranan ne aka manna musu time table din waec dinsu dazasu fara nan da wata daya.

Wuraren biyar da rabi ta shigo gidan nasu atsakar gida Umma data fito daga kitchen ta tareta tace "maiya sameki idanunki suka kumbura haka?" shiru tayi takasa magana dan ta tsani yin Karya, sai hawaye tafada jikin Umma tana kuka, Umma dukta rude tacirota daga jikinta tace "cikin newai?" girgiza mata kai tayi ahankali tace "dukana Sargent yayi amakaran ta" tai maganan tana nuna mata hannun dayay jajir "wayyo Allah sannu kinji Allah zai saka miki, jekiyi wanka kizo nazuba miki tuwo, Maman ku dasu Raiyana suna gidan Baabar ku" daki ta shiga ta cire kayan makarantar ta dauro zani akirji tafito rike da kayan makarantar ta zuba abotiki, kan window kitchen takoma ta dauko omo ta zazzaga aciki ta jawo ruwa daga rijiya ta wanke kayan fess ta shanya kafin takara dauraye botikin taja ruwan wanka tai bayi, tana tafitowa Umma ta zuba mata tuwo nan tsakar gida ta zauna ta tadashi tass dan miyan kukar harda wake yau akasa aciki, tana gamawa ta wanke hannu takai kwanon kitchen ta shiga daki ta dauko wayarta ta kunna, aiko kiran Isyaka ya shigo dauka tayi yay mata sallama anatse. "Assalamu Alaykum gimbiyar zuciyata, waya tabamin ke amakaranta idanunki sukai ja haka?" kaman zatai kuka ta harari bangon dakin tace "ba Sargent din school dinmu bane ba, yawani dakeni da bulalar inji a hannu" dan lumshe ido Isyaka yayi akan dakalin waje dan duk dalibai sun fita bara sai bayan sallan Isha'i za'a cigaba da karatu, malam ma bayanan, ahankali yace "kece kin dage saikin yi karatun nasara, mezaki yi dashi? Kinada ilimin addinin ki kin sauke yanzu kina kan hadda wacce kin kusa gamawa, kin haddace hadisai da dama kin iya littatafai da dama duk wanan ilimin addinin naki kika dage saikiyi na nasara, mezakiyi dashi, ai dole kisha duka haka kam, mutumin daba muharmin kiba yakama yana dukan ki, danba wanan makarantar ba dayanzu

munyi auren mu natafi dake garin mu anya Bilkisu kina tausayina kuwa?" gyadamai kai tayi tace "kayakuri kaga watan gobe ma zamu fara jarabawan, muna gamawa komi yazo karshe" dan ajiyar zuciya ya sauke yace "shikenan Allah ya bada sa'a, sanan gobe zamuje school din saina koyama Sargent din hankali waye shi dazai tabamin gimbiyar mata, mar'atu saliha" dariya tayi sosai tana auna Isyaka da Sargent hakan yasa yace "mekike ma dariya?" murmushi tasake yi tace "babba nefa Sargent din?" "kina nufin banda karfin dukan shine kome?" zatai magana taji yakatse wayar, wayar tabi da kallo kafin ta fashe da dariya harda rike ciki tace "to daga fadin gaskiya Sargent ai babba ne kaiko bama kakai girman Sergent ba balle nasa rai zaka iya ramamin" kwanciya tayi kafin ta ijiye wayar akan kujera ta lumshe ido haka nan taji tana tunanin mahaukacin nan.
Wuraren 9 ta shigo dakin nasu dan daga dakin Abba take ta tsugunna agaban Mama dake kada lagwani, "Mama inje gidan Baaba?" "saikin dawo" da sauri ta zuri hijabin ta dake kan kofa har kasa tasaka sanan ta wuce uwar daka ta tsugunna karkashin gado ta ciro asusun ta tadawo palo ta zauna kan kujera tana jijjigawa, Mama ta kalleta tace "mezakiyi da asusun?" adan tsorace tace "fasawa zanyi Maman mu?" "kiyi meda kudin?" Mama takara jefa mata wani tambayan kasa amsawa tayi saima wasa da hijabin ta tahauyi, kafin ta dago kanta a tsorace tace "gidan Baaba zankai" dauke kai Mama tayi daga kallonta tacigaba da abinda takeyi hakan yasa ta saci kallon maman nasu kafin tadau asusun tafita daga dakin da saurin ta.
Akofar gidansu Baaba ta tsaya ta fasa asusun dayake na katsa ne, ta tattare kudin ciki ta kirga dubu biyu da dari uku ne sanan ta shiga gidan, Baaba ta gani gaban murhu Baaba tace "yar arziki kinzo" shiga dakin Muji tayi tace "ina zuwa Baaba" samunshi tayi yana shiryawa zai fita hakan yasa tazo kusa da shi tawani yi laushi dan tasan halin shi, ahankali tace "Ya Muji inkanama Allah ka kaini muyi aikin lada" "aikin ladan mene?" ya tambaye ta yana kokarin daukar sabuwar wayarshi daya saya ta gionee, wayar tabi da kallo kafin tace "dan Allah ka kaini muje muba mahaukacin nan abinci sanan in sharemai wurin nan dayake bacci kaji" wani kallo Muji yabita dashi hakan yasa ta tsugunna agabanshi tafashe da kuka, cikin kuka tace "ya Muji karka manta akwai karuwar data shiga aljanna sabida kare, taimako da kyautatawa sune dabi'un dakowani musulmi yakamata yanada shi, bamusan dame Allah zai dubemu yaji kanmuba yasamu a aljanna, kaji dan Allah, kuma karka fadanma Baaba sirrin mune wanan dan Allah ka kaini, nibanaso naje ni kadai ne, tsoro nakeji kaga jiyama ya yanke sosai akafa saisa nafasa asusu na musaimai takalmi ahanya da riga sabida ya chanxa yagargiyar jikinshi" kudin datake nunamai ya kalla mamaki dukya kasheshi ya tabe baki yace "lamarin ki akwai ban mamaki, daga ganin mutum saikace ubanku daya, nidai mutafi karki batamin lokaci" wani dadine ya kasheta ta shiga dakin Baaba, kula ta dauko tazo tukunya ganin baba na bayi ta bude dafadukar taliyar hausa ta gani ta deba sanan tarufe suka fito ta ijiye a keke sanan takoma ciki Muji yace "ina kuma zaki" bata bashi amsaba saidai tafito da jarkan ruwa da tsintsiya dawani ledan daki da Baaba tacire dan tasa sabo, dukta saka akeken Muji yabita da kallo, tai murmushi mai karamata kyau tace "muje" kunna keken yayi suka tafi. Ahanya suka tsaya tasaimai bakin takalmi kito size 43, irin takalmin nan damasu noma kesawa inzasu gona wanda yake arufe sanan tasai babbar t-shirt blue suka taho.
Tun kafin suyi parking ta hango shi abola yanata tsintse tsintse, ahankali tafito daga keken bayan sunyi parkin rike da kulan, mahaukacin na hangota yataho da gudu har saida takoma baya da sauri amma ya bita ya fizge kulan hanunta yana dariya, da sauri ta kalli Muji daya bisu

da kallo tace "kama gani yaganeni wlh" tabe baki Muji yayi yataya ta daukan jarkan ruwan itakuma ta dauko tsintsiya da leda suka shiga gidan. Yana zaune akasa sai kiciniyar bude kulan yake hakan yasa ta budemai ya fizge da sauri zai saka hannu ta rike hanun nashi gabanta na faduwa tace "tsaya in wanke ma hannun da datti" ta kalli Muji hakan yasa ya tabe baki yakaraso wajen yabude jarkan ya daga itakuma takai hannunshi tana wankewa Muji na zuba musu ruwan sanan ya fizge yahau ci, murmushi tayi tana kallon ciwon kafar nashi sanan ta yayyafa ruwa a wajen tasa tsintsiya tafara shara har takai waje ta shinfida carpet din dayadan yayyage, nan da nan wurin yay kyau, yana gama cin taliyar yayar da kulan da sauri ta mikamai ruwan ya karba yasha sosai yay wata irin katuwar gyatsa, takalmin ta dauko tazo ta gabanshi tana kallon kafarshi daduk yay datti, ruwan tasa ta wawwanke mai kafar yanata kallonta kafin ta saka mishi takalmin aiko yamai  daidai, ya mike tsaye yanata tsalle yana kallon takalmin, ta kalli Muji kaman zatai kuka tace "toka sakamai rigar dan Allah" atsorace yace "ni? Ni wlh tsoro nakeji" dariya tai tace "Allah bazai maka komiba baya komi" ta mikamai rigar suka karasa kusada shi tare, ya juyo yana kallonsu duk suka tsaya chak suna kallon juna, daga mai rigar Muji yayi yana juyawa asama hakan yasa yadinga bin rigar da kallo sanan Muji yasa hannu zai ciremai ta jikinshi da sauri ta juya musu baya saida Muji ya ciremai sanan ya samai wacce suka siyo aikuwa tamai daidai, da sauri Muji yace "juyo kigani" murmushi tayi tana dafa Muji tace "laaa ashe na cinka size din daidai" ganin yanda yaketa tsalle yasa muji yace "bari namai hoto" ciro wayarshi yay yadinga daukan shi hoto yanda yaketa tsalle tsalle ya kalli Bilkisun daketa dariya yace "dalla malama mu matsa kusa dashi dukmuyi selfie, selfie da mahaukaci" yay maganan yana dariya yana janta har inda yake ai kuwa mahaukacin na ganinsu ya dena tsallen yana kallonsu duk suka tsaya a gefenshi, Muji ya dau hoton. Tace "zomu tafi to tunda mungama" fita sukayi suka barshi yanata tsalle tsalle.

Yau kwana ta biyu kenan bataje wurin shi ba sabida weekend gashi ba makaran ta, sanan Baaba nama wasu dalibai daya yaye walima aiki suketa yi bata samu daman fita daga gidan ba, haka tai kwanaki biyun nan tunanin shi koya yake oho koma yaci abinci oho duk tabi ta damu sosai.
Yau Monday tun shadaya ta shirya Mama tace "da wuri haka zaki yau Bilkisu?" gyada mata kai tayi tace "eh inaso nai karatu ne sosai Mama jarabawan mu yakusa" kudi Mama tabata sanan tafito ta karbi kudin mota wurin Baba kafin ta wuce gidan Baaba dayawa ta dibi wainar yau tazuba ruwa agora tafito har bakin titi kafin tahau mota dazai kaita sabon gari. Sauka tayi ajunction sanan tafara dandara wa har zuwa layin mahaukacin, babu kowa a wajen wurin hakan yasa ta shiga ginin tana karanto addu'o'i, a kwance ta hangoshi abinda bata taba zuwa ta tarar dashi haka ba kenan, idanunshi sunyi jajir kaman ma rawan sanyi yake, da sauri ta karasa ciki ta tsugunna agabanshi tace "menene?" ganin ko dago kai baiyiba yasa takai hanunta dake rawa sosai tadan taba wuyanshi da sauri tajanye hanun jin wani irin zafi da jikinshi yayi, fashewa tai da kuka sosai tace "kayakuri bankawo ma abinci jiya da shekaran jiyaba halama saisa kake ciwo, zokaci abinci" hannu tasa zata da gashi ya tunkude ta har saida tafadi ya cigaba da rawan sanyi yana jan hanci, sake dawowa gabanshi tayi tana goge hawaye tadau kulan wainar ta bude ta nunamai sanan ta ijiye gefe tasa hannu ta dago shi ya tashi ta jinginashi da bango, wani

irin rawan sanyi yake tadau kulan ta bashi amma yakasa fizgewa yanda yasaba yi, wani irin mugun tausayi yabata tafashe da kuka sosai, hannu tasaka ta dauko wainar daya tace "ci" bude baki yay kadan yakarba daga gani kasan yunwa yake ji, biyu kawai ya iya ci daga nan bai kara bude baki ya karba ba, hakan yasa ta bude ruwa tabashi shima yasha kadan ya ture har saida ruwan ya zuba afuskar ta bata damuba ta share fuskar, kwanciya yakara yi saikuma taga yafara mimmikewa yana wani irin iri dabaki kaman yanason yay magana amman yakasa, sai kallon sama yake yana wani iri dabaki, matsowa tai kusa dashi duktama rude hakan yasa ta mike tsaye tafita daga wurin dagudu tana kuka har bakin layi, mota ta tare tahau sai gida, Koda takai gida Baba bayanan Mama ta kalleta tace "Ipy kika dawo tun yanzu?" hawaye tasake shareware tace "Baba nake nema" tabe baki Mama tayi tacigaba da kwashe kayan datake yi daga kan igiya tace "ai siki jirashi yaje wani jana'izar abokin shi daya rasu ne" to kawai tace tama fita daga gidan taje chan kofar gida ta zauna tanata kallon almajiran dasuke karatu tana share hawaye Allah Allah kawai take Baba yadawo, sai wajen karfe uku da rabi Baba yadawo tun akofar gidan yace "maiya dawo dake Bana riga nabiya kudin makaranta ba" dan azaton shi ko an korota ne, girgiza mai kai tayi saikuma tafashe da kuka hakan yasa yace "baki da lpy ne?" girgiza mai kai tayi, ahankali ta shiga goge hawayen sanan tace "Baba kawata yar makarantar mu yayan ta mahaukaci ne, yau haukan shi yatashi baida lpy sosai, sai wani iri yakeyi da baki kaman yana magana dawasu, shine suka ce nazo dan Allah kamusu addu'a aruwa dazasu bashi ko zaiji sauki" "sabida hakane kike wanan uban kukan" girgiza kai Baba yayi yace "Allah ya shiryaki, je gida ki kawo ruwa mai kyau agora namiki addu'a aciki saiki kaimusu abashi" da sauri ta koma cikin gidan ta debo ruwa mai kyau agora sanan tafito takawo ma Baba dake zaune akan tabarman shi na Zaure, karba yayi ta zauna kusa dashi, kara ruwan yay abaki yafara karanto addu'o'i daban daban da karatu, yafi awa daya ahaka sanan yay topi aciki yarufe yabata yace "gashi nan ki kaimusu subashi, idan yasha su tofa mai ayatul kursiyu kafa bakwai aka, kulhuwallahu kafa uku a ka falaki da nasi uku aka, inhar sihiri ne wanan addu'a zai Karya shi, inkuma haukar ciwo ne daga ma'aiki to wanan kuma duk lokacin da ubangiji yaso warkar dashine zai warke, amma dai inhar sihiri ne zai karye yabar jikinshi da izinin Allah, i maza jeki kai musu" hamsin yakara cirowa yabata ta karba tawuce harda gudunta takai bakin titi tahau bus, sosai ake traffic dan wai hatsari akai a hanya ba ita takai ba sai wuraren magrib, tana sauka a bus din takara kwasa da gudu zuwa layin da addu'a da shiga ginin.

Juye juye ta sameshi yanata yi akasa Allah kadai yasan meyake mai ciwo, da gudu takara sa gaban shi ta tsugunna ta dukar dakai tana kallon fuskarshi dataga idanunshi sunyi ja sai rawan sanyi yake yana atishawa, kama hanunshi tayi hakan yasa yadan dago kai, da duka karfin ta tajashi tamaida shi kan carpet har tana buga baya da bango ta zauna a gefenshi, goran ta bude takaimai ruwan baki ta kafamai, karba yay yasha sosai dan dama kishi yakeji, saida yasha kusan rabi sanan ya cire bakin yasake kwanciya tareda buga kanshi akasa saida ta runtse ido, ta rufe goran ta ijiye, sake matsowa kusa dashi tayi ta karanta mai su ayatul kursiyu da Baba yace ta karantamai duka ta tofamai aka, takoma ta zauna agefen shi tana kokarin bude jaka dan bashi cingum din data tahomai dashi kozaidan ci, gani tai ya zabura ya mike ya dafe kanshi da duka hanunshi biyu yarda jakan tai tadan matso kusa dashi ta kallai, buga kai taga yay da bango ta fashe da kuka tareda daura hanunta akan nashi tace "kadena kanka zai fashe" buge hanunta yayi yawani kwanta akasa tareda rike cinki shi yana numfashi sama sama kaman zai

mutu, bakaramin tashi hankalin ta yayi ba, rasa abinda zatayi yasa tafita da gudu kozata ga wani amma babu kowa a wajen sai karan speaker wani massallaci dake bayan layin dan wa'azin bayan sallan magriba akeyi, kakarin aman dataji yasa tadawo ciki da sauri cikin shi taga yarike sai amai yake kaman zai amayar da hanjin cikinshi, tsugunnawa tayi kusa dashi dan jitake kaman ta daukemai ciwon, duka wainar dayaci saida ya amayar saikara kakarin aman yake amma babu abinda ke fitowa ragowan ruwan ta dauko takawo mai ya bude tasaka mai abaki yadansha kadan sanan yakara komawa ya kwanta akan carpet din yana wani irin mugun rawan sanyi fiye dana da, daga gani kasan mugun sanyi yakeji rasa mezatayi yasa tacire hijabin makarantar dake jikinta ta rufamai, yarage daga ita sai faran rigar makarantar mai dogon hannu da purple dankawalin makarantar dake kanta ta zauna ata kanshi tana sake tofamai addu'a ganin bai dena rawan sanyin ba, tashi zaune yayi azabure yafada jikinta yawani irin kankame ta yana wani irin nishi da ita kanta saida taji kaman zata suma wajen tsoro ga jikinshi wani irin mugun zafi, duk wani addu'a dayazo bakinta karantashi takeyi tana kokarin tureshi amma takasa sabida wani irin kankameta dayayi fuskarshi akan wuyan ta, sunfi minti goma ahaka ganin gari yasoma duhu sosai dan bamata iya ganin fuskar shi sosai yasa tafara kokarin tureshi danya saketa tatafi gida amma takasa, danko motsa hannu takasa, kuka tafashe dashi sosai tace "ka sakeni natafi gida" ganin baimasan metake cewaba saima jikinshi da ko ina ke rawa yanata wani irin nishi ya kankameta yasa tai shiru tana kuka ahankali zafin jikinshi na kona ta sosai, wani irin tsoro ma taji tanaji yanda takejin kukan abubuwa daban daban awurin tafara karanto addu'o'i tana kuka kasa kasa, jujjuya kanshi taji yanayi awuyan ta yana wani irin nishi kafin yafara bubbuga kanshi akan kafadarta da karfi, tafashe da kuka sosai dan bakaramin zafi buga kan kemata ba, dena wa yayi kafin ya burkito ya gangaro da kanshi kan kirjinta, ya kwantar da kanshi awurin ya kankameta sosai dan kaman zai shige jikinta yana rawan sanyi, wani irin kuka takeyi gabaki daya yawani irin riketa danko motsi, ko numfashin kirki ma bata fitarwa, kuka tacigaba dayi har wani irin wahalallen bacci yay gaba da ita azaunen.

Ahankali yake bude idonshi dayaji sunmai wani irin shegen nauyi ga kanshi dake wani irin fitinannen sarawa, daga hannunshi dayaji yay mai nauyi yay yadaura akanshi yafi minti biyu ahaka kafin yakara sa bude ido gabaki daya yana karema wurin kallo daya cika da hasken rana, bin gabaki daya wajen yay da kallo kafin ya sauke idonshi a inda kanshi yake da sauri ya janye kanshi daga kan kirjin wata faran kakkywan yarinya dayaga ta takure abango gawasu busassun hawaye dasukai layi layi a fuskarta, da sauri ya mike tsaye ganin ajikinta yake yabi gabaki dayan wurin da kallo yana kare hancin shi sabida wani irin wari dayaji wurin nayi, yana komawa da baya da baya, champal dayaji akafan shi yasa ya kalli kafar da sauri yaga kafarshi cikin amai yasa yay wani irin ihu "Fuck! Wah! Ewww" yawani yatsine fuska, afirgice ta bude ido jin ihu tabi wurin da kallo kafin ta sauke kanta akan mahaukacin dataga sai kallon kanshi yake yana mikar da hanunshi sama yana kallon hanun nashi dama duka jikinshi gabaki daya, kokarin tashi tayi amma takasa sabida yanda kafarta yay mugun tsami dan kafarta alankwashe suke daya kankameta jiya, kiciniyar tashi datake yi takasa yasa yajuyo kai ya zuba mata idanun dayasa taji kirjinta yabada wani irin duma dum! Zuwa wajen yay azuciye yawani irin fizgota har saida tai kara sabida yanda kafarta yay kara tace "wayyo Allah kafata" kawad da kanshi yayi tareda saka hannu daya yana kare hanci saikace kashine yazo gabanshi, dan matsawa yay nesa da ita

yana kakkare hanci tareda mata wani irin banzar kallo dayasa taji kaman zatai fitsari, nuna ta yay daga sama har kasa da yatsa yace "who d f*ck are u?".
[7/15, 12:18 PM] Ummi Tandama: ♦♦ *SANGARTATTCE*♦♦

Maman Abd Shakur

11 - 12

Kasa bashi amsa tai ganin maganin Baba yay aiki gashi yaji sauki, bayan hannu tasa to goge hawayen dasuka zubo ta juya ahankali tana dingisawa batare data sake kallonshi ba ta tsugunna da kyar sabida kafarta tadau hijabin ta dake kan carpet tasaka tai hanyar fita daga dakin, wani irin fizgota taji anyi arude tajuyo baiyi watawata ba ya dauke ta da mari mai kyau hakan yasa tafasa wani irin uban ihu ta dafe kuncinta tana wani irin kuka, nuna kanshi yay da yatsa yana kallon fuskarta cikin husky voice dinshi yace "ke kinsan wayeni ina miki magana and u dare walk out of me, F*ck!" yawani dunkule hannu ya daki iska, Muji da tuntuni yake tsaye abakin kofa ya shigo da sauri yazo wajen dan tun jiya da daddare ake nemanta agida, hankalin kowa yatashi, dazu dasafe ma su Umma sukazo duba ko agidansu ta kwana, kotadawo da latti tsoro yasa ta kwana amma batanan hankalin Baaba duk yabi yatashi, yanajin haka yadau keke yafito batare da kowa yaganshi ba hakanan zuciyar shi yace yazo yadubata anan. Karasa shigowa yay yabita da kallo yanda take kuka sosai ga hanunta akan kuncinta da sauri Muji ya kama hanun ya cire daga kan kuncinta ya kalla yanda wajen yay ja duk shatin hanunshi sunfito, fadawa kan Muji tayi tana sheshekan kuka da kyar ta iya cewa "mutafi Ya Muji yariga ya warke" Cireta Muji yay daga jikinshi ya kalli Mahaukacin dasu yake kallo, azuciye Muji yace "uban me kanwata tama ka mare ta haka eh adam, butulu kawai, kasan irin dawainiyar datai dakaine mahauka..." da sauri tarufe mai baki tana kuka tace "dan Allah nidai mutafi gida, yaji sauki shikenan ai" ture ta Muji yayi hartana neman faduwa cike da masifa yace "wlh karki bari na daura miki wani marin nima, tun dazu na tsaya anan ina ganin abunda yamiki uban wayeshi dazai mareki haka? aida kinbarshi anan yacigaba dacin abincin bola banza dakiki mai dukan mata" cakumo shi yayi azuciye da idanunshi dasukai mugun ja ya shake Muji sosai, Muji yafara tari abunku daba karfi daya ba, tashi tayi daga tsugunen datake tana kuka tafara dukan kakkarfan hannunshi da karfi tana kuka. "ka sakeshi, ka saken min wana, wlh ka sakeshi, zaka kashe shi" cire hanunshi daya yay daga kwalar rigar Muji yasa hannun ya hankadeta tafadi kasa, wani irin mukurkusu tayi sabida ciwon ta daya kama mata tafasa ihu sosai. "wayyo Allah na cikina, Ya Muji zan mutu, zan mutu wayyo" juyo da kai yay ya kalli Muji da tsabagen wuya idanunshi sunyi ja sosai, jijiyoyin kanshi sun fiffito yace "duk randa ka kara haduwa dani watch ur tongue and know how u speak to me, bana tolerating raini one single bit get it?" ya tambaye shi fuskarshi a mugun daure dan ranshi yay tsananin baci, gyadamai kai Muji yayi ahankali dan ya shaku wlh, hakan yasa ya sake shi yana kai hanun hancin shi yana tsaki, da sauri Muji yay kanta ganin yanda take kuka kaman zata mutu, dagota yay da karfi tareda saka hanunta daya ta bayan wuyan shi ya taimaka mata ta mike tsaye da kyar, fasa ihu tasake yi zata koma kasa. "Ya Muji bazan iya tashi ba, cikina, Wayyo Allah na jama'a, wayyo na shiga uku na lalace ku taimakeni" ta rirrike shi, Muji dayake ji da bakin cikinta dan ita tajamai wanan muguwan shakan

gakuma tausayin ganin yanda dukta rikice, ahankali yace "toyi tafiya ahankali muje waje mu shiga napep muje gida" girgiza mai kai tayi tafashe da kuka sosai tace "ni kadauke ni idan nai tafiya barkewa ciwon zaiyi ayanda nakejin yakemini" kwalalo ido Muji yay ya harareta yace "to ta ina zan iya daukan ki wai Balkisu, kinga wlh ko kiyi tafiya konabarki anan baruwa na narantse" kara maida hanun nata bayan wuyanshi yayi tana kuka, ya jata da karfi dayaji kaman zasu fadi dan kin tafiya tayi sabida ciwon dake mata sosai, yafita da ita daga ginin ya sakata a keken yana hararan ta yace "ai Allah yakara uwar taimakon cikin ma yafashe banziya kawai" ya watsa mata mugun hararan jiyake kaman ya gwabje ta, ya shiga gaba azuciye danhar yana buge kai, harya kunna keken yakasa hakura ganin yanda take kuka daga gani bakaramin buge ciwon tayiba gakuma wuyan shi daya rikemai dan har yanzu bai dena zafiba. Wlh bazan yarda ba" fita yay daga keken yay hanyar ginin daidai shima mahaukacin yana fitowa sai wani kyankyani kyankyani yake yana kallon kuturun takalmin kafarshi injishi, ganin bolan wajen yasa yay turus ya tsaya yana tunanin yanda zaibi ya wuce, ganin Muji yadawo yasa ya zubamai mayun idanunshi masu kama dana mage, dan komawa baya kadan Muji yayi dan yaune rana tafarko dayaji mahaukacin nan ya mugun cikamai ido, sanan ya  kallai yace "wlh Allah ya isa bamu yafema ba dukan mu dakayi, kaga yarinyar chan daka tado mata da ciwo" ya nuna Bilkisu dake cikin keke ta cusa kanta a cinya tana kuka yace "da kana mahaukacin ka, duk uban dattin dakayi bata kyamace kaba ta kula dakai, ta gyara inda kake zama, tasaka ledar dakake kwana dinchan aciki wanda tundaga gida ta dauko, kullu yaumin saita debo abinci daga gida takawo ma kaci sabida dukan ka ake idan kasatoma yan shaguna buredi, tafasa asusun ta tasiyo ma wanan takalmin dake kafarka sabida yankewa dakayi akafa sabida  rashin takalmi, tasaima wanan rigar jikin naka dan na jikin ka yagama yawo, sanan ta karboma addu'a wajen Baban ta, tabaka kasha ka warke shine ka zanemu ko, to Allah ya isanmana wlh, da marinta da shakeni dakuma fama mata ciwon ta bamu yafeba" yana fadin haka yajuya da gudun bala'i ya shige keken dayariga ya kunna yabar wajen dan gani yay kaman zai biyosu.

Wani irin dogon tsaki yaja kafin yakara kallon bolan yana rufe hanci yafi minti uku ahaka yana tunanin yanda zai tsallaka da kyar yabi bolan tareda runtse ido "jeez, i hate dis sh*t" saida ya tsallake sanan ya bude ido tareda sauke ajiyar zuciya yana tofar ya yawu, kallon dogon layin yayi yana tunanin yanda zai iya tafiya akafa ya shanye layin, sanan ya kalli kayan jikinshi, sake runtse ido yayi tareda shafo kanshi da duka hannu biyu, abinda yatuna na karshe shine yana garden yanacin white rice da pepper soup. Ajiyar zuciya yakara saukewa mai sauti kafin yafara tafiya ahankali dan gabaki daya jinshi yake very very weak ko rabin layin bai shanye ba ya zauna akan wani dakali yana mayar da numfashi, cije lips dinshi yayi kafin ya dunkule hannu yadaki iska. "f*uck wats all dis sh*t?" tunda yake baitaba dogon tafiya akasa hakaba, maganan yaran dayaji agabanshi yan kananu haka suna leken fuskar  shi yasa yabude ido ya kallesu, sunata mai dariya suna waka "waye barawon buredi?" sauran suna amshi "mahaukacin nan shine barawon buredin shagon malam liti mai shayi" saisuyi dariya suna mai gwalo, binsu yay da kallo kafin ahankali ya yunkura zai tashi aiko suka kwasa a guje suna ihu "wayyo mahaukacin yabiyomu Maman mu" bai sake kallon suba yacigaba da tafiya aiko yaran suka cigaba da binshi sunamai wakan mahaukata, ahaka haryakai bakin titi yarasa inda xaisa kanshi baimasan wani gari ne nanba saida garin bai mishi kama da kano ba, haka yadinga tafiya yana

tare abin hawa babu wanda ya kulashi, yafi awa biyu dan harya fidda rai saiga wani dan xpress ya tsaya daga ganinshi kasan dan wiwi ne yace "kai yane mahaukaci Ipy ka tsaya akan titi? Kosai wani ya kwashe ka ya aikaka lahira?" wani irin kallo yama dan Xpress din hakan yasa mai machine din yace "wayihuhu kai wlh kafadama aljanun kanka nafi karfinsu dasuke min wanga kallo dama na tsaya ne nazaci ko wani abu kakeso dan naga tuntuni kake tsaye anan ashe duk cikin haukan ne" burga machine dinshi yayi zaitafi, ganin shine only hope dinshi yace "tsaya" authoritatively yay maganan, kallonshi dan acaban yayi yace "kace mene kai mahaukaci?"  dan shiru yay rasa maima zaice, shi baisama roko ba, bai iya neman taimako ba, jin karan ya kunna machine zai wuce yasa yasake kallonshi yace "inane nan wurin?" "kaman ya inane nan wurin, bakin titi mana?" dan lumshe ido yayi kafin yabude su ahankali yace "wani gari ne nan?" "zaria" dan acaban ya bashi amsa atakaice yana fito "ya muje ne" yanama wani singnal dake tsallake ko tafiya ne yaje sutafi, mayar da dubanshi yay kanshi, kai tsaye yace "ban aran wayan ka?" karkato bakin glass daya saka a idonshi yayi ya kalleshi yace "wayyo ni iskokan kanshi na sona, kai mahaukaci ni wayata na wajen chaji aida nabaka naga uban me mahaukaci na iya da waya" runtse ido yayi jin maganganun shi gakuma zafin rana dake dafamai fata, gakuma gajiya, atsanake ya bude idon ya saukesu akan mai machine din yace "zaka kaini kano chan GRA?" yay maganan yana dafe kanshi sabida saramai dayayi, bin shi da kallo mai machine din yayi yace "ka warke newai? Naga kanata min magana kaman mai hankali, nafa saba ganin ka dan liti nacin ubanka idan kasato mai buredi, yanzu kai to da baka da kosisi mezaka bani idan zan kaika Kanon?" tattaba aljihun shi yayi kafin ya shafa wuyanshi jin chain dinshi na nan yasa yaciro da sauri ya mikama mai machine din yace "24 karat gold chain ne, made in Austria 🇦🇹, worth millions, gashi ka rike ka kaini kano yanzu" hanunshi mai machine din har rawa yake ya karba yana dubawa, gold ne har gold, ga chain din doguwa sosai irin ta maza dinan yan iska, kasa rufe baki yayi ya kalleshi yace "hau, hau muje tasha inada aboki mai mota nasaka aciki mu kaika" kiri kiri yakasa hawa machine din dan baitaba hawa machine arayuwan shiba tunda aka haifeshi, ganin hakan yasa mai machine din yace "dafani saika ware kafarka kahau" dafashin yayi kaman bayaso yana kallon rigar jikinshi da tsabagen datti tai annakiya sanan yay yanda yace saida yakusa fadin da machine din da kyar mai machine din yay controlling ya gyara zaman shi yace "kai kacika karfi" sanan yatada machine din yawani jaa machine din tareda yin awizo ganin yana neman faduwa yasa ya dafa kafadar mai machine din yana yatsine fuska, wani gareje suka je suka sauka mai machine din yay parking machine din suka karasa wajen wani mota, cikin minti goma suka tada motar suka ce ya shigo ya shiga sai kano.
[7/15, 12:18 PM] Ummi Tandama: ♦♦ *SANGARTATTCE* ♦♦

Maman Abd Shakur

13 - 14

Daidai kofar gidansu Muji yay parking keken, lokacin duk daliban sun fita bara dan karfe goma dama ake tashin su, Baba da Isyaka ne duk a tsaye a kofar gidan sunje dogon bauchi makarantar su tsakanin jiya da yau yafi sau hudu nemanta, amma duk basu ganta ba, ganin keken Muji ya paka ga Bilkisun sai rusa uban kuka take yasa Baba yay azamar zuwa wajen

daidai Muji yafito daga keken, anatse Baba ya kallai yace "a ina ka ganta Mujittapa?" kame kame Muji yafara yama rasa wani karya zai shararo da sauri ya juya yafara kokarin fito da ita yace "chan hanyar gidan kawarsu na ganta awani lungu asume Baba" "subhanallah" yafada yana kokarin cirota daga keken da kyar suka fito da ita dan kasa tsayuwa tayi sabida cikin, da taimakon Baba da Muji sukai cikin gida da ita, Isyaka yabisu hankali atashe dan bazai iya daurewa ba ya shiga gidan ganin duka matayen tsaye a tsakar gidan ba lullubi yasa yajuya da sauri yakoma zaure danba karamin kunyan su Mama yakeba.

"La'ilaha illallahu maiya sameta malam?" Baaba tai magana kafin ta kalli Mama dake gefenta tace "dauko tabarma Amina a shinfideta akai" daki Mama takoma ta fito da tabarma ta shinfida anan bakin kofa sabida nanne da inuwa, nan Baba da Muji suka kwantar da ita, da kyar ta kwanta dan kafe musu tai a tsaye wai zafi, Baba zai juya yaje daki yadebo ruwan addu'an daya mata ta kamo hanunshi gam tarike. "Baba, Baba to ina zaka wlh azaba yakemin yamafi na ranan nan, dan Allah ka tsaya kusa dani kaji Baba" tafara daddaga dayar hanunta saman tana neman ruko wani, dan haka take inhar tana rashin lpy to bata barin mutane tabuka komi duk kakkama su zatayi ta rike muku hannu hakan nasata jin kaman ciwon ya ragu, hannun Baaba takamo ta rike gam cikin kuka tace "Baaba kene ko rikeni to, dan Allah kema karki tafi" tasake sakin wani ihun tareda damke hannayen nasu gam. "wayyo Allah na Mama, Mamaaa, Raiyana, na shiga uku Umma, Umma Umma zo kibude min cikin yasha iska" jiki a sanyaye Umma ta tsugunna ta nannade mata rigar makarantar zuwa sama aikuwa wajen yadan kumburo kaman tahadiye karamin kwai a wurin, tagumi Mama tai ta zubama Baaba ido hakan yasa ahankali Baba ta juyo ta kalli Malam dake gefenta ya tsugunna yana mata addu'a sanan ta kalli Muji dake kallon yanda Bilkisu ke kuka tace "wuce katafi nema zataji sauki kaji dan arziki" fita yay daga gidan jiki asake, Malam nagama tofa mata addu'an ya mike tsaye zai shiga daki hakan yasa Baaba tabi bayanshi, sallama tai yabata izinin shiga, zama duk sukayi sanan tafara koromai zance anatse. "Malam wata yar magana nakeson nama dama, bawai inaja da Allah bane kokuma inaso nama shishigi ba, zancen ciwon Bilkisun ne dama, naga tun fa tana shekara sha bakwai abinnan yafara fitomata dan karami kullum saidai aita mata addu'a aruwa tasha ya lapa, gashi har yanzu tana sha takwas amma ana kan abu daya saima kara girma yake, ni dama cha nayi ko za agwada na turawa ne mugani koya kagani malam?" shiru yayi yanadan dogon tunani kafin yace "da yardan Allah haka za'ayi amma akwai wani maganin gargajiya dazan karbo mata wajen wani abokina anjima inhar tasha babu chanji to zamuje asibitin" murmushi jin dadi tayi ganin Allah ya dorata akanshi dan Maman Bilkisu tasha fama dashi akai yarinyar asibiti yaki yarda hakan yasa tafito daga dakin rai fes ta sakan musu murmushi tareda kallon Bilkisun dake baccin wahala har wani irin nishi takeyi abaccin.

*************************

*Kano*

Agaban wani Mansion yasa sukai parking, wanda girman gidan kadai yayi girman wani anguwa fita yay daga motar, su dan acaban sai kallon gidan suke hakadai suka kunna mota sukabar unguwar, tunkarar gate din yayi wanda securities sunfi biyar biyu agaban gate sauran kuma

suna tsattsaye akowani bangare na wajen duk shi suke kallo, hanyar gate yay zai shiga securities din suka tareshi da fuskokin su da babu alamun wasa sukace "wakake nema agidan nan?" wani irin kallo yamusu tareda rungume hanunshi akirji ya zuba musu mayun idanunshi, dayan ne yafara cewa "innalillahi, kai sir ne, he is back" gabaki dayan su tsugunnawa sukai suna bashi hakuri baiko sake kallonsu ba yatabe baki ya shige cikin gida. Bababan gidane dake dauke da motoci kala kala, different part ne agidan har hudu, da sauri yay part din parents dinshi yana kwalama baban shi kira. "Popsy, Popsy" Abba dake zaune a bedroom dinshi ga karin ruwa a hanunshi wanda yakusa karewa ya kalli Mami dake zauna a gefenshi tana bashi yankanken fruits abaki dayake ci da kyar dukya fita hayyacin shi, kaman daga sama sukaji muryan shi. "Popsy" hakan yasa ya ware ido tareda dagama Mami hannu dan yaji ko gizo kunenshi kemai jin muryan Ayaan, sake jin muryan shi yana "Popsy" yasa yamike ya cizge karin ruwan daga hanunshi yafice daga dakin Mami na biye dashi itama.

Shigowa katafaren falon mai kama da aljannar duniya yayi, yan aikin dake sanye da uniform suna kokarin gyara dining suka bishi da kallon waye wanan ammadai basuyi magana ba. "Popsy, Popsy" yakara kwalama baban nashi kira, baki zai bude yakara kiranshi sai yay turus yana kallon fuskar shi ta jikin uban show glass din dake falon da aka jera wasu hadaddun verses aciki, madubi ne gabaki daya, yanda gashin kanshi suka wani mummurde kaman dada ga gemushi busu busu da yanda fatar shi tai wani irin mugun baki ya tsaya kallo shi kanshi yana mamakin shine haka, dan yama kasa gane shine. "Boy!" yaji Abba yakira shi da irin muryan manya dinan wayanda suka kwana biyu aduniya da sauri ya juya yaga Abba akan stairs ya tsaya tareda kama karfen stairs din dan baida karfin tsayawa complete ga Mami itama tsaye a gefenshi duk sun kafeshi da ido.
"Pops" yafada kaman zaiyi kuka yay hanyar benen da sauri, Abba ma yafara tattakala stairs da sauri kaman bashine mara lpy ba. "Boy, Mah Boy is back, Ayaan is back" da gudu da Ayaan yafada jikin Abba ya kankame shi sosai, hakama Abba ya kankame shi ya sumbaci gefen fuskarshi batare daya damu da warin da fatarshi yakeba, sunfi minti kusan biyar ahaka yan aiki sai kallonsu suke suna murna da yau sunsan zasu sami special kyauta dan gatan alhaji da aketa nema yadawo, sakin juna sukayi Abba yay cupping fuskar shi yakara sumbatar goshin shi kafin ya kara rungume shi akaro nabiyu ya sauke ajiyar zuciya, murmushi yay wanda daga rashin yake anya akwai abinda yakeso a duniyar nan kaman Pops dinshi kuwa, sakinshi Abba yay yakara cupping fuskarshi kaman zaiyi kuka yace "maiya faru dakai Boy? Babu wani gidan talabijin da gidan radio dabamu sanar da bacewar kaba, da saka hotunan ka aduka gidan talabijin din Nigeria nan, waye yama wanan abun Boy, yaushe ka girma mema kasani dahar mutum saiso cutarmin dakai, kuma agidana ma, koma waccece maid dinan data baka abinci ranan da sunan ka mahaifiyar ka sai annemota zata gane ta tabamin kaine wlh azim" zame fuskar shi yay daga hannun Abba yawuce ya rungume Mami daketa kallon su tareda daura kanshi akafadar ta ahankali yace "i miss you Mami na" wani kwalla ne yazo mata kafin itama ta ciroshi ta sumbaci goshin shi daidai lokacin Baba Sule ya shigo da Hajiya Saratu (uwar gida) data shigo da kuka sosai ta tsaya agaban shi takai hannu tana shafa fuskar shi tafashe da kuka sosai cikin kuka tace "maiya sameka d'ana, Ayaan haukacewa kayi ashe da gaske dai? Innalillahi wa innaillahi raji'un, duniya ina zaki damu?" cikin kuka takara kallon Alhaji daketa shafa kan Ayaan din kaman zai hadiye shi dan so, tace "Alhaji wlh ko bangon duniya ta shiga

anemo maid dinan data bashi abincin karshe" tasake fashewa dawani irin kuka tafada jikin Ayaan din, dago da kanta yay ya girgiza mata kai tareda sa hannu ya goge hawayen dake zuba daga idonta yace "stop crying Big Mummy, am okay now" gyadamai kai tayi kafin tai murmushi tace "to ya akayi kaji sauki, CCTV footage damuka kalla ya nuna a haukace kafita daga garden din, ya akayi ka warke?" yatsine fuska yay tareda dafa kanshi da sauri Abba ya rikeshi ya kalli Big Mummy yace "ki barshi haka da tambayoyin nan daga dawowan shi muje side dinka ka huta" yarike mai hannu tareda kallon Baba Sule yace "muje Sulaiman" Baba Sulaiman yabisu abaya suna sauka kasa Abba yafara kwalama chief of staff din gidan kira "Mike, Mike" da sauri mutumin yafito shima sanye da uniform yace "call for home service masu massage, manicure, pedicure, da kuma barber dakemai aski be fast" dukar dakai Mike yay yace "to Alaji" ya juyo ya kalli big Mummy yace "kekuma kira Dr Hassan yaduba min shi" ashagwabe ya kalli Abba ya turo baki yace "Pops no basai yazo ba, zanyi prescribing drugs din danake bukata Mike yaje yasiyo min a pharmacy" ahankali Abba ya shafa kanshi yace "are u sure, likita fa baya duba kanshi saidai wani likita ya dubashi" dariya yay a sangarce ya kalli Baba Suleman yace "Baffa tell Pops to leave me alone" duk dariya sukayi kafin Abba yace "shikenan Boy tunda hakan kakeso baza'a kirashin ba" yasake juyowa ya kalli Mami dahar lokacin take tsaye sai kallon dan nata take yace "jekimi shi fevorite dinshi Firdausi, kinsan bayacin abincin yan aiki" da sauri Big Mummy tace "Alhaji tabarshi ni zanmai" girgiza kai yay yace "a'a Saratu, kinsan Boy bayason spicy food kuma girkin ki is way too spicy for his liking, kibarshi Firdausi ta dafamai" yana fadin haka yajuyo ya kalli Mama jummai wacce itace mai gyara bangaren Mami, yanzu ma tagama aikin tane zata tafi taga Ayaan yadawo ai da sauri ta tsaya dan tasan yau akwai buduri zasu sha kyauta harda na innanaha abunka da alhaji mai kyauta bare yau da dalili, Abba yace "Mama Jummai konawa kikeso ga Sulaimanu nan zai baki, kinajina direba ya daukeki kije kasuwa, inaso ahadamin gagarimin girki sanan dukan ku" ya kalli duka yan aikin yace "harda su securities dukku fada musu su gayyaci koma wasukeso azo anjima bayan sallan magriba akwai walima anan" Yasake kallon Baba sule yace "Sulaimanu inaso kaje office kai order motoci dari, and kai contacting dangote company inaso akawo min trailer daya na buhun shikafa araba ma marasa karfin gari Boy yadawo" duka yan aikin sai murna suke, sake kallon Ayaan din yayi dake kallon mahaifin nashi yana murmushi, ya saki hanunshi kafin ya tsugunna yay sujjadan godema Allah na amsa mai addu'a dakuma bayyanar mai da danshi, aiko dakin yadau kabbara kowa saida yay sujjada ganin Abba yayi banda shi gogan daya tabe baki ashagwabe yace "Pops am tired of standing fa" kama hanunshi Abba yay kaman wani yaro ya sanya dayan hanunshi yakamo kafadarshi ya kwanto da fuskar shi kan shoulder dinshi yana murmushi ya shafa uban gemun daya tarun mai yace "sannu dan albarka, muje kahuta kaji" fita sukai daga dakin Mami da Big Mummy dama kowa na dakin suka bisu da kallo, girgiza kai Mami tayi kafin ta sakko ta karaso inda Big Mummy take tace "barka da rana Hajiya" "barkan mudai" Big Mummy ta amsa mata awulakan ce, murmushi tayi tawuce kitchen kasancewar ta mace mai hakuri ko sau daya bata taba biyema Hajiya Saratu sunyi fadaba koma ko mezatayi.
[7/15, 12:18 PM] Ummi Tandama: ♦♦ *SANGARTATTCE* ♦♦

Maman Abd Shakur

15 - 16

Alhaji Abdulrasheed Gwanaye shararan mai kudine dakeda shakaru sabain da bakwai 75 aduniya, su biyu iyayen su suka haifa shi da kaninshi Sulaiman, ya girma Sulaiman dakusan shakara ashirin danhar mahaifiyar su ta cire ran haihuwa sai Allah yabasu Sulaiman, shahararan mai kudi ne Alhaji Abdulrasheed dake business din man fetur, danhar jirgin ruwa dake tsotsomai yanada shi, sanan yanada gidan mai gidan mai daban daban akowana gari na Nigeria, sunan gidan man shi Gwanaye filling Station, cikakken bahaushe ne shi, mutum ne shi mai saukin kai ga yawan kyauta, tun yana da shekara 20 yay auren shi na farko da Saratu sabida yanada son yin aure, suna zaman lafiya sosai bayan shekaru biyar maman shi ta matsa mai ya auri yarinyar makwabciyar ta da mahaifiyar ta ta mutu wato Firdausi, nan fa akai aure dudda Saratu bataso ba amma ganin yanda Mami kemata biyayya yasa tadan sauko haka suka zauna dukba haihuwa.
Alhaji harya cire rai dan har yakai shekaru 45, rana daya kawai Allah ya albarka ceshi da da namiji. Lokacin da aka gane Mami nada ciki bakaramin murna yayi ba yakasa boye farin cikin shi hakafa aka haifi yaro namiji kyakyawan gaske kaman bature, yaro sak mahaifin shi, aka radama yaron suna Ayaan, duk wani son duniya Alhaji ya daurama yaron nan, wani zubin ko abu kakeso kabiyo ta hanunshi shikenan kasamu, nursery da primary kawai yay a Nigeria Alhaji ya fitar dashi waje anan yay secondary yay karatun gaba da secondary ko hausan dayakejima dan yana dawowa gida hutu ne. Alhaji da Hajiya Saratu sun bata yaron, kullum cewa suke yarone idan ya girma zai gyaru da kanshi, Mami ce ke tsayin daka wajen tarbiyan tar dashi amma bata sami goyon bayaba dazaran tafara mai fada zai fara kuka yafada jikin Abba, Abba yadinga bala'i kenan har washe gari shida hajiya Saratu. Baba Sulaiman kadai ne ke supporting dinta. Bari nabar labarin haka zakuji sauran nan gaba.

Part dinshi sukayi wanda yafi kowani part kyau agidan, komi na bangaren ma daban ne, kofar Abba ya bude suka shiga ciki dakine da akai komi na ciki dark blue and white iya haduwa dakin nan yahadu, bedroom suka shiga, Abba ya zaunar dashi akan makeken gadon dakin mai kama da gadon president ya zauna a gefenshi tareda kamo kafarshi yaciremai takalmin ya ijiye yacire dayan ma ya ijiye, daura kanshi yay akan kafadar Abba ya lumshe ido kaman xaiyi bacci, Abba ya shafa kanshi yace "tashi kayo wanka Boy, amma kafin nan" tashi yay ya dauko wani memo mai kyau da byro dake cikin drawer gefen gadon ya mikamai yace "rubuta magungunan da za'a siyoma" karba yay ahankali yana yatsine fuska tareda dan girgiza kanshi, da sauri Abba yace "menene?" daura kanshi yay a kafadar Abba ahankali yace "kaine ke ciwo Pops" rubutun yayi sanan ya mikama Abba takardan, ya karba yana dafa kanshi kafin ya sake rike mai hannu yace "muje kai wanka zakadan ji dadi" ahankali yatashi yabi Abban ya bude mai bayi ya shiga sanan yarufo mai yawuce yafita daga dakin.
Wanka yafara yi, yayi sabi kuwa yafi sabi goma, amma dudda haka gani yake baifita ba, dan kanshi yagaji yafito daga bayin daure da bathrobe yazo gaban mirror yana kallon kanshi, yadan fita tunda duk baki bakin jikinshi sunbace, knocking akayi a kofa ya kalli kofan ya harara kafin ya maida kanshi jikin madubin yana kallon kanshi, kara knocking akayi baiyi magana ba saima

daukan daya daga cikin uban turarukun daga gaban madubin yana kokarin fesawa  yaga anbude kofar, daga kai yayi ya kalli kofar wata maid ce ta dauko tray jikinta har rawa yake ganinshi atsaye da kyar tace "sir, sorry sir, Mami ce tace nakawo ma abincin ka" wani irin kallon wulakanci yamata, hanunta har rawa yake ta ijiye tray din akan gado tajuya tafita da sauri har tana buge kai da bango, yay tsaki yacigaba da abinda yakeyi sanan yakoma ya zauna yadau tray din yana kallo, kasa cin rice din yayi sabida rashin apatite pepper soup na kayan ciki kawai yasha sanan yasa tissue ya goge bakinshi kafin yadan sha ruwa kadan yamike ya kwanta akan gado sai bacci, bawani yi nisa sosai acikin baccin yayiba yaji Abba na kiran shi yana shafamai gashin kai, bude ido yay kadan kafin ya mirgino ya daura kanshi akan cinyar Abba ya cigaba da baccin shi, murmushi Abba yayi yadanyi tapping bayanshi kadan yace "tashi Boy, masu aski sunzo idan aka gyarama kunbunan sai ama massage kai bacci, ince kayi salla?" ba kunya ba tsoron Allah ya gyadama Abba kai, Abba yamike yakamo hanunshi suka fito falon nan fa aka shiga gyarashi Abba kuma na tsaye akansu yana kallon dan nashi dayake ji kaman ya hadiye dan so, duba wani littafin da mai askin yabashi na styles din aski yakeyi sabida yazabi wanda yakeso amai, nan fa yazabo wani aski da ake cema "dakalin shaidan" da sauri Abba ya kalli barber yace "yimai low-cut karkamai wanan" kaman zaiyi kuka yace "Popsy" yawani ja sunan, da sauri Abba ya zauna kusa dashi yaja hancin shi tareda saukar da murya kasa kasa yace "haba Boy, yanzu ka girma yakamata ka daina irin askin nan, kayi low-cut kaji dan albarka zaima fi maka kyau" yatsine fuska yayi tareda cewa "ok" ahankali badan ranshi yasoba aka soma mai askin dayamai mugun kyau yafito shi sak, ana gamawa akamai massage yasha maganin daya aika ya mike sai bacci bai tashi ba sai lokacin magrib, Abba yasake shigowa part dinshi yace "yo alwala mutafi masallaci" dan yatsine fuska yay yace "Popsy kaje bari nai wanka nafito" shiga bayi yay hakan yasa Abba tafiya shikadai, Koda yafito chanza kaya yay zuwa crock t-shirt daya kamshi yafito da six packs dinshi dawani shegen wando crazy jean duk abarke  ya zaxxago yasaka belt ajikin wando batare daya rufe belt dinba ya sanya farar kafarshi cikin bathroom slippers yafita daga dakin sai uban kamshi yake zubawa, bangaren Mami yay bata falo hakan yasa ya haura sama ya tura kofa dayar sallama yashiga dakinta, tana kan dadduma tana addu'o'i hakan yasa ya zauna akan gado yana jiranta tashi tayi ta cire hijabi tana kokarin linkewa tana kallonshi ahankali yace "Mami ina wayana?" ajiye hijabin tai kan gado kafin tazo kusa dashi ta zauna tace "yana wurin Abban ka, maisa bakaje masallaci ba?" yatsine fuska yay yace "nariga nayi adaki" kafeshi tai da ido hakan yasa ya dauke kai da sauri, hanunshi ta kamo a natse ta rike ahankali  takirashi. "Ayaan" juyo dakai yayi ya kalli Mamin kasa kasa yaki bari suhada ido dan ta iya gane idan yay karya, ajiyar zuciya tayi tace "Ayaan wanan abin daya sameka bai isheka ishara ba ka koma ga Allah ba, ka rike salla karike ibada? Sabida rashin azkar da salla ne yasa koma me akama ya kamaka fa, don't you think is high time ka ijiye all dis bad character da bad ways da bazai amfane kaba ka koma ga Allah, nabaka tarbiya iya karfina ka shiga islamiya kasan me addinin ka ya koyar why did you choose to go astray ha? Oya ga dadduma jeka hau kai sallan magrib kar na sabamaka wlh" tashi yayi yafara shiga bathroom ya dauro alwala kafin yazo yay salla yana idarwa ta kallai tace "and kaje ka chanza wayan nan shegun kayan jikin nan naka, yanzun nan za'a cika gidan nan za'a zo walimar da baban ka ya shirya" fita yay daga dakin ranshi duk adagule, maid din daya gani a falo suna fiffito da manya manyan kuloli daga kitchen ne ya dakama tsawa kaman su suka batamai rai yace "kubar falon nan" da sauri kowacce tabace mai daga gani kafin yaja tsaki yafita daga dakin, abakin kofa yaci

karo da Big Mummy taci gayu sosai tana ganin fuskarshi tace "waya batama rai daga dawowan ka yau" kaman zaiyi kuka yace "Mami ne, please big Mummy wats wrong with kayan jikina?" yanuna kayan jikinshi, shafa kumatun shi tayi tace "share ta, daga dawowan ka zata fara takura ma, karka canza, yaro dakai kayan tsofaffi takeso kadinga sawa, jeka abinka zan sa meta, saki ranka kasan yanzu mutane xasu cika gidan" murmushi yay tareda mata peck yace "u are d best big Mummy natafi" murmushi tamai yajuya yatafi part dinshi.

Ba karamin shagali akayi ba sai wuraren goma mutane suka watse ya lallabo yadawo part dinshi danya mugun gaji, wanka yay yazo yay shirin bacci, kwanciya yay sai juye juye yake yakasa bacci idanunshi sunyi ja, agogon dakin ya kalla yaga kusan shadaya, wayarshi ya dauka wanda ya karba daga hannun Popsy dazu yay dailing wani number ringing biyu aka dauka da kyar dan muryan shi batama fita da kyau yace "kisame ni agidana am coming dere now" tashi yay daga kan gadon yadau car key yafita batare daya chanza pajamas din dake jikinshi ba.

[7/15, 12:18 PM] Ummi Tandama: ♦♦ *SANGARTATTCE* ♦♦

Maman Abd Shakur

17 - 18

Mota yadauka security dake gate yabude mai gate yafita daga gidan, agaban wani hahhaden gida yay horn aka bude ya shiga fitowa yay daga mota, daidai lokacin wata kakkyawar yarinyar matashiya haka dan akalla zatai 26 tafito daga wata mota dake parking anan tsakar gidan wacce shine yasai mata, da gudu tayo kanshi tafado jikinshi tareda rungume tsam tsam tana kissing din ko ina na fuskarshi saikuma tafashe da kuka tace "My Ayaan ina kaje? kawai u stop calling me nadena ganinka, naje club dinmu ance suma sun dade basu ganka ba, nazo nan gidan mai gadi ma yacemin bai ganka ba, laifi nama kai abandoning dina like dis eh?" kara fashewa tai da kuka ta manna kanta afadadden kirjinshi tace "koma menawa ka yakuri don't ever leave me like this, nai kewan ka and ur hot screw sosai" fitowa tayi ta kalli daga jikinshi jin shiru ta kalli fuskarshi ganin ita yake kallo yasa tai murmushi takai bakinta kan bakinshi tafara kissing dinshi, matseta yayi sosai har saida tai kara kafin ya dauketa chak batare daya raba bakinsu ba yay sitting room da ita, sanan suka wuce bedroom, kayan jikinta yahau cirewa itama tana cire nashi kafin ya bugata akan gado yahawo gadon yawani chapko yan nonuwan da dabasu da girma sosai yahau matsesu tana ihu, ya dade awurin dan a rayuwan shi yana mugun sonsu, sanan ya shigeta tana maida mai martani tana ihu, sosai suke abunsu har tasoma galabaita fizge bakinta tayi daga nashi tareda tureshi da karfi tace "Ayaan don't kill me nagaji wlh" fizgota yay yace "uban mesa to kikazo inkinsan kin gaji am not done with u yet, and shut d f*uck up" fizgota yay ya sake matseta ya shigeta da kyau nan yacigaba dayin abunda yahana shi bacci agida, saida yaji shi ya gamsu sanan ya ture ta yatashi ya shiga bayi, fitowa yay daure da towel dakuma karami yana goge jikinshi kallon yanda take maida numfashin gajiya yayi yadanyi murmushin gefen baki duk cikin yan matan shi Meram ce kadai maidan iya jureshi gashi ta mutun mai murus, tabe baki yay yadau kayan baccin shi yamaida ya kalleta yace "will

call you tomorrow, idan kin huta kitafi gidan ku, am off" fita yay daga dakin batare dayasake kallonta ba singlet dinshi daya bari akan gadon tajawo ta rungume tana murmushi tana kissing din rigan, tana mugun son Ayaan.

********************

*Zaria*

Kwanan ta biyar kenan tana fama, dan ciwon saiya zo yahade mata da ciwon mara hakan yasa duk ta fita hayyacin ta, Abba ya karbo mata maganin tasha kuma Alhamdulillah tasami Ipy dan yau da kanta ta tashi tai shara, ita dasu Raiyana kuma suka hura wuta suka dumama tuwon da za'ai kari dashi.
Isyaka ma duk ya rame sabida ciwon da gimbiyar shi takeyi dan har saida yay zazzabin kwana daya Baba yabashi magani.

Dakin Baba tai sallama ta shiga ta zauna agabanshi tace "gani Baba" littafin dayake dubawa ya rufe ya mayar ya ijiye yace "ya karfin jikin Bilkisu?" murmushi tai tace "Alhamdulillah Baaba da sauki" gyra zama Baba yay yana kallonta hakan yasa itama ta natsu yace "Bilkisu dama inaso naji yaushe ne zaki fara zana jarabawan gama sakandirin ne" ahankali tace "uhm Baba sai karshen watan gobe, talatin ga watan August zamu fara, sai mugama karshen watan September dan wata daya akeyi ana yi" takarashe maganan tana murmushi, Baba dayay shiru kaman mai tunani yana sauraron ta yace "kuma yanzu muna tsakiyar watan July ko?" gyadamai kai tayi tace "eh Baba yau sha biyar ga wata" ajiyar zuciya ya sauke yace "to Masha Allah daman abinda yasa nakiraki shine, kinga Isyaku zai karayin walima haddace Qur'ani akaro nabiyu ranan goma ga watan gobe, August kenan, shine nakeso ranan na daura muku aure, ranan goma gawatan August din sai ya kasance ranan bikin, nan da sati uku dayan kwanaki kenan, kinga ga aure ga walima abin zaiyi kyau ahaka, idan yaso sai na baku dayan gidana ku zauna aciki dazaran kin gama jarabawan saiku tafi sokoton" boye fuskarta tayi a hijabi duk kunya ya cikata, murmushi Baba yay yace "tashi ki tafi Allah miki albarka su Baaba aiduk sunsan zancen, kin shadai maganin ki nayau ko?" gyadamai kai tayi yace "to masha Allah tafi abinki" fita tayi da sauri ta shiga dakin Umma dake tareda Mama suna hira abunsu, kan Umma tafada tawani fashe da kukan iskanci. "Umma shine ko kufadamin zancen ko" dungure mata kai Umma tayi tace "zancen me bayan keda Isyaku kun kasa hakuri har ki gama jarabawa ai wlh malam yamin daidai dayace kawai ranan walimar shi kawai a daura auren". Tashi tai tayo kan Mama tana kuka Mama ta daure fuska tace "kina zuwa nan saina mammake ki" juyawa tai tafita daga dakin tana kuka sosai mara sauti, nan fa aka fara gyara amarya Umma da Mama, ba abar Baaba abaya bama yau abata wanan gobe abata wancan tasha.

****

*kano*

Wani irin mugun kallo yabi yan aikin dake gyara flowers din side din Mami dashi kafin ya bude kofa ya shiga, stairs yahau yawuce dakin Popsy dake nan bangaren ta, da sallama yabude

kofar ya shiga dakin yabi kowa nadakin da kallo Daga Pops sai Baba sule da Mami sai big Mummy dake kusa da Mami. gaida su yay Mami tabi tsinannun kayan dake jikinshi da kallo ta nunamai kofa tace "wuce kaje ka chanzo kayan nan" "ke firdausi kibarmin yaro fa yasha iska a gidan nan, shida gidan mahaifin shi ba agida yake yasa ba fita yay dasu kinfa takurawa Ayaan dayawa fa" Big Mummy ta chabe tace "atoh! Duk tabi ta gwanzabi yaro, dududu nawa yake dabazai sa abinda ranshi kesoba bahaka yaran zamani kesa crazy jeans dinan suyi ass down ba is normal suwagan kenan, kifita daga idanunshi gaskiya firdausi" "shekara talatin fa hajiya shine yaro? Sa'anin shi nada yara uku wasu ma fin hakan" Mami ta tai maganan cike dajin haushi, "ahap gorin aure zaki mana? Ai aure nufine na Allah ingaya miki, kuma mata saiya dirja ya dirje ta nunawa duniya wlh, ranan bikin shi dole duniya tasan SANGARTATTCE danmu ke aure" takarashe maganan tana hararan Mami ta gefen ido,
shiru Mami tayi bata sake cewa komiba Abba ya kalleshi yace "shigo kaji dan gata na" shigowa yayi batare daya bari sun sake hada ido da Mami ba yawani shege jikin Abba, Baba Sulaiman dai murmushi kawai yay ya girgiza kai dan agidan nan daga shi sai Mami ne ke kokarin gyara Ayaan tun yana yaro amma Abba da Big Mummy son shi ya rufe musu ido basaji basa ganine akanshi.
Shafa kumatun shi Abba yayi yace "kowani irin kaya kakeso kasaka gidan ubanka kake, idan ban maka abinda kakeso ba inada wani wanda zan mawa ne" ya kalli Mami yace "ki kiyayi fushi na wlh, duk randa kika kara batama Ayaan rai nida kene" yay kwafa yasake juyowa ya maida hankalinshi kan Ayaan yace "son yau kusan sati daya da dawowan ka baka bamu labarin yanda kasamu Ipy ba".
[7/15, 12:20 PM] Ummi Tandama: ♦♦ *SANGARTATTCE* ♦♦

Maman Abd Shakur

19 - 20

"Baka bamu labarin yanda kasamu Ipy ba dan from video damuka kalla a haukace kabar gidan nan, maiya sameka bayan nan dazaka iya tunawa?" shiru yayi yana kallon fuskar mahaifin nashi kafin ya maida kanshi kan kafadar shi ya yatsine fuska yace "wata yarinya ce haka Popsy a zaria" saikuma yay shiru Abba yace "wace yarinya Boy? Metayi ita yarinyar? Ya sunanta?" shiru yay yana kokarin tuno sunanta dayaji wanan marakunyan yakira amma yakasa tunawa, karamar tsaki yadan ya yace "namanta sunanta Pops buh her brother yace wai itane ta karbo magani wurin Dad dinta tabani ta dinga kula dani na warke?" Abba yace "yanzu shine baka gayamin tuntuni ba, yaudin ma inda ban tambaye kaba haka zakai shiru ko" shiru yay baice komiba. kallon Baba Sulaiman Abba yay wanda shima shi yake kallo bayan gamajin maganan da Ayaan yayi yace "Sulaiman jeka shirya Zaria zamu yanzu kuwa, muje mu godema iyayen ta da ita yarinyar, sanan kome takeso aduniyar nan wlh sainai mata shi inhar baifi karfina ba dan tamin abinda har na mutu bazan iya biyan taba, ta kularmin da Boy" da sauri Ayaan ya kalli mahaifin nashi murya chan kasa dan bai fiye son magana ba yace "Popsy nifa bansan gidan suba" "badai zaria take ba, koma inane koma kwana nawa zai dauke mu saimun nemota dan

haka kama debo extra kaya?" "ni fa clinic zani Pops inada patients" yawani daure fuska hakan yasa Abba ya sassauta murya yace "to idan baka bimu munje ba tayaya zamu ganeta kaine ai kataba ganinta" kaman zaiyi kuka sabida bakin ciki danyau akwai party da zaije yace "ni namanta fuskarta i can't recognize her kona ganta" shiru Abba yay saikuma yakamo kafadarshi tareda jan hancin shi da dan karfi hakan yasa yadanyi murmushi, murmushi shima Abban yay yace "to me zaka iya tunawa ranan dai daka gansun?" shiru yadanyi saikuma yace "wanta nada wanan abun da ake xpress dashi?" Abba yace "machine?" girgiza kai yay yace "a'a ni bansan sunan abin ba, but yellow ne kaman car kaman bike" da sauri Baba Suleman yace "keke napep?" shiru yadanyi jin kaman ranan fa yaji yaron yana cewa napep hakan yasa yace "i think so" Abba ya sauke ajiyar zuciya ya kalli Baba Sulaiman yace "ya za'ayi kenan?" Baba Sulaiman yace "yanzu dai idan munje zai fara kaimu inda yatashi yaganshi ne daganan kuma zamu iya tambayan mutanen wajen idan babu wanda yasansu saimu je duk inda yan keke napep ke taruwa ko parking mu binciko wannata aikasan sunanshi ko?" ya jefoma Ayaan dake danna waya yana jinsu tambaya, maida wayar yay aljihu tareda saukowa daga gadon yace "am not sure but i think she called him Muji" Abba yace "shikenan jeka shirya kasa manyan kaya kaji Boy" shiru yay bai amsaba yafita daga dakin duk ranshi adagule, Big Mummy ta mike tace "Alhaji mu shirya mubiku muma?" girgiza kai yay yace "a'a kudai hadamin kaya, muda bamusan gidan suba idan mun gano gidan next zuwa aiduk sai mu shirya mutafi tare". Ranta bai soba haka tai wajen Wardrobe Mami ma tatashi suka hada kayan tare.
Saida Abba yaje part dinshi da kanshi ya ganshi a kwance sai wani cin magani yake, murmushi yay yawuce gaban wardrobe dinshi yaciro mai manyan kaya shadda fara da blue sai kuma yadi mai laushi black daya ijiye mai agefen gado da hula kube agefe dakuma su singlet da boxers, sauran kuma yahada a akwatin shi karami ya dau turarurukan shi yasaka ciki yarufe sanan ya kwalama Mike kira ya shigo dakin da gudu ya bashi jakan yace "yaje yasaka a mota" karba yay yafita, sanan Abba yadawo gadon da kyar ya lallaba shi ya shawo kanshi sanan ya yarda zaisa kayan, kafin yakamo hanunshi yakaishi bayi sanan yabarmai dakin.

Koda suka fito za'a tafi bai fitoba, Abba yakara komawa part dinshi Mami tabishi da kallo tana girgiza kai dan wlh bata data cewa amma abu na Alhaji ya isheta, tare suka fito da Abba yawani sha mur bakaramin kyau manyan kayan sukamai ba bakin soft yard ne da akamai dinkin half jumper daya kama jikinshi yafito da murdaden jikinshi sosai, ga yadin ya haska shi tareda kara bayyana farin fatar shi da pink lips dinshi, harara Mami ta watsamai dasuka hada ido hakan yasa ya dauke kai da sauri, Abba daya kamata lokacin data harare shi ya nunata da yatsa. "kifita daga idona fa Firdausi wlh inkikace xaki takurawa yaron nan zamu zuba dake nefa" gidan gaba ya budemai yashiga dudda akwai body guard dake wajen wanda aikinshi bude kofa ne, Baba suleman ya shiga baya, driver Abba ya shiga mazaunin shikuma Abba yakoma baya ya zauna Mami da Big Mummy suka musu Allah kiyaye hanya suka tafi.
Wuraren azahar suka shigo zaria agaban wani massallaci suka tsaya sukai salla sanan suka kara shiga mota hakadai yadinga nuna musu hanya har gaban bolar nan.
Kin fitowa yay daga mota saidai ya nuna musu ginin suka shiga Abba harsaida yay kwalla babu komi a wajen sai carpet din data sakamai, fitowa sukayi suka shiga motar Abba nata kallon fuskar shi ta madubin kofar mota yana mamakin wakeson halaka mai da, shi baimasan Abba na kallonshi ba dan danna waya yake. Duk wani samari dazasu gani a anguwar saisun tambaye

shi koyasan Muji suce basu saniba, hakadai har suka fara zuwa duk inda sukaga yan keke napep sunyi parking suce basusan wani Muji ba, har akai sallan la'asar suka tsaya sukayi suna fitowa yace "Popsy ni am tired fa" "shikenan to muje hotel kahuta gobe macigaba da neman sun" wani hadadden hotel sukai lodging a The Fabs anan suka kwana, washe gari tun wurin 8 Abba ya shigo yatashe shi yace ya shirya su cigaba da nemanta kaman zaiyi ihu haka yatashi ya shirya cikin farar shadda ya dauko black shade yasaka ta sanan yafito sai uban kamshi yake mai shegen dadi fuskar nan daure kaman zai fashe.
Tasha tasha haka suke zuwa har wurin karfe biyu suna abu daya, ata bakin kasuwan tudun wada sukai parking inda masu keke napep ke parking Abba da Baba Sulaiman ne suka fito suka gaggaisa dasu suka tambaye su ko sunsan wani mai keke sunanshi Muji, wani daga cikin su ne yace "Mujin filin mallawa?" shiru Abba yay chan yace "wlh bamu san dan ina bane mundai san sunanshi Muji" mutumin yace "to bari nakira shi kuga ko shine" godiya Abba yamai cike da fara'a aiko yana gama wayan mutumin yace" yace gashi nan zuwa" Kudi Abba yaciro masu yawa yamasu kyauta aiko sai murna suke nan fa suka fara koda yazo inba shi bane koma waye yake nema saisun nemomai shi. Abba yadinga godiya dan shi mutum ne mai fara'a mara girman kai, dason mutane idan yafita baruwan shi baya yanuna shine mai kudin nan da Nigeria keji dashi. Shidai gogan yana mota abinshi iskan Ac na hura shi yana danne danne awaya dan Meram ta isheshi da message.

Cikin minti talatin saiga Muji yazo da keken shi yay parking yafito, ya kalli abokin daya kirashi yace "Maska yane tasamu ne wanan kira dakamin ina masu nemana din?" daidai nan Abba da Baba Sulaiman suka taso daga  jikin mota dasuka jingina, dafashi dayaji anyi yajuyo ganin magidanci ne yadafa shi yaci uban babbar riga yasa yay murmushi tareda dan dukar dakai yace "ina yini alaji" murmushi Abba yay yace "Mun wuni Ipy, yar tambaya nake dan Allah Kaine Muji" gyada kai yay yace "eh sunana Mujittapa amma Muji ake cemin, kaikasa akirani Alaji dafatan dai Ipy?" murmushi Abba yasake mai yace "Ipy kalau, dan Allah tambaya nakeson nama kaine kokuma nace kasan wani mahaukaci haka achan wata anguwa haka gaban wani Bola a sabon gari. "wanan mara mutuncin mahaukacin na hanyar dogon bauchi, ai yariga ya warke Alhaji, kanwata data lura dashi tun yana sato buredi ta dinga kawomai abinci yanaci daga bayama ta karbo mai magani wurin baban mu tabashi yasha shine yana warke wa ya zanemu dagani har ita, ya kwada mata mari nikuma ya shakeni yakusa kasheni ai namai Allah ya isa wlh" tunda yake maganan Abba yakasa dauke ido akanshi, saida ya ijiye maganan sanan yace "shine ya shakeku?" da sauri Muji yanuna mai wuyan shi yace "kagani alaji har yanzu wuyana bai dawo daidai ba, har yanzu da shati shatin jan dayayi" dan murmushi Baba Sulaiman yayi dan so kawai yake yaga me Abba zaiyi, ga mamakin shi sai yaga Abba yarike hanun Muji yace "zokaga wani abu" kofar gaban motar ya bude daidai inda Ayaan dake chatting yake, bakin glass din fuskarshi Abba ya cire hakan yasa Ayaan dago kai ya kalli Abba, Abba ya nuna Ayaan da hannu ya kalli Muji yace "wanan ne ya shake kan?" shiru Muji yay yako kafeshi da ido shima Ayaan Mujin ya kalla rass ya ganeshi amma yawani basar ya cigaba da danna wayar dayake yi, ta kwayar idonshi masu kama dana mage muji ya gane shi dan har gobe bazai manta da idanun mahaukacin daya shake shiba aiko ya ballamai harara ganin ya dauke kai ya kalli Abba yace "shine alaji" Abba ya daure fuska tamau yace "Boy dama abinda kama wayanda suka taimake ka kenan dan iskanci, oya bashi hakuri right dis minute" tsaki Baba Sulaiman yaja aranshi dan

yazaci Abba zaidan zubama Ayaan mari ne ya ramama yaron amma ina bazai iyaba, tashi ma yay daga wurin yakoma bayan mota ya bude ya shiga abinshi ya xauna. Ayaan dako dago kai baiyiba Abba yace "badakai nake ba bashi hakuri" dago kai yay ya zubama Muji ido batare dayace komiba, bakaramin kwarjini yama Muji ba, dauke kai Muji yayi ya kalli Abba yay murmushi yace "haba alaji basai yabani hakuri ba, mu dan Allah muka yi kumama wlh inda nasan dan kane daban fadama ba saiyanzu naga kaman ku wlh kaman kai kaki" murmushi Abba yay kaman bashine ya daure fuska ba yanzun nan yace "nagode dan albarkan yanzu kaimu gida mu godema mahaifin naka da ita yarinyar ko" rasa yanda Muji zaiyi yasa yakoma keken shi dan kunyan tsohon yake ya kunna keken shikuma Abba yashiga mota sukabi keken nashi abaya har kofar gidan su Bilkisu dake cike da almajirai anata karatu.
[7/15, 12:20 PM] Ummi Tandama: ♦♦ *SANGARTATTCE* ♦♦

Maman Abd Shakur

21 - 22

Parking Muji yafara yi kafin babbar jeep dinsu kirar range rover tai parking, Muji ne yafara fitowa kafin Abba da Baba Sulaiman, gaban motar Abba yabude ganin baida niyyar fitowa ya kalleshi yace "fito mah boy" fitowa yay sai wani cin magani yake, Abba yasa hannu yacire shegen bakin gilashin dake idonshi tareda turawa a aljihu, Muji ya kalli Abba yace "bari nagaya mai" shiga zauren yayi almajiran dai sunata karatu sai kallon su Abba suke, karasa wa zauren Muji yayi ya tsugunna agefen malam dake biyama wani karatu saida yagama sanan ya dago kai yace "Mujittapa ba'aje sana'a bane yau" dariya yay yace "Baba baki nakawo ma, kai ake nema suna kofar gida" Baba ya mike tsaye yace "muje" fita sukayi daga xauren shida Muji, Abba na ganinshi ya washe baki dudda zai girmi Baba bai hanashi dukawa ba lokacin daya mikomai hannu, shima Baba kunya yaji ya duka ya karbi hanun nashi suka gaisa, sanan ya mikama Baba Suleman hannu suka gaisa, bugeshi Abba yay tabayan shi hakan yasa yamikama Baba hannu yanadan murmushin dabaikai ciki ba yace "barka da warhaka" karba Baba yay cike da fara'a dudda dai bai sansuba amma yaga kaman daga gani dan tsohon nanne, ya kalli Muji yace "shiga gida kace su gyara zan shigo da baki" da sauri Muji yajuya yay cikin gidan yayinda Malam yajuya aka cigaba da gaishe gaishe kaman ansan juna, Muji yafito yace "Baba zaku iya shiga" Malam ya kallesu yace "to Bismillan ku" Muji ne yafara gaba Baba biye dashi abaya sai Abba daya fizgo hannun Ayaan da baida niyyar zuwa sai kallon almajiran yake kaman baitaba ganiba, daure fuska yay yabi Abba suka shiga zaure ya nunama Abba allo yana wani yatsine fuska yace "wats dat Pops" gaba Abba yay abinshi ya barshi tsaye yanata kallon bangon da yaran daketa kallonshi suna washemai wani harda lashe majinan daya fito daga hancin shi da sauri yajuya ya tabe baki kafin yabi bayan Abban nashi dayaga ya bude kofa suka shiga cikin gidan dake a gyare tsaf dashi, simintin sai kyalli yake, babu kowa a tsakar gidan sai kamshin turaren wuta mai dadin kamshi dake tashi, iso Malam yamusu afaddadden falonshi dake gyare tsaf an shimfida babbar tabarma a tsakiya duk suka zazzauna sai bin dakin yake da kallo yanda yaga littatafai kala kala sun cika bangon dakin an jerasu kaman mesuim, Baba ya kalli Muji tareda ciro kudi a aljihu yace "jeka sawo ruwan gora" ganin yanayin su na yan gayu ne, da sauri

Abba yace "ina ga randa nan ina gani kawani ce ruwan gora malam, ban yarda ba gaskiya" yay maganan yana nuna randar dakin yana dariya, tashi Muji yay yadebo ruwa ya cika babbar jug din malam mai tsafta yadaura akan tray dinshi sanan ya sanya kopuna biyun a kai yakawo musu Abba ya karba yana washe baki diba yay yasha Baba Sulaiman ma yasha ruwan dadi ga sanyi, tsiyayawa Abba yay ya mikama Ayaan dake gefenshi duk atakure, murmushin dole yay yace "ina azumi kamanta ne Popsy" shanye ruwan Abba yay sanan ya ijiye cup din, Baba yay murmushi yace "Masha Allah sassannun ku da zuwa saidai ban ganekuba wlh" Muji ne yadawo kusa da Baba yace "Baba uhm dama" saikuma yakasa magana Baba yace "ina jinka" ahankali Muji yace "Baba dan Allah kayakuri daga ni har Bilkisu bamu fada muku komi akaiba, dama akwai wani.. ...." nan Muji yafadi ma Baba komi, Abba ya chabe da. "Malam babu abinda zamu iya ce muku sai ubangiji Allah ya saka da alheri yakuma biya bukata yakara daukaka ka, ai da Ayaan yafada mini shine muka shirya tundaga kano mukazo neman ku, munsha wuya kafin mu gano nan, Allah ubangiji ya biya muku bukatun ku duniya da lahira, yanda kuka taimaki dana kuka sani farin ciki ubangiji Allah yasaku ku farin ciki ranan gobe kiyama, watana daya da kwana goma sha biyu banga Ayaan ba rana daya kawai yadawo ta sanadin ku, nagode nagode malam" murmushi Malam yay yace "Ameen Alaji mugode ma Allah, a'aa ikon Allah kaji magana fa, shine kuma yaran nan sukamin karya, inda ace Bilkisu tafadamin ai danasa ma har gida anje an dauko shi namai addu'a nabashi magun guna anan, to ubangiji Allah ya kara mana katanga da makiyan mu, ko lokacin dana bata addu'an nace mata inhar sihiri ne dazaran yasha zai karya ashe kam sihirin ne" Abba ya girgiza kai cike da damuwa yace "bamusan waye ke neman shi da shairi hakaba, amma muna kan rokon Allah daya bayyana mana gaskiya" Baba yace "ai wanan ba matsala bace zan bashi addu'o'i dazai dingayi kullum safe da maraice in sha Allah babu abinda zasuyi dazai kara kamashi da izinin Allah kuwa dan kariya ce" Abba da kaman yazuba ruwa akasa yasha yace "mun gode, mun gode akaramakallahu, Allah ya biya bukata" sukadan yi shiru shidai Ayaan kanshi akasa Allah Allah kawai yake Pops yagama surutun shi sutafi, gashi yakasa daddana waya hakanan yaji malam ya cikamai ido, maganan Abba ne yadawo dashi daga zancen zucin dayake yi. "Malam ina diyar naka Bilkisu zanzo mu ganta mu kara yimata godiya idan ba damuwa" murmushi Baba yay yace "tana makaranta chan dogon bauchi, dayake na rana takeyi sai biyar da rabi zata dawo" Abba yay shiru chan yace "inba damuwa zamu jirata tadawo Malam" Malam yace "babu komi ai tama kusa tunda gashi yanzu hudu saura" nan fa hira yakachame tsakanin Abba da Malam da Baba Suleman kaman sunsan juna ataba nan ataba chan, suna yin la'asar Muji yamusu sallama yatafi nan Umma ta gabatar musu da abincin da aka dafa musu farar shinkafa da jar miya bayan ta gaisa dasu ta fita, abincin su Abba sukaci sosai abinsu dan wlh yay dadi.

Wuraren biyar da rabi ta shigo gidan nasu da sallama a gajiye, tun awaje take mamakin babar motar data gani a pake akofar gidan su, gashi kuma gidansu nawani fitinannen bakon kamshi, abakin kofar su ta zaunar ta ijiye jakan makarantar ta agefe tana kokarin cire takalmi da safa dan bama ta lura da takalman dake gaban kofar dakin Baba ba, cikin yar siriyar muryan ta ta kwalama Maman su kira "Mama nadawo" safan tacire tarike su ahannu tana kallonsu ganin sunyi datti yasa ta taka farar kafarta datama jan lallin salatef jiya dayay kyau sosai zuwa wajen botikin dake gefen rijiya ta wurga zafan tajuya zata shiga daki taji muryan Baba daga dakinshi

yana kiranta. "Bilkisu" "Na'am Baba" tajuya zata tafi da sauri Raiyana dake falo zaune tace "Baby bakine fa kizo ki chanza kaya" turus tai a tsakar gidan tana kallon takalman da sauri tadawo daki hijabin makarantar kawai tacire sanan tadau pink hijab dinta data goge dake makale ajikin kusa tasaka, har kasa hijabin ya kaimata mai hula aiko bakaramin kyau yamata ba yafitar da baby face dinta sosai, ko silifas bata sakaba tai hanyar dakin Baba, abakin kofa tai sallama sanan ta shiga, gani tai kowa na dakin ita yake kallo banda mutum daya da kanshi ke kasa, murmushi tadan kakalo daya lobar da dimple dinta sanan ta shiga tsakar falon, dukawa tayi tafara gaida wanda bata ganin fuskarshi danya dukar dakai, sanan tadan matsa batare data jira amsar shiba ta gaida tsohon na tsakiyan su wanda tunda ta shigo yake kallonta yana washe baki ahankali tace "ina yini Abba" murmushi Abba yay yace "andawo yan makaranta Bilkisu ya karatu?" a kunyace ta sunnar dakai tace "Alhamdulillah Abba" sanan tagaida Baba Sule da shima ya amsa mata cike da fara'a kafin ta koma gaban Baba ta tsugunna kusa dashi tace "gani Baba" Baba da tunda tashigo yake kallonta yadan nisa yace "wajen ki akazo?" dan zaro ido tayi dan bataga wanda tasani cikin suba hakan yasa Baba ya gyara zaman shi ya fuskanceta da kyau yace "yaushe kika faramin karya Bilkisu? Maisa baki gayamin gaskiya ba ranan dakika zo kika karbi addu'an nan? Eh? Inda nasan gaskiyar zancen aidana hadaki dasu Isyaka kun kawoshi nadinga mai magani agida" rasa abinda zatace yasa tafashe da kuka mara sauti, jikinta ta har rawa yake tasa bayan hannu ta goge idanunta ahankali tace "Baba kayakuri, tsoro nakeji na dauka xakamin fadane" takarashe maganan cikin kuka, akaro nafarko kenan daya dago kai yadan saci kallonta da sauri ya kawad dakai kuma. Malam ya nisa yace "shikenan ya wuce haka Allah ya kaddara faruwan lamarin, gashin nan shida iyayen shi zunzo yimana godiya tun dazu ke suke jira ki dawo daga makaranta, daga kano suke"Juyo dakai tai tadan saci kallon su daidai lokacin shima yasake dago kanshi suka hada ido da sauri ta janye nata kirjinta na bugawa, yanzu wanne ne dama mahaukacin nan kai anya kuwa. Maganan Baba yadawo da ita daga duniyar tunani ya kalli su Abba yace "bari indan leka yaran nan Alaji" Abba yace "to Malam, saimun fito muma" fita Baba yayi Abba ya gyara zama ya kalleta yace "yar arziki Allah yamiki albarka y'ata, yabiya miki bukatun ki duniya da lahira, duk mai taimako baya tabewa ladanki na wajen Allah, Allah ubangiji ya baki duk abinda kikeso anan duniya da lahira banda abinda xan ce miki Bilkisu amma nagode, nagode, Ayaan yafadan mana abinda kika mai shine mukazo mu gode miki, Allah ya saka da alheri" wani irin kunya ne ya lullube ta mutumin da yamafi Baba tsufa ne yaketa gode mata haka lullube fuskar tai da hijabi kanta akasa hakan yasa Abba yay murmushi sosai ya kalli Baba Suleman yace "kaga yar albarkan kunyamu take ji, zomu basu waje sabida shima yamata tasa godiyar" yay maganan yana hararan Ayaan dake kallonshi kaman zaiyi ihu, fita sukai daga dakin sukai zaure wajen Baba, hakan yasa dakin yay shiru tamaki dago kai sai wasa take da yatsunta dasuka sha jan lalle a kumba.

Daga chan tsakar gida Raiyana ta kwala mata kira. "Anty Baby kizo wai" tashi tayi ahankali batare data kalleshi ba tafita daga dakin, Raiyana dake wurin zaure tace "Baba yace kikai mai charbin shi" tana fadin haka tafice daga gidan ahankali tajuya jiki asanyaye tai hanyar dakin Baban idanunta ne suka sauka akan Layla dake labe a kitchen tana mata game da waya, "lalala wayata Layla jeki ijiye kafin kija arufemin sim" tai maganan tana tafiya, tana kaiwa bakin kofar Baba takara juyowa ta kalli kitchen din dan taga ko Layla ta ijiye wayar ganin bata ganta ba yasa tahau kan dakalin da zaka tsallake ka shiga dakin Baba, ta kama labulen ta rike gam kafin ta daga kafa tana leken kitchen din ta window ko ta labene awani wajen, daidai lokacin shikuma

yazo zai fita yasa hannu yakama labulen yaja zai bude, jan labulen dayayi yasa kafarta ta turgude tayo baya gabaki daya tafada jikinshi tabaya tareda sakin labulen yakoma jikin kofa, mugun firgitan datayi ne yasa takasa motsi saima sauke ajiyar zuciya datake yi jin kirjinta kaman zai fado waje gashi takasa juyowa takuma kasa barin jikinshi, kafarta datasha jan lallin salataf yabi da kallo yana kallon gashi gashin ta daya leko ta hular hijabin ta zufan datayi yasa sun kwanta luplup, yafita tsawo sosai hakan yasa har kwakwalwanta yana gani, hannu yasa ya juyo da ita atsorace ta kallai, daure fuska yay kaman baitaba dariya ba yace "banason rawan kai, ki natsu, karki sake barin irin haka yasake faruwa" yay maganan yana mata wani irin kallo sanan yawuce yafita daga dakin cike da izza duk takun dazaiyi saitaji a kirjinta harta dena ganinshi, tafi minti biyu a tsaye a wurin sanan ta share yan guntun hawayen dasuka zubomata ta rufo kofar tafito tai dakinsu.
Sai bayan sallan magrib suka tafi Baba yamusu rakiya har wurin mota sanan yakoma ciki, ba'a dadeba saiga amajirai sun kawoma malam manya manya ledoji da rapan kudi yan dubu daidai guda biyu malam baiyi niyar karbaba yafita waje da sauri dan ya maida musu amma harsun tafi haka yadawo yabama su Isyaka leda daya su rarraba tunda kayan kwalama ne dayan ledan kuma ya shiga gida dashi da kudin.

Abba ne zaune gefen Ayaan dayay bacci abinshi a dakinshi na hotel yay tagumi yana kallon fuskar Ayaan yayinda dayar hanunshi ke shafa kwantacen gashin shi, sosai ya zurfi a tunani hoton Balkisu yakasa barin ranshi, for d first a duniyar nan yaji lokaci yayi da Ayaan zai ijiye mata ya ijiye iyali zaizo yaga jikokin shi kafin yabar duniyar nan, yana mugun kwadayin ma Ayaan Bilkisu, yarinya hafiza, ga ilimi natsuwa da kunya ai itace tafi dacewa da Ayaan sanadinta hala ya natsu. Sai wajajen karfe daya sanan yabar dakin Ayaan din yawuce nashi.

Misalin karfe biyar na yamma suka fito daga cikin school dan anatashi su biyar ne na yamma, suka jero ita Aisha shehu, Walawa, Fa'iza dakuma Fatima, itace a tsakiyar su cikin dogon farin hijabin ta dayasha guga da wandonta purple kafarta sanye da farar safa tasaka brown takalmin makaranta mai igiya, babu komi a fuskar ta sai kwalli dakuma mai data shafa a lips dinta bayan sallan la'asar wanda yasa har yanzu pink lips dinta ke shining sosai da black din abin sai yay kaman tasa jan baki, murmushi dukan su sukeyi dan Fa'iza ke basu labarin yanda sukai da saurayinta jiya dayazo tadi sunata murmushi, bayan Fa'iza tagama duk sukai dariya, takara yin wani irin murmushi daya lobar da dimple dinta tana dan tunani tace "niko jiya da Isyaka yazo ko" sai kuma tai shiru tana fari da ido hakan yasa Walawa ta dafata tace "fada mana yar malam meya faru dayazo ke badai ya mammatse kiba" hararan ta tayi tace "Allah kyauta bama iskanci mu" murmushi duk sukayi suna kallonta, sai kuma tasake yin fari da ido tace "anbiya shi kudin aikin hannu shaddan dayayi aiko ya siyomin ice cream jiya, muka sha nida su Raiyana" ihu suka hau yi suna tafi. "woh ke woh ke, ashe dai ustaxai sun iya soyewa su isyaku an iya sawo ice-cream" dariya tai kafin ta dauke kai tace "an sa fa, nan da 2weeks da some days ne?" "mene!" dukan su suka tambayeta atare Aisha Shehu ce tace "amma kin cika yar iska Billyn Malam, keda kikace mana sai bayan kun gama exam?" kaman zatai kuka tace "wlh bahaka bake fa, Babane yace ranan walimar shi kawai ahada da auren" duk shiru sukayi suna tafiya ahankali saikace ba gida zasu ba sai kallon su take tana murmushi, chan Walawa tace "inko

hakane bazamu yarda ba wlh dole mutaba mu mulmula su kafin Isyaka yataba" ihu sosai tayi da saida sauran daliban gabansu suka juyo ta arce da gudu sosai tana dariya saida ta musu nisa sosai dan har bata hangosu sosai sanan ta jingina dawani mota tana mayar da numfashi tana dariya tana kallon layin data kusa kurewa da gudu, kirjinta ta dafe tace "wayyo Allah na" jin yanda ya wani irin buga sanan tacigaba da nishi tareda lumshe ido tana kokarin saita numfashin ta, wani irin kamshin turaren kamshi daya daki hancin ta yasa ta bude ido ahankali ta saukesu akanshi ya tsaya agaban ta yay folding hannu akirji yana sanye cikin wani black bodyhug daya kama shi dan kana ganin layi layin six pack dinshi, da fadadden kirjinshi dake nan kaman ya rabe biyu, sanan hannun rigar yakama muscle 💪 dinshi jijiyoyin sun fito, kafara shi cikin wani original tomford sneakers, ya sanya wani dan iskan crazy jeans dayay tokin rigar aciki sanan yasaka belt mai bala'in kyau, kana iya hango sarka dake kyalli ta wuyarshi gawani sheken dan kunne na diamond wanda maza ke makalawa da gum, dan dan kunnen da gum dinshi yake zuwa, idanunshi sanye cikin dark shade da bata iya tantance mema yake kallo, yanda ya tsaya a gabanta sosai yasa tama kasa janye jikinta daga motar dan go tafiya daya kacal tayi zata iya gogan jikinshi ta lafe ajikin motar numfashin ta nafita da sauri da sauri, hannu yasa a aljihun bayan wandon shi yazaro bandir din kudi yan dubu daidai ya rike kudin kafin ya kalleta, kanta akasa tana wasa da bakin hijabin ta, wurgamata kudin yay a fuska wanda har saida ya bugi bakinta kafin ya fadi akasa tsakakanin kafanta, yabi kudin da kallo sanan ya tabe baki yace "Pops ne yadaman nabiyo ki school dinku namiki kyauta, so here u go" yajuya yay inda ya paka mota zai shiga, bin kudin tai da kallo ranta ya mugun baci da sauri ta share hawayen dataji ya zubomata ta tsugunna ta dauki kudin ta mike ta kalli motar daya shiga ganin baibar wurinba yasa tai wurin motar, kai tsaye tabude daidai lokacin ya dauko bottle water ya bude zaikai baki, ajiye mai kudin tai akan cinya ahankali tace "nagode amma ni bana bukatar wani abu daga wurin ka" tajuya zata tafi karaf taji yarike wutsiyar hanunta, da sauri ta juyo taga bama ita yake kallo ba saima kai bottle din dayay bakinshi yana shan ruwan shi a natse, duk iya karfinta takasa kwance hanun gashi duk yan makarantar su dazasu wuce nata kallonsu duddu su Walawa basu riga sun karaso ba, zafin dataji hannun nayi yasa hawaye ya gangaro mata a kunci, saida yagama shan ruwan sanan ya ijiye bottle din ya juyo da kanshi ya kalleta tareda cire bakin glass din idonshi ya ijiye a gefe ya kafeta da idanu da sauri ta janye nata ta cigaba da kokarin fizge hanunta, muryar ta har rawa yake tace "ka sakeni natafi gid..."  "ke!" ya daka mata tsawan da batasan lokacin data fashe da kuka ba ta hadiye sauran maganan, wani irin mugun kallo yamata dayasa ta hadiye hawayen tarasa mesa take shakan shi haka, cikin wata irin kakkausar murya yace "kinsan wayeni kuwa?" dan murmushin gefen baki yayi dayawani irin karamai kyau kafin yasake damke fuska yace "Am Dr Ayaan, a doctor, double degree holder, masters holder and PhD holder, am a surgeon and a pathologist, mace bata kawomin wargi, babu abinda bansani ba na mace, so ki kula! Ki natsu! I don't take shit! dan haka pick dis money and get out of my sight" yafada cikin tsawa tareda jawo hanunta daya damke tun dazu ya daura kan kudin yamata wani irin kallo dayasa ta bude hannun da sauri ta dauke kudin sanan ya turata dahar saida tafadi kasa yaja motar dawani irin gudu yabar wajen yana tsaki, baisan mesa Popsy kemai wanan abinba wlh me zaiwani sa yazo nan, thank God yau zasu bar garin.
[7/15, 12:21 PM] Ummi Tandama: [7/13, 10:15 PM] +234 802 916 3341: ♦♦ *SANGARTATTCE* ♦♦

Maman Abd Shakur

23 - 24

*For Sell! idan baka biyaba dont F*ck*ng read it in Ayaan voice. Aha*

Hawaye ta share tabi wutsiyar hanun nata da kallo yanda yay ja abunku da farar fata ahankali tace "kuma ban yafeba mugu kawai" ta tashi da gudu tana kuka tai bakin titi batare data waigi su Walawa dake kiranta ba, ta tare Bus ta shige tana share kwalla ahaka har gida. Tana zuwa gida kofar gidan su tai turus tana kallon baban trailer company Uniform, suna sauke katipu irin na boarding school dinan ankawo ma almajirai kowa daidai, aiko sai tsalle suke suna murna wajen ya kacame da hayaniyan su, karasawa tai wajen Baba dake tsaye yay shiru yana kallon masu sauke katifar tace "Baba waya aiko da wayan nan katipun?" "mutanen dasuka zo jiya ne suka aikoma dalibai dashi, wai suna Allah kadai zai iya biyan mu amma ga wanan abama dalibai" shiru tayi tama rasa yanda zatayi tabama Baba kudin daya bata dan kunya takeji fada zai mata mesa ta karba hakan yasa ta wuce cikin gida tana satan kallon Isyaka dake rubutu a allo yana binta da kallo shima, murguda mai baki tayi tana nunamai allon ta shiga gida tana dariya, da sauri yabi allon da kallo yaga ashe afarar rigarshi yay rubutun baima saniba garin kallon ta muurmushi yay ya shafa gemunshi daya cika kaman wani babba sosai yacigaba da rubutun dayake yi. Tana shiga ta debo ruwa daga rijiya ta shiga tai wanka tadawo daure da zani, tana bubbuga kunenta dan ruwa ya shiga gajiya tayi da goge kunen kafin ta zauna gefen mama hanunta Mama tabi da kallo yanda yay ja tace "maiya sameki a hannu?" girgiza kai tayi tace "bakomi bugewa nai a school" kofin magani Mama tabata ta karba tasha sanan a ijiye tana yatsine baki, jakarta tadauko taciro bandir din kudin ta ijiye kusa da Mama tace "Mama mutumin nan najiya nahadu dashi a makarantar mu yabani wanan" kudin Mama tabi da kallo tace "aisai ki kaima Baban ki tunda kinada hannun amsa ni meruwa na" kaman zatai kuka tace "Mama dan Allah kibashi nidai tsoro nakeji, fada zemin wlh" tai kaman zatai kuka ta mike ta shige uwar daka dan saka kaya.

*******

Yau kwanan su biyu kenan da dawowa daga kano.

Mami dake kwance kan gadon Abba danyau ita keda girki ta kalli agogon bangon dakin taga karfe biyu har da rabi nadare kafin tasake kallon Alaji, tun wuraren goma Alaji ke kan dadduma sai salla yake yana addu'o'i data rasa name, kasa hakura tayi ta sakko itama ta shiga bayi ta dauro alwala tafito tadau hijabi ta bishi, bayan sun sallame ta dafa shi, juyo dakai yayi ya kalleta, murmushi tamai dake sanyaya mai rai tace "Alaji matsalar mekake dashi haka? Meke damunka tunda kadawo daga zaria naganka duk wani irin wats d matter talk to me, kasan state of health dinka bai kamata kanasa damuwa aranka ba" dan ajiyar zuciya tayi kafin ta maida kanta kan kafadar shi ahankali tace "meke damun mijina abin alfahari na haka?" murmushin dabai shirya yiba yasaki Firdausi daban ce, koyaya yake cikin damuwa kobai fadi mataba zata

gane, duk wani hanyar sanyaya mai rai tasani, murmushi yasakeyi kafin ahankali yace "akan dan mu nake addu'an nan" tabe baki Mami tayi hakan yasa ya girgiza mata kai yace "ba abinda kike tunani bane wlh" yadan gyara zama alamun serious yace "tunda naje zaria naga Bilkisu zancen ta ya tsayamin arai, duk sakan sai maganar ta yazomin rai, ina son Ayaan da yarinyar nan fiye da yanda kike tunani, yarinyar akwai natsuwa ga ilimi, ta sauke fa takuma kusa gama hada hadda inji baban ta, ga taimako, ayanda Boy yake yanzu mace mai irin natsuwar nan yakamata ya aura wlh hala ta sanadiyar ta ya gyaru yasan ya girma, inamai kwadayin auren ta sosai Firdausi" dan tagumi yayi Mami taja hannun ta saukar ya girgiza kai yace "yanzu dai istihara nai akan zancen auren nasu indai alkairi ni na tabbata Allah zai kara natsarmin da alamarin araina, to ni babbar matsalata yanda zan bijirowa da Boy al'amarin ne yanda aure baya gabanshi dinan zaima yarda" tabe baki Mami tayi tsabagen takaici kafin tace "hmm shikenan ai tunda hakane saikaita kallon shi kar yay aure tunda bakason ganin jikokin ka, kana dai ganin shi aure bayama gabanshi baiki yakare rayuwan shi ahaka daga yawo sai saka gantalallun kaya" ta tashi tahau gado danba karamin baci ranta yay ba yanda yadauko zancen da farko tiryan tiryan ba karamin murna yasata ba finally for d first time in long time, alaji zaiyi abinda ya dace shine kuma wai yana shakkan tunkarar shi da magana sabida gujin bacin ranshi.
[7/13, 10:15 PM] +234 802 916 3341: ♦♦ *SANGARTATTCE* ♦♦

Maman Abd Shakur

25 - 26

*idan baka biyaba karka kar karanta, for sell*

Kasa bacci Abba yay ranan gabaki daya danji yayi maganar takara natsun mai azuciya sai tunane tunane yake.

Bayan kwana biyu.
Wuraren 8 ya shigo falon Abban sanye da black trouser yau normal wando yasa saidai ya dame wandon, yasa white long sleeve shirt da kake iya hango chain din dake kyalli a wuyar shi yay tucking yakawo belt mai kyau yasa, yasa black cover shoe dake shining na zuwa aiki ya shigo dakin yana kokarin gyara tie din wuyarshi hanunshi daya kuma rike da white ironed lab coat dinshi sai kamshi yake looking cooperate, fatarshi har wani glowing yake sabida hutu, gashin kanshi da sajen shi sun kwanta lub lub, Abba ne kadai adakin zaune akan carpet ga abinci nan agabanshi anjera kala kala. "Morning Pops" ya gaida Abba da tunda ya shigo yake kallonshi, tsugunnawa yayi yadau cup din coffee dake gaban Abba sanin ba sugar aciki yasa yadau two cube of sugar yasaka yakoma kan kujera ya ijiye labcot din kafin yakoma gaban Tv rike da cup din coffee ya dauko remote yadawo ya zauna yana kokarin chanza channel daidai lokacin Mami ta shigo dakin da sallama rike da tray da blow din dake dauke da koko daketa kamshin su citta akai, ajiyewa tai agaban Abba dataga hankalin shi nakan Ayaan daya daura kafa daya kan daya yana kallon tashar kwallo, zama Mami tai gefenshi tace "ga kokon dakace na ma" dan juyowa

yay ya kalleta yay murmushi yace "nagode" sanan ya juya ya kalli Ayaan daya natsu yana kallon Ball yana sipping coffee, ahankali yace "Boy inaso muyi wata magana dakai" juyo dakai yay ya kalli mahaifin nashi yay murmushi dake karama fuskarshi kyau yace "okay Popsy" tashi Abba yay yakoma kan kujeran dayake zaune Mami dai ta tabe baki kawai tadau cup tana kokarin hadama kanta tea, Abba yadan dafa kafadar Ayaan dake kallonshi yace "Boy I've been thinking alot lately" Ayaan yay sipping coffee yace "yea I've noticed dat, wats d matter Pops" Abba yace "I've been thinking alot nai addu'a akai, nakuma samu natsuwa saisa nazo maka da zancen" ya danyi shiru yasake kallon Ayaan din daya natsu yana kallonshi yana kokarin kai cup din Coffee bakinshi, Abba yace "ina so ka auri yarinyar data taimake ka, wat i mean to say is inaso ka auri Bilkisu" wani irin mugun choking dinshi coffee dake bakinshi yayi hakan yasa yafara wani irin mugun tari, da sauri ya mike tsaye yana buga kirjinshi dayan hanunshi kuma akan bakinshi yana tari sosai yana kallon Abba daya kafeshi da ido, idonshi har ja yayi tsabagen kwarewan dayayi, da kyar tarin ya tsaya hakan yasa ya kalli Abba yace "Pops bakaine kai maganan dakayi yanzun nan bako? I refuse to believe u are d one" tashi shima Abba yakamo hanunshi ya zaunar dashi kan kujeran, kaman wawa ya zauna baki bude yana kallon fuskar mahaifin nashi, kwantar da murya Abba yayi irin yanda ake lallashin yara yace "akwai alkairi a auren ku, son ina maka kwadayin yarinyar she's way too good, saisa nakeso ka aure ta, i want you to marry Bilkisu" fizge hanunshi yay da karfi daga na Abba ya mike tsaye yace "wah! Pops, like, kaiii, for real?" yay maganan sounding so confuse shi mamaki ma maganan yabashi kodai Pops baida lpy ne, yasake kallon Abban yace "are you really saying dis, ni Popsy, ni fa, ni Ayaan na auri that gurl wats her name ma?" ya tsaya yana kokarin tuno sunan. "ehen Bilkisu, Popsy how old i am dama zanyi aure, and auren ma she!" yawani ja she din arrogantly yace "wanan yarinyar mara natsuwa mai rawan kai yar kauyen nan gata ma.." tsawan da Abba ya dakamai yasa ya tsaya galala yana kallonshi. "shut up Ayaan! One more bad word against that poor innocent girl wlh saina mareka, bazadai ka aure ta bako is fine with me, am not going to force u, but karka kara fadin any bad thing akanta" surprisingly yake kallon Abba da idanunshi dasukai ja tunda yake zai iya cewa tunda yay wayau Popsy bai tabamai ihu ko tsawa ba this is the first time and all akan dat lousy being Bilkisu, hakan ko ba karamin bakanta mai rai yayi ba yace "but Pops.." kofa Abba ya nunamai alamun yafita hakan yasa yasake kallon fuskar Abban yama kasa koda kwakkwaran motsi sabida mamaki, baki yabude zaiyi magana Abba ya dakamai tsawa da har Mami saida ta runtse ido sabida yanda ya shiga kunenta. "i said out" Abba ya nunamai kofa daukar labcoat dinshi yayi azuciye saikace dashi suke fada yafita daga dakin ranshi abace, da yan aiki yaci karo a falo yawani daka musu tsawa. "u all are fired out of this out right this minute" ya nuna musu kofa ganin yanayin fuskarshi yasa duk suka fiffita harda gudu yafita kaman zaki, Big Mummy da fitowar ta kenan tana kiranshi "Boy Boy" ko jinta baiyiba tsabagen bacin rai ya shiga mota, tsabagen yanda ranshi yabaci yasa yaja motar dawani irin gudu kaman mental sai hospital dinsu wanda na abokin Popsy ne yana aiki a wurin, duk uban nurses din dake gaisheshi ko amsasu bayayi, yawuce office dinshi wata receptionist ta biyoshi har office din bayan ya zauna ta gaida shi. "good morning sir, karfe goma ne zaku shiga theater din" wani irin kallo daya mata da idanunshi dasukai jajir yasa jikinta yafara rawa da kyar ya isa saita kanshi ya kalleta yace "the next senior doctor should do it, banajin dadi yau" jikinta har rawa yake tajuya ta fita tana memai fatan samun lpy.

Rasa inda zaisa kanshi sabida yanda ranshi ke tafarfasa yasa ya mike tsaye yafara zagaye

Sai bayan sallan la'asar dan lokacin hartai sallan la'asar har an chanza mata kaya wanan karan amtapa ne ajikin ta milk colour anmai kwalliyan black ajiki, wayyo Allah bakaramin kyau Bilkisu tayi ba tasa takalmin dazu baki da gyalen da jakan tana zaune cikin su Walawa daketa mata tsiya Baaba da wata kawarta sukazo gidan, gyalenta suka saka mata sukai mata lullube sanan suka kalli kawayen Baaba tace "kudan bamu aronta" suka fice tana biye dasu abaya har gidan Baaba da babu mutane saidai su Mama, Umma, da bakin dazu na kano datake iya hangosu ta huji hujin gyalen dake jikinta, sallama ababban falon Baaba taji Baaba tayi ta shiga da ita ta zaunar da ita kusa da mutum dabata san kowaye ba, saikuma taji Baaba ta cire gyalen daga kanta ta maida mata dashi kafada kafin tajuya tafita daga dakin, tasami su Mama dasu Mami da ita suke jira duk suka fita daga gidan dan komawa gidan su, kana ganin fuskar Mami kaga farin ciki lullube akan fuskarta, Baba dashi kadaine zaune adakin da Ayaan da aka ijiye Bilkisu kusa dashi dan su Abba basu dade da fita daga gidanba sunje dauko wasu abokan shi daya kira ya fadi musu zancen auren Ayaan, ajiyar zuciya Baba yayi yana tausayin yanda ma zai fadama yar tashi abinda Isyaka yayi hakanan dai ya tatataro jarumtar shi ya fuskanceta yakira sunanta "Bilkisu" dago kai tayi ta kalli Baban nata tace "na'am Baba" yace "inaso ki zama jaruma mai karban kaddara aduk yanda tazo mata, karki sa komi aranka ki dauka komi yafaru ne ayanda Allah yakeso, ahaka Allah ya tsara tun kafin ma a hallice mu" yadanyi shiru kafin ya nisa yace "yau awurin daurin aure Isyaka ya tashi agaban kowa" saikuma yay shiru kafin yay murmushi me ciwo yace "yace yafasa auren ki baya sonki yajuya yama fita daga masallacin abinshi" tunda yafara maganan ta dago kai take kallon mahaifin nata badadan shi bane ke gayamata maganan nanba da wlh zata iya cewa karyane Isyakan ta bazai taba yimata hakaba, yace "bazai aure kiba, shine dama mahaifin Ayaan yataba zuba nemama danshi auren ki lokacin ankusa bikin ki da Isyaka, shine yau bayan abin yafaru Ayaan yace shi abashi yana sonki shine nasa aka daura auren ki da Ayaan ga sadakin ki nan" ya daura mata kudin ajiki, kaman ma bata duniyar nan haka takejin ta Isyaka yace bazai aureta ba, andaura mata aure da Ayaan din dabama tasan wayeshi ba, dan bilhakki takara manta wani Ayaan, Isyaka na ne yace "bazai aureni ba?" da sauri ta kalli Baba da rinannun idanunta dasuka cicciko da hawaye dan shima ita yake kallo tace "Baba Isyaku nane yace bazai aureni ba? Menamai Baba, wlh banmai komiba dan Allah kace yayakuri Baba" tafashe da kuka sosai kaman zata mutu, Baba ya girgiza mata kai yace "i shiru ki manta da zancen isyaka danke matar wani ce yanzu, nasan ban kyauta miki ba dan banji ta bakinki ba, amma a matsayina na uba zan iya zaba miki miji nagari daga ganin Ayaan

yaron ne dan gidan arziki, ga mahaifin shi da kirki da daraja musulmai, nariga na musu bayanin jarabawan da zaki zana sun amince daki zauna agida bayan gama jarabawan saiki tare, yanzu dai bari na barku tare kudan tattauna ni natafi wajen su mahaifin ka" yay maganan yana kallon Ayaan da kanshi ke kasa tun dazu, dago kai yayi ya kakalo murmushi yace "to Abba" Baba yafita yana kallon Bilkisu dake wani irin kuka dake tabamai zuciya gidan yarage daga shi sai ita.

Baba nafita tamike tsaye zata fita dan bama tason ganin koma waye mijin da Abba yace yamata, hanyar fita daga dakin tayi cikin kuka fuuu taji an wani irin fincikota danhar saida gyalenta yafadi kasa saura kiris tafada kanshi amma ganin wanda take shirin fadawa jikinshi yasa ta dage ta tare kanta tafadi agabanshi tana kuka, wanan mugun Baba ya aura mata dama, wutsiyar hanunta daya kama tabi da kallo, hawaye masu dumi suka zubomata tafara kokarin fizge hanun nata amma yaki sakinta saima wani irin matsiyacin kallo dayay yace "Ke! bazaki natsu ba" ko kallon shi bataiba saima daddagewa data keyi zata fizge hannun, hannun yabi da kallo ba karamin kyau lallen yayiba barinma yatsunan ta da dogayen kumbunan ta da aka zagaye su da ja, yasake mata wani irin kallon yadanyi murmushin gefen baki yace "bakiji dadi bama na taimaka miki? Wanan kazamin yaron yace baya sonki shine nace ni bari indan rufamiki asiri sabida tausayin mahaifin ki danaga hawan jini yana neman kamashi za'ai abun kunya, shine na taimaki rayuwan ki inda bahaka ba mezanyi dake jibeki fa dan Allah" wani irin bakin ciki da maganganun shi yasa taji yasa ta daddage taja wata shegiyar tsaki. "mtswwww" fizgota yay wanan karan saida tafado a kirjinshi, gabaki daya hanunta daya rike yamaida shi ta baya ya lankwasa hakan yasa tai wani irin ihu. "wayyo Allah Mama zai kasheni" tafashe da kuka mara sauti jikinta ko ina rawa yake, dan lumshe ido yayi jin yanda numfashin ta na kuka ke sauka akan fuskarshi kafin ya budesu ya sauke akan hawayen dakebin kuncinta ba kakkautawa ya daure fuska tamau tareda sake matse hannun tabaya ihu tayi sosai har saida ta bankare ta daura dayan hanunta akan kafadarshi duk cikin azaba, hanun yabi dawani irin kallo da sauri ta janye tana kuka sosai tana yarfe hannun harda shesheka, sakinta yayi tareda tureta harsaida ta fadi akasan wajen ta tashi ta zauna da sauri ta kamo hanun daya kama tana kallon yanda yay ja takara fashewa da kuka tana hurama hanun iskan bakinta dan zafi yake mata, tsaki yay yafita daga dakin, akofar gidan yaga su Abba da abokanen shi dasuka zo tareda Malam ya gaidasu sanan yaja Abban shi gefe kaman zaiyi kuka yace "Pops am going to the hotel nidai nagaji wlh i need to sleep" da sauri Pops yataba kanshi yace "shikenan Mah Boy jeka huta muma dasu maman ka Anjima bayan Isha zamu dawo hotel din, gobe da safe zamu dawo akara gaishe gaishe da sanin juna kafin mu wuce kano ko" gyada kai kawai yayi yawuce ya shiga mota yaja yabar wajen.
[7/15, 12:21 PM] Ummi Tandama: ♦♦ *SANGARTATTCE* ♦♦

Maman Abd Shakur

31 - 32

Anan falon Baaba taci kukan ta ta koshi, ji take kaman tahadi yi zuciya ta mutu maisa Baba yamata haka tunda Isyaka yace bayayi basai abarta ba anwani hadata da wanan basamuden

mugun, ahaka bacci yay awon gaba da ita a wurin.
Hayaniyan dataji yatada ita daga baccin daya dauketa Baaba tagani zaune da wasu bakin gidansu dasuka zo daga kauye anata hiran rabon kudin da Abba yay tayi, fashewa tai da kuka hakan yasa suka lura ma tatashi Baaba tace "hakuri zakiyi ai Isyaku duniya ce tanada girma yama kanshi, ki yakuri ba gashi Allah ya musanya miki ba mai sonki wanda kika taimaka, ni wlh inxakiji ta tawama kinfi dacewa dashi, tashi kije kiyo salla kici abincin ki karfe sha biyu fa" tashi tayi ta karbi toculan da Baaba ke mikamata ta karba tafita daga dakin ta wuce yo alwala.

Misalin karfe takwas na safe tafito daga wanka daure da zani a kirji Baaba dake zaune gaban murhu ta bita da kallo yanda take uban sheki, murmushi tayi tajuya tacigaba da dama kokon datake yi, daki ta shiga ta shafa mai ta shirya cikin doguwar rigan kampala shaddan purple da fari da Baaba ta iniye mata aiko yay mata shegen kyau tana cikin fama da daurin dankwalin dan takasa sabida dan kwalin yay kaba kaba Baaba ta shigo tace "ke imaza yapa gyalen tunda kin kasa daurin kije Baban ki ya aiko Muji ya kiraki iyayen mijin ki suna hanya zakuyi sallama su tafi, mike" Baaba ta dagata ganin bamata da niyyar tashi tadau gyalen ta yafa mata tace "imaza tafi nima ganinan zuwa" fita tayi daga gidan jikinta duk asake har gidan su da babu wasu mutane sosai dan yan uwan su kadanne suka rage dakinsu tayi tana shiga uwar daka tafada kan Maman su tafashe da kuka sosai dagota Mama tayi ta share mata hawayen dasuke zubowa tace "kiyakuri Baby, nasan yanda kikeji, haka Allah ya kaddara zai faru dama chan Isyaka ba mijin ki bane, bahakanan Allah ke hadaka da wani arayuwa ba rana daya ba, kin hadu da Ayaan ta dalili ne, asheko shine wanan mijinki, ki yakuri kinji anriga andaura babu yanda zakiyi" cikin kuka tabude baki zatai magana Mama ta girgiza mata kai tace "banison ji" sallaman da akayi yasa Mama ta amsa ta fita ganin Mami ce itakadai dan sauran duk sun shiga falon Baba yasa Mama tai murmushi tace "barka da zuwa kun iso, shigo" shigowa Mami tai tasami waje ta zauna tace "ina kwana ya gajiyan bik" Mama tace "Ipy lau ya taku gajiyar" murmushi Mami tayi tace "Alhamdulillah ina yar tawa?" murmushi sosai Mama tayi tace "tana ciki bari nakira miki ita" da sauri Mami tace "a'a kibarshi dan Allah ni nashiga?" a kunyace Mama tace "kai dan Allah keda yarki kike wani tambayana, ni kinga ma tafiyata bari naje agaggaisa" Mama tadau hijabi ta fice zuwa dakin Baba, Mami ta daga labulen da sallama ta shiga dakin, a kunyace ta mike tsaye dan taji Mama na magana bama ta tsaya ta saurara ba sabida kukan ta take, tsugunnawa tayi tanadan murmushi ahankali tace "ina kwana Mumy" hannu Mami tasa ta dagota sama kafin ta sumbaci gaban goshin ta, lumshe ido tai a kunyace dan bata sababa, Mami ta zauna da ita akan gado kafin ta zauna agefenta tana murmushi tace "Allah miki albarka Bilkisu kiyakuri kinji, Ayaan zai kula dake karkija komi zamu rikeki amana" jakar hannunta ta bude ta ciro wata sabuwar Samsung ta mika mata kin karba tayi saima kara sunnar da kanta kasa datayi tana wasa da bakin gyalenta, ajiye mata wayar Mami tai agefe tace "ga wayar kinan nasamiki number na aciki, zan dinga kiranki, kiyi karatun jarabawa da kyau kinji Allah yabada sa'a" ahankali tace "nagode Mumy" shafa kuncinta Mami tayi kafin ta tashi tafita daga dakin itama ta shiga falon Baba anata magana.
Fadawa tayi kan gado tafashe da kuka sosai tarasa inda zatasaka ranta taji dadi, zumbur tamike kaman an tsikareta tafito daga dakin Maman ahankali tai hanyar zaure tana tafiya sadaf sadaf tana bude kofa tafita zaure saida tadan labe abayan kofa kafin tadan leka kofar gidan kosu Baba nanan awaje ganin babu kowa sai kusan motoci uku dake fake akofar gidan nasu

akukkule yasa tai wuf tafito, tana waige waige ganin lallai ba kowa dan ko almajiri daya babu yasa ta gyara gyalen kanta tareda tattare doguwar rigar dan tadan mata tsawo ta arce a guje. Ayaan da tunda take leke leken ta daga bayan kofa yake kallon ta dan yana cikin mota ya kunna AC yana sha, gajiya yay da surutan su yay fitowar shi waje, dayake glass din motar tinted ne saisa bata lura dashi ba, gyara zama yay ya kalli madubin window motar yanda take tafiya gudu gudu, sauri sauri ya kafeta da ido tareda hade hannayen shi biyu ya dunkule yakai karamar yatsan shi daya yadaura akan lips dinshi kaman mai tunani, ganin tasha layin tai kwana yasa ya kunna motar yaja yabita.

Babban wuri ne haka da akamai runfa sabida asamu inuwa, mutane ne zazzaune daketa aikin hannu, wasu na sakan hula wasu kuma na aikin wuyar shadda, da sauri da sauri take karasawa wajen fatanta Allah yasa ta ganshi anan dan tasan baida wajen zuwa sai nan, anan duka abokan shi suke, tsayawa awurin tayi tana kalle kalle ganin bashi awurin kaman ance ta daga kai ta hangoshi kan bencin dake gaban wani shagon dake gefen wajen, ga yar jaka agabanshi yanata diban kayanshi dake gefenshi akan bencin yana jerasu acikin jakar, da gudu tai wurin tana share hawayen dataji yafara kwararowa, kaman daga sama yaji ance "mena maka kafasa aure na?" dago kai yayi asanyaye ya kalleta gani tayi idanunshi sunyi jajir suma harma sun kumbura, kasa daurewa tayi tafashe da kuka sosai tasa gyalenta tana sharewa bata ma damu da mutanen dake shiga shagon siyan abu bama cikin kuka tace "maiya sameka idanunka sukai haka? Mena maka? Maiya sa kace kafasa aure ne kasan illar da hakan yamun kuwa? Inda kasan baka sona maiya sa tuntuni baka fadaba sai a wurin daurin aure? Maisa kamin haka eh?" baki yabude zaiyi magana saikuma yafasa yay shiru taga ya kurama bayanta ido, da sauri ta juya dan taga maiyake kallo Ayaan ne acikin mota yay wining glass down idanunshi sanye cikin bakin glasses, daure fuska yay tamau ya kalleta babu alamun wasa atattare dashi yace "get in" kaman bada ita yake ba ta juya ta kalli Isyaka daya cigaba da hada kaya abinshi kaman bashi a wurin tace "kasan yanda nake sonka kuwa shine ka cutar dani haka ko, maiya sa kamin abinda kami..." tsawan dataji yasa takasa karashe maganan datake yi. "are u deaf nace kishiga mota mutafi" yay maganan har lokacin yana zaune cikin mota afirgice ta juyo tafashe da kuka sosai batare data shiga motar ba mutane sai kallon su suke, bude kofar yayi yafito yana wani irin taku da duk taku daya saitaji har a kokon ranta, da sauri ta runtse ido sabida wani irin mugun tsoron dataji yana shigan ta, hanunta dataji ya fizga kaman zai katsa yasa ta bude ido janta yayi ya bude mota ya wurgarta ciki kafin ya koma ta dayan side din yanama Isyaka dasuka hada ido wani irin kallo, da sauri Isyaka yadau jakar ya juyama motar baya kirjinshi na bugawa, wani irin dan iskan murmushi yayi kafin ya bude motar ya shiga ya bata wuta, kuka take kaman ranta zai fita kanta nakan cinya.

Bai tsaya ko inaba sai gidan dam, wurin babu kowa gashi very peaceful sai iskan bishiyoyin daketa kadawa da kukan tsintsaye dake wucewa, zagayawa yay ya bude side din datake har lokacin kanta nakan cinyanta kuka take sosai cikin kakkausar murya yace "fito" ko dago kai batayi ba balle yasa ran zata fito, hakan yasa ya jawota da karfi luuu ta taho zata fada kanshi dan ko karfi daya bataji dan rabonta da abinci tun jiya ya matsa gefe da sauri hakan yasa ta zube akasa, wani wahalanlen  kuka tasaki ahankali tana share guwiwar hannunta daya bugu da kasa, ya dawo ta gabanta yay wani irin tsugunnawa daya karamai kyau yana karkada key motar

dake hanunshi yana mata wani irin kallo yace "baki da natsuwa ko, bakisan kinada aure ba zakije kina ma wanchan dan kauyen magana" turo baki tai cikin kunci tace "Isyaka na niba dan kauye bane karka sake cemai dan kauye" takarashe maganan tana wani lankawasa wuya gawasu sababbin hawaye dasuka zubo mata tsabagen takaici, dagota yay da karfi ya jingineta jikin mota ya kafeta da ido da sauri ta kawad dakai tareda sa bayan hannu tana goge kwallan yace "ke ki natsu fa banason raini ko kadan wlh, auren taimako nayi, na taimake ki da mahaifin ki danaga hawan jini na neman kamashi da almajirin chan yace yafasa auren ki" murguda mai baki tayi dan wlh yakaita bango tace "eh almajirin ne aidai Allah ya halicce shi, kuma ahaka nakeson abuna har yanz..." bakinta daya kaima duka da karfi yasa tai shiru ta fashe da kuka, hanunta ya kama yakai baya ya murde hakan yasa ta bankare tana ihu. "wayyo Allah na Mama zai ciremin hannu" hadata yay da mota ya matseta danhar jikinsu na gogan juna ya kalli kwayar idonta yace "wlh idan kika sakemin rashin kunya sai namiki abinda zaki dinga kuka tunda ga yau har ranan daza'a kawoki gidana".....
[7/17, 11:57 AM] +234 814 359 8303: ♦♦ *SANGARTATTCE* ♦♦

Maman Abd Shakur

33 - 34

Ya ja hanunta ya bude side dinta ya wurgata ciki kafin ya koma mazaunin driver ya shiga ya yatada motar yabar wajen, duk tacika mai mota da kuka abakin layin su yay niyar sauketa hango su Abba da Malam awaje yasa yawani dakamata tsawa. "ke!" atsorace ta dago kai ta kallai hannu ya daura akan lips dinshi alamun tai shiru hakan yasa ko tai shiru har yakarasa kofar gidansu, aiko su Abba sukabi motar da kallo parking yay yafito da sauri ya zagayo ta inda take ya bude mata daidai nan su Walawa dasuka zo wurinta suka fito daga gidansu, murmushi both Abba da Baba harda Baba Sulaiman duk sukayi hankalin su yakara kwanciya ganin Ayaan da Bilkisu tare. Fitowa tayi daidai lokacin su Walawa sun iso sai kallonshi suke atare suka gaidashi "ango ina yini, ina kukaje kaida Amaryan tun dazu mukaxo fa" murmushin dole ya kakalo ganin su Abba a wajen itakuma wucewa tai cikin gida abinta, su Walawa sai uban surutu suke mai yana yake daga baya sukamai sallama rapper kudi yaciro yabasu suka karba sukamai godiya kafin su koma cikin gidan.
Sai bayan azahar suka tafi bayan sun cika gidan da kayan abinci da kudi duk yanda malam yaso yaki karba kin yarda Abba yayi yace ai yanzu anzama daya kafin su wuce kano kowanensu rai fess.

**************
Tun tanama su Umma, Mama da Baaba kuku asaurareta ana lallabata har yazo kowa yafita harkan ta to uban ma me zasu iya aure dai anriga an daura saidai kuma abisu da fatan alheri, ganin babu mai sauraron ta danhar su Walawa sunfison Ayaan sunce mezatayi da Isyaka daya wulakan tata ranan daurin aure yace bayaso, tama godema Allah yaro dan gayu yace yanayi, hakadai ta tattara ta manta da alamarin tacigaba da zuwa school abinta ta dage da karatun exam, Mami na yawan kiranta ganin haka yasa duk Friday saita turama Mami Friday message

mai dadi da ma'an hakan ko ba karamin faranta ran Mami yakeba.
Cikin iko na ubangiji ta fara zana jarabawan ta abinta sosai ta dage tana karatu ta manta zance wani Ayaan da Isyaka, inbama su Walawa sun kirata da matar Ayaan ba wanda yanzu shine sunanta har mantawa ma take ita matan aure ce, kumama wai Matar dan iskan nan maisa sarka da dan kunne hmm.

Zaune yake akan daya daga cikin kujerun platinum table dake cikin club din wanda aka jerasu mussam sabida mayan, non alcoholic wine mai sanyi waiter ya zubamai a glass cup kasancewar sunsan shi bayashan alcohol, gefenshi wasu maza ne hadaddu guda biyu wanda suke friends dinshi tare sukai school, daya daga cikin sune mai suna Fawaz yace "wai kai bazaka je ka dubo matar kaba yanzu more than a month kenan da bikin ku da baka gayyace muba" jan tsaki yayi tareda kara relaxing ajikin kujeran dayake kai yanabin wankan dake tashi a club din na Drake, dariya su biyun sukayi banda shi daya wani lumshe ido dayan ne mai suna Paul yace "yo wai tayaya ma wanda zai aureta kace yafasa awurin daurin auren, mekayi Ayaan? I know u have something to do with him saying bazai aureta ba" sai a lokacin yadan yi murmushi kadan kafin yawani tabe baki yana girgiza kai yace "nothing much, I just threaten d poor guy, bayan nasa an kamomin shi na kusan harbinshi da bindiga ya tsorata harda kuka fa wai bayason ya mutu yanzu he's just 25, yadan ban taudayi so saikuma na cikamai aljihu shikenan" dariya sukahau yi dukan su Fawaz yace "shege mugun iche, ashedai kana son yarinyar" da sauri ya kallesu kafin ya murtuke fuska yace "guys banson iskanci, ni" yanuna kanshi yace "ni, ni, me fa, inso yarinyar nan wanan yar kauyen? God forbid, Allah ya kyauta, she is not my type infact tamamin kadan as my woman, i did wat i did for Pops, u know he's old yo, so banison abinda zaisa yay breaking down, i gats make d old man happy now" atare samarin suka gyada kai suna "yeah hakane, we gats make our Pops happy kam" drinks dukansu sukai sipping atare Fawaz ya kalleshi yace "wat about ur Meram?" kallonshi yadanyi kafin ya maida mai da tambayar. "wat about her?" Fawaz yay yar dariya yace "i mean baka sonta bazaka aureta ba ita? Me relationship din dake tsakanin ku dont u have feelings for her" tabe baki yay yace "Gee, get this straight nifa aure ko soyayya bayama ajenda na, infact inda baku tunamin da dat low life girl da Pops yahadani da itaba ninama manta inada wata so called wife, and Meram, Meram" yakira sunan sau biyu yanadan rolling eyes dinshi saikuma ya tabe baki yace "ina more rayuwana da ita ne kawai anytime am in d mood, babu komi tsakanina da ita, she's just a girl dat love giving her self to me okay" dariya duka sukayi Fawaz yaciro wayarshi yace "lemme call my babe nima" tabe baki yayi kafin ya mike yaje dance floor yafara rawa abinshi yana sipping wine din glass cup din hanunshi.

Sai gurin sha biyu suka fito daga club din kowa yaja motar shi dan zuwa gida. Abangaren shi yay parking yafito yana kwance belt din wandon shi ya bude kofa ya shiga daki, zaune yaga Abba a kujera ga dukkan alamu shiyake jira, dan sosa kai yayi yamaido kofan ya rufo yazo kusa da Abban daya kafeshi da ido dan murmushi yayi yace "Pops bakayi bacci ba" yay maganan yana zama tareda daura kanshi akan kafadar Abba, sosai yay niyar mai masifa amma saiya sassauta murya cikin lallashi yace "Boy lokaci yayi da u will stop clubbing, da nabarka ne sabida inama kallon yaro but yanzu ai ka girma tunda ma har ka ijiye mata, ehen talking of mata wat do you mean ne eh? More than a month yanzu bakasan kaje ka duba matar kaba, ina so gobe

goben nan ka shirya kaje" daure fuska yay tamau kaman zai fashe yace "zanje hospital gobe akwai aikin da zanma wata" "karya kake" Abba yatari maganar shi afadace ya nunashi da yatsa yace "wlh inhar baka tattara komi ka ijiye gefe ka wuce kadubo matar ka gobe ba saina saba maka" ya kamo kunnenshi tareda daye dankunen diamond din daya makala da gum kara yayi. "Pops zafiiii" ya dafe kunen kaman zaiyi kuka Abba ya cillar da dankunen yace "wlh karna kara ganin ka dasu, wanan shegiyar sarkar ma kacire, kai ai ba mace bane" turo baki yay yace "sarkan ma ai bana mata bane, baka gani bane Pops namaza ne fa" "I've said my own, first thing tommorow morning kabar gidan nan kawuce kaje ka dubo matar ka, hakkin ta na kanka be careful" Abba ya wuce yafita yana masifa.

Da gudu take tafiya danyau ko tsayawa karban waina batayi ba daga wurin Baaba, yaune take rubuta last paper ta Civic education kuma karfe biyu ranane paper bacci tayi babu wanda ya tasheta dan Mama da Umma sunje barka, biyu saura minti goma ta tashi hakan yasa ta zabura tasaka kayan makaranta tafito tana kaiwa bakin titi tasami Bus ta shiga, abinka da bus sauke dauka ba ita takai makaranta ba wuraren karfe biyu da rabi, sunayen Allah kawai take kira ta shiga makarantar da gudu tai exam hall atsorace takai bakin class din ta tsaya yan aji sai kallonta suke su Walawa dake rubutu suna mata alamu data shigo, kallon fuskar invigilator tayi ganin baice karta shigo ba saima wani kallon wulakanci dayake mata irin na kinyi latti kinkuma tsaya awaje dinan yasa ta kwasa da mugun sauri tai cikin hall din, tsayawa tasake yi dan tsoron zuwa ta karbi booklet da question paper take ganin ya mikomata daga inda yake zaune yasa tai inda yake da saurin ta, zuiiii tai wani irin mugun faduwa sakamakon bawan ayabar dake kasa data taka wani irin mugun ihu tayi dan saida ajin duka ya dauka sakamakon faduwa datayi gabaki daya ta saitin ciwonta, dan ciwonne ma yafara buga kasa kafin sauran ilahirin jikinta, da sauri shi kanshi invigilator ya sauko daga kan kujera su Walawa ma haka duk aka zagaye ta, Walawa tasamu ta damke da karfin bala'i cikin kuka tace "Walawa na bige ciwona uhm uhm uhm" wani irin nishi take tana kuka sosai tama kasa magana, invigilator yace "ku kira principal dinku" da gudu yan ajin aka fita aka kira principal koda tazo tuni Bilkisu tafice hayyacin ta sabida azaba kuka kawai take da ihu, Keke napep principal tasa aka kira ta dubi dabilan ajin tace "wayasan gidansu?" su Walawa ne suka daga hannu hakan yasa principal din tace "kuzo ku maidata gida wurin iyayenta ku dawo yanzun nan sabida kuyi jarabawar ku" kokarin mikar da ita ake ta kankame Walawa tana ihu "dan Allah dan Allah nace wlh inna tashi fashewa cikin nan zaiyi" tana maganan tana kukkule ido kaman mai shirin suma, principal tace sudauketa, taruwa sukayi suka dauketa suka saka a Keke Walawa da Aisha shehu suka bita sai gida.
[7/17, 12:04 PM] +234 814 359 8303: ♦♦ *SANGARTATTCE* ♦♦

Maman Abd Shakur

35 - 36

Yafi minti biyar da parking a kofar gidan nasu amma yaki fitowa saima kallon kofar gidan yake

daba kowa dan duk almajiran sun tafi bara, yana sanye da dark blue shadda da akamai aikin hannu mai shrgen kyau, jumper ne rigar danshi ya tsani tazarce, kanshi ba hula saidai gashin shi dayay lub lub dashi sai uban kamshi yake, tsaki yakara ja ya dunkule hannu ya daki iska "f*ck! hanayinyar dayaji yasa yadan dago kai, yan mata biyu yagani da fararen hijabi da purple dankwali da purple wando alamun yan makaranta ne sun tsaya gaban keke suna mika hannu suna magana alamun da wani akeken dasuke ma magana, daya daga cikin su yaga ta juya ta shiga gidan su da sauri chan sai gashi tafito da Baba yasa babban kaya kanshi da rawani irin ta malamai, magana yaga Baba natayi baya iyaji sabida glass din motar arufe suke fararen hannu yaga an miko daga keken wanda kumbunan hannun ke zagaye dajan lalli dayay jajir, hannun Baba ya kama, ya kara daya ta bayan wuyan shi da kyar ta sakko da kafa daya kasa saikuma ta kece dawani irin kuka da shida kanshi saida yaji daga motar, kamota Baba yayi hakan yasa tafado jikinshi tama kasa mikewa da kyau tana neman yin kasa tana wani irin kuka da sauri su Walawa suka taya Baba riketa dukansu, hankali tashe Baba ya rikota da taimakon su sukai cikin gida tana mugun kuka, dan tabe baki yayi kafin yace "wats wrong with her?"

Shimfideta Baba yayi akan tabarman dake dakinshi sabida tsakar gida yajiku dan dazu anyi yayyafi, Baaba dasu Umma suka zagayeta dan bama su dade da dawowa daga barka ba, ganin yanda take ihu tana kuka yasa Malam ya tsugunna ya daga hijabin tareda rigar ya janye farar shimin datasa ya kalli ciwon bugewan datayi yasa wurin yay ja sosai abunku dafara, mikewa tsaye yay yakalli Mama yace "cire mata kayan nan iska yadan shigeta kotaji dadi, bari naje na nemo taxi abakin hanya saimu kaita asibiti" to Mama tace jiki asanyaye ta tsugunna tana kokarin maida hawayen dataji yana kokarin zubomata, cire hijabin da rigar tayi ta barta da farar shimin kadai sai kuma wandon makaranta jikinta zata mike ta cafko hanunta tana kuka tace "ina zaki Mama? Dan Allah ki rikeni, Umma, Baba" takirasu duk awahale, dan uban kukan datake yasa ta galabaita, zuwa wajen Umma tayi ta rike, Baaba kuma dasu Raiyana duk suka tsaya akanta suna mata addu'a.

Bude mota yay yafito sabida hango Malam dayayi yana shirin fitowa daga gida adan kunyace ya dukar dakai ganin Baba na kallonshi dudda hankalinshi atashe yake hakan bai boye farin cikin ganinshi dayayi ba, ahankali yace "ina yini Abba" murmushi Baba yayi yace "barka dazuwa saukan yaushe? Yasu Alaji da kowa da kowa" ahankali yace "Alhamdulilllah sunce agaishe ku" girgiza kai Baba yayi yace "kaga ikon Allah yanzu hakafa fita zanyi nem mota ahanya, dan matar takace ba lapiya yanzun nan daga wajen jarabawan tasu ce aka kawota ma, cha nayi nasamo sai muzo akaita asibiti amma tunda kaga Allah yakawo ka ai sai kadubata" dan murmushi yayi yace "meke damunta Abba?" ajiyar zuciya Baba yadan yi yace "wanan dai matsalar cikin dana fada muku tanada shi, wai bawon ayaba ta taka a makaranta shine fa tafadi, mu shiga ciki ka dubata" gaba Baba yayi yana biye dashi a tsakar gida har dakin nashi, aiko tundaga zaure yakejin ihun nata tsaki yadanja wanda shi kadai zai iya jin karanta. Sallama Baba yayi ya shiga dakin daidai lokacin ta kara kankame hannun su Mama kaman zata shide tace "Mama Mama wlh zafin yakaru kaman wurin zai farke" dan leko dakai yayi tabayan Baba ya kalleta kitson shiku ne akanta manya da kanana idan akai babba daga sai ayi karami siriri guda daya, tsawon shikun har bayanta yakai jelar nata lilo sabida yanda take jujjuya kai, dan

makalen dan kunnene akunnenta ja, ya gangaro xuwa jikinta dake cikin farin shimi dayabi jikinta gabaki daya saikuma purple wandon da farar safan makarantar dake kafarta, gashin gaban kanta sunbi zufan datakeyi sun kwanta lub lub idanunta sunyi jajir danhar kumbura sunyi tsabagen kuka, yanda ta kakkame su Mama tarike su kace a nakuda take, ganinshi yasa su Mama duk suka mike tsaye a kunyace siriki yazo, dukar dakai yay ya gidansu suka amsa sunamai barka da zuwa kafin duk su fita dakin su ka barta akan tabarman tana uban kuka, karasawa inda take Baba yayi ya kalli Ayaan da har lokacin yake tsaye a inda yake kai akasa yace "karaso ka dubata Ayaan" kara fashewa tai dawani sabon kuka jin sunan da Baba yakira, ahankali ya tako yazo gefen Baba ya tsaya akaro nabiyu ya daga kai ya kalleta aiko suka hada ido da sauri ya dauke kai, Baba yace "dubata ina zuwa" fashewa tayi da kuka sosai ta damke babbar rigan Baba tana kuka tace "Baba ni bazai dubani ba nidai ka kaini asibiti Baba zafi yakeminin sosai wlh" karban babbban rigan shi Baba yayi yace "kagamin shirme keda baki da lpy kuma kice likita bazai dubaki ba" ya kalli Ayaan yace "karka biye mata dan Allah rakinta yawa ne dashi wlh, yarinya ba dauriya ko kadan" Baba yay ficewar shi yana korafin halinta.
Ihu tayi da saida ya daura hanunshi akunne. "wayyo Allah na Baba dan Allah kadawo, cikina Baba, mutuwa zanyi, wayyo Allah na na banu na" kukan ta taciagaba dayi tana jujjuga kai ta daddaga hannayen ta sama tana yayyarfe su tsabagen raki, ahankali ya daga kai ya kafe cikinta da ido dake a shafe ta shimi, ta gefen haggunne yaga shimin yadanyi tudu, dan matsawa yay kusa da ita fuska adaure, duk uban kukan datake da zafin da cikin ke mata bai hanata tattaro ragowan karfin daya ragemata ba ta matsa baya da sauri cikin kuka tace "mehaka malam" wani irin wulakantattcen kallo yamata batare daya daga murya ba gudun kar ajisu yace "ke banason rashin hankali" yakara matsawa kusa da ita matsawa tayi da sauri sai kuma tafasa uban ihun dayasa ya bugi bakin ta  yace "wlh kika karamin irin ihun nan saina fasa miki baki" yana fadin haka yasa hannu akan shimin jikinta yana wani irin tabe fuska ya yaye shimin zuwa sama hakan ya bayyanar da shafefen cikin ta fari, wajen ciwon ya dade yana kallo yanda wurin ya kumbura yay ja kafin ya kalli fuskarta yanda take hawayen ba kakkautawa ga uban zufan da goshin ta keyi sabida wahala, ahankali ya mika hannu zai taba wurin da sauri ta rike hanunshi tafashe dawani irin kuka tana kokarin tashi zaune amma takasa ta kalleshi da rinannun idanunta tareda kara cukwuikuye hanunshi cikin nata tace "dan Allah, dan Allah, karka taba wlh zafi yakeyi inka taba mutuwa zanyi dan Allah" hanunshi yabi da kallo hakan yasa ta sakeshi atsorace tana kuka, yabi hanun da kallo yanda zufan hanunta ya jikamai hannu kaman yasa hannun aruwa, dan ajiyar zuciya ya sauke kafin ya sanya dayar hanun nashi a aljihu yaciro handky ya goge zufan sanan yakara maida hanun zai taba wurin cikin kuka sosai tafara kokarin tare hanunshi kama hannayen nata yayi da hannu daya fuska adaure kafin yakai hannunshi ahankali ya daura akan wurin, ihu tayi cikin kuka kirjinta na bugawa sosai, shiru yadanyi kaman mai nazarin abu kafin ya gangaro da hanunshi kasan ciwon kadan ya danne da karfi, wani irin ihu tayi da saida ta zaburo ta dago kanta ta daura akan fuskarshi dan yadan rankwafo sabida akwance take, tsabagen azafa yasa tafara jujjuya fuskarta akanshi gabaki daya zuban datai agoshi da hawayen ta sharemai su tass a fuskarshi tana kuka, cire hannun yay ya tureta da karfi takoma ta kwanta tana kuka yace "wat d heck! Are u mad" tsaki yayi yamike tsaye yadau handky yana share fuskarshi dashi, sanan yafita daga dakin rai abace. Ganin su Baba a tsakar gidan yasa yadan kakalo murmushi, Baba yace "mecece matsala Ayaan?" dan dukar dakai yayi sabida kunyar Abba dayakeji ahankali yace "Abba tun yaushe take ciwon nan?" karaf Baaba ta

chabe tace "yafi shekara biyu fa tafara har yazo yafara girma kullum inyafara saidai ai addu'a abata" ahankali ya gyada kai yanadan tunani saikuma ya kalli Abba yace "ina ganin Appendix ne, yay girma har ya rika haka, yanzu inaso zan tafi da ita asibitin danake aiki a kano zamuje ai yan gwaje gwaje inhar shine to dole operation za'a mata acire tahuta" salati su Mama keyi kaman wani baban abu, shi abin ma yaso bashi dariya yadan daure Baba ne ya nisa yace "shikenan Ayaanu ai matar kace duk yanda kace hakan za'ayi Allah dai ya bata lpy, yasa kuma muji alheri" Ameen duk sukace yadan kalli Mama yace "wazai bimu dan dole wani yabimu dazai riketa amota ni ina tuki" Mama da Umma shiru sukayi ina zasu wani iya zuwa gidan surukai hakan yasa Baaba tace "muje nabiku, bari naje nahado kayana" takalli Mama tace "hada mata nata itama" da sauri yace "a'a tanada kayanta achan" murmushi kowa yayi, Baba yace "muje waje sa fito da ita insun shirya" bin Baba yayi sukai waje, nan da nan Baaba taje tahado kayanta karban jakan yayi yasaka mata a boot itakuma ta shige gida, ba'a jimaba suka fito dauke da Bilkisu da aka chanxa mata kasa zuwa doguwar rigan atampa brown da hijabi milk sai uban kuka take kaman ana yankata sata sukai amota Baba ma ta shiga Baba yamusu sallama Ayaan yatada motar su Baba suka bisu da addu'a sai kano.
[7/17, 12:31 PM] +234 814 359 8303: ♦♦ *SANGARTATTCE* ♦♦

Maman Abd Shakur

37 - 38

Acikin mota haka ta dinga uban kuka dukta rukunkume Baaba daketa bata baki, sai satan kallonta yake ta madubin gaban mota ahaka ta dinga kuka har daga baya wani irin wahalallen bacci yay gaba da ita. "thank God" yafada dan wlh kukan ya cikamai kunne, Baaba dake wurin ne daya mata tsawa shifa bayason iskance iskancen mata da rakin nan fa, nonsense.

Acikin wani ubansu asibiti yay parking yafito da hannu yama wasu nurses guda biyu dake reception alamun suzo da gado da sauri ko suka gangaro gadon suka zo suka gaishe shi batare daya amsaba ya bude bayan motar inda suke ya sakanma Baaba murmushi sanan ya nuna musu ita yace "kuciro ta ahankali karta tashi" matsawa baya yayi yaciro waya yana daddannawa suna fara dagata ta bude idanunta dake buduwa da kyar sabida nauyin dasukai mata fashewa tai da wani irin wahalallen kuka ta rirrike Baaba hakanan dai suka fito da ita suka sata akan gado sai alokacin ya dago kai ya kallesu batare daya kalleta ba dan mugun haushin kukan datake yi yake yace "to my office" wucewa da ita sukayi Baaba nabiye dasu yadau waya yakira matar dake scanning a hospital din yace amata, nan fa aka kaita hadadden office din nashi akazo akafara scanning.

Fita yay daga asibitin yaje wani eatry yaci abinci iya cinshi sanan yayo musu takeaway dan ita yanzu daza'ama operation bazata iya ciba, wuraren 7:30 ya shigo asibitin saida ya tsaya ya karbi report dinta yagama dubawa sanan ya kalli Nurse din wajen yace "set d theater" yawuce office din nashi, yabude ahankali tareda yin yar gajeren sallama zaune ya ganta akan gadon ta

make da bango tana kuka kuka gyangyadi gyangyadi dan yanzu hakama bama taji shigowan shiba, juyowa yay yace "sannu Baaba" ya ijiye ruwa da takeaway din abincin agaban ta ahankali yace "Baaba ga abinci kici, nakira su Mami zasuzo sutafi dake gida kihuta dan theater zamu shiga yanzu, nariga naduba hoton da aka mata dole aiki za'ayi acire" tagumi Baaba tayi tace "oh ni Salamatu shikenan anjama yar karaman yarinya operation, duka duka sha takwas take fa, inda tunda cikin yafara ciwo Malam ya kaita asibiti ai da abu baikai hakaba, amma shi ina saida addu'a da magungunan hausa yarinya sai wahala take" dan murmushi yayi ya mike ya bude wani kofa ya shiga wani hadadden dakine ya bayyana, bathroom ya shiga yayo wanka sanan yafito ya shirya cikin wani green riga ta likitoci wacce ta tsayamai a cinya an rubuta Dr Ayaan ata wurin kan aljihun dakuma doguwar wando yasa hular kayan blue yadau wayarshi yafito yana kamshi daidai lokacin nurse din tai knocking office din afirgice ta farka tana kokarin bude idanunta duka, dan kallonta yayi kafin ya dauke kai ya kalli kofar yace "yes come in" shigowa nurse din tayi tana gunguro wani hadadden gado tace "sir everything is set" gyada mata kai yayi tareda nuna mata Bilkisu dake kuka wanan karan mara sauti dantai bala'in gajiya, ahankali nurse din tadafa Bilkisu tai murmushi tace "my shagwaba friend yama sunanki" cikin kuka ta turo baki tace "Bilkisu kuma niba shagwababbiya bace, ciwo yakemin saisa nake kuka ai" kama baki nurse din tayi dan tasan aikin ta ta iya lallaba patients tace "ai yama rage ciwon tunda gashi baki ya bude, dazu ko uppan baki cewa sai uban ihu dakike mana kunenmu duk ciwo suke yanzu" kara matso wasu sababin hawayen tayi batare datace komiba, hanunta nurse din takama tana dariya Baaba ma dariya tai tace "Bilkisu uwar raki" nurse din tanuna Baaba tace "nuna mata keba mai raki bane taso kihau gadon da kanki" baki Baaba ta rike jin dariya na neman fitomata Bilkisu dai data sani inbadai tadane jin zafin gabaki daya bane shine zata mike da kanta amma inhar tanaji ko kankanu ne wlh bata mikewa, kallon Baaba tayi idanun nan sai shining suke sabida hawayen daya cikasu da sauri Baaba ta mike tsaye tana lullube fuskarta da hijabin ta tace "ke nifa ba dariya nake ba haba mai gadon zinare yar wajena guda" karaf suka hada ido da Ayaan da tuntuni yake tsaye yana daddana waya kaman da gaske nanko kallon su yake kawad dakai tayi kafin ahankali tai yunkurin mikewa tsaye ihu sosai tayi. "wayyo Allah na Mama" komawa tayi zata zauna da sauri nurse din tarike ta daurata akan gadon ta kwantar, fashewa tayi da kuka sosai danji tayi gabaki daya wurin yafara wani sabon ciwon dan dan baccin datayi yasa ya lafa amma yanzu yafara, gungura ta nurse din tayi suka fita daga dakin, dan murmushi yayi yatura wayar aljihun wando ya kalli Baaba yace "ki zauna anan, zaki iya shiga ciki kiyo alwala idan zakiyi salla su Abba nanan zuwa saiku tafi tare dan bansan lokacin dazamu fito daga operation dinba" kaman Baaba zatai kuka tace "to dannan ubangiji Allah yasa ayi a sa'a, Allah yabata lpy Allah kuma yabaku nasara" Ameen ya amsa ciki ciki sanan yabude kofa yafita.

Hadadden theater ta gungurata suka shiga duk tana kuka, ko ina haske wajen, dagota tayi ta zauna da kyar sanan tacire mata hijabin jikin nata tana murmushi ta linke ta ijiye, sanan ta wuce wajen wani hadadden wardrobe din bango ta bude taciro sabuwan rigar nan da ake bama Wayan da za'a musu aiki su saka, tadawo tace "kinga rigar nan zaki saka, dole ki cire na jikinki" ta bayanta ta koma ta zuge zip din doguwar rigan dake jikinta tana kokarin saukar da kafadun rigar ta rike mata hannu tana kuka ahankali tace "zan iya" ahankali nurse din tace "are you sure zaki iya" gyada mata kai tayi da kyar, nurse din tace "okay to bari na taimaka miki ki mike tsaye,

komifa na jikinki zaki cire, wanan rigar kawai ake bukata kisa" aranta cewa take to uban me za'a matane daga dan ciwon cikin nan dahar ake cewa tacire komi najikin ta, tsaki taja aranta, nurse din tarike hannunta ta mike tsaye da kyar tareda dafa gado tana hawaye, nurse din tace "sannu kinji kinama kokari" hannu takai ta zame rigar daga sama yay kasa yarage daga ita sai bra da dogon sket daya tsaya a gwuiwa kasa tai dakai duk kunya ta isheta, dan murmushi nurse din tayi tace "bari nabaki wuri to kicire sauran nan ki ijiye agefe, bari naje nadauko file dinki idan nadawo zan tattare kayan nasaka miki a wardrobe kafin Dr yazo" tana fadin haka tafita daga dakin tareda rufo mata kofa.
Hawaye ta goge kafin ahankali tadanyi bendi kadan ta tube sket din batare data cire white pant din dake jikinta dayabi fatarta yay wani irin kyau kaman jikin wata celebrity, hannu tasa tabaya da kyar ta balle maballin clean white bra dake jikinta, kirjin masha Allah luhu luhu dasu a tsaye, hannu ta mika tadau rigar tabude tana kallo tana kuka mara sauti, tama rasa ta yanda zata saka dan igiyoyi ne ajikin rigar takasa gane inane wuya inane hannu, karan bude kofa dataji yasa ta dago kai atsorace suka hada ido wani irin ihu tayi ta daura rigar agaban kirjinta ta danne da hannu dayan hannun kuma ta daura ta danne ta wajen cinyarta tana wani irin kuka, mayadda kofan yay ya yarufe ya shigo dakin, wani irin firgicewa tayi tana waige waige inda zata gudu tsabagen yanda jikinta da hannayen ta ke rawa yasa rigar fadi akasa, wani irin ihu tayi zata tsugunna tadau rigar amma saitai baya zata fadi sabida yanda cikin yamata wani irin azababben zafi da sauri yataro ta tafado jikinshi yamata iso a fadadden kirjinshi, ihu takeyi amma baya fita tsabagen uban ihun datayi yau muryanta ya taushe tana kokarin kwace kanta amma takasa daidai lokacin akai knocking kofar. "Sir is Dr Ibrahim ur assistant permission to come inside sir" da kyar ya iya bude bakinshi dayamai nauyi yace "she's not ready Ibrahim go, will call u later" okay yafadi yajuya batare daya bude kofar ba, kokarin cirota yake daga jikinshi amma taki sakinshi saima sake rukunkume shi datayi dan wlh bazai gane mata jikiba, dan gajeren tsaki yay awahale kafin yajata ahaka tana jikinshi ya daurata akan gado, still taki rabuwa dashi saima uban kukan datake yi mara sauti, hannun shi yakai bayanshi ya bambare hanunta data kulla abayan shi ya fisge kanshi yana tsaki yana hararan ta, da sauri ta dauki rigarta dake kan gadon ta rufe kirjinta dashi tana kuka, tsaki yasake yi ya tsugunna yadau rigar ya gyara mata ta yanda zata sa sanan ya saka mata akai ya barshi anan wuyan ta, ganin yadan tarufe kirjinta da kaya ya koma baya yana kallonta yanda take sauke ajiyar zuciyar kuka tana share hawayen da sunki dena zuba yace "ke saka rigar nan da kyau an kicire wanan abun na jikinki" yanuna farin pant din dake jikinta, ko kallonshi batayi ba saima kara jajjan rigar take tana rufe cinyarta dashi daidai lokacin akai knocking juyawa yayi kaman ance dole yay maganan yace "who" daga waje akace "nurse Sameera" tsaki yasake yi yakoma kan kujeran dake wurin desk din dake dauke da computer a theater din ya zauna sanan yace "come in" shigowa nurse din tayi tana kallon Bilkisu tace "laa bakisa sakaba har yanzu, ki cire pant din mana" ko kallonta batayi ba, ganin haka yasa ta saukar mata da labulen daya zagaye gadon ta lallabata tacire ta dubata taga tai shaving dan dole idan za'ayi operation ayi shaving sanan ta taimaka mata tasaka rigar sanan ta kwantar da ita akan gadon duk tana kuka ta tattare labulen sama, sanan ta tattare kayan data cire ta linke taje ta ijiye a wardrobe sanan ta dauko roban fitsari tazo gaban desk din dayake tace "Dr nasaka mata robar fitsarin ne incase of fitsari" shiru yadanyi kafin agadaran ce yace "no intanajin fitsari a kaita tayi" komawa tayi ta ijiye tana mamakin shi wanan itace first patient din dayake hana kar asamata kome yahana oho. Bayan ta ijiye ya

kalleta yace "go and call Dr Ibrahim lets start, and the anesthesiologist"
Fita tayi daga dakin shikuma ya mike yaje wardrobe ya ciro rigar operation ya saka ya kulle igayan ta baya yadan juyo ya kalleta yaga tana kwance ta lankwashe kafa tana hawaye, dan tabe baki yayi yaje gaban washhand basin ya wanke hanunshi har zuwa elbow yadawo jikin gadon ya kukkuna wasu mashina yanadan satan kallon fuskar ta idanunta alumshe ya kunna wani wuta dake saman gadon aiko ya haskota bau da sauri ta bude ido tana kakkare fuskarta tana hawaye, hada ido sukayi da sauri yawani dauke kai yakoma yasake wanke hannu sabida abubuwan daya taba sanan yazo ya saka hand glove yadauko dan kwanon dake dauke da different surgical blades daga sterilizing machine yadawo gaban gado ya ijiyesu akan table din dake kusa da kanta da karfi kwanon yay kara hakan yasa tasake bude idon data lumshe tayi ahankali dan bacci bacci tafara ji ta mugun gajiya, wasu Sharpe surgical blades ya dauko kusan guda uku ya nunamata ya daure fuska tamau yace "kingan su, kinga wayan nan wukaken" ya ijiyesu ya sake dauko wasu ya nuna mata yana wani shafa wukan da hand glove din hanunshi amma blunt side din yake shafawa yace "kinsan yanda ake fede akuya?" yay maganan yana kallon fuskar ta yanda ta zaro ido tana kallon wukaken ya kara daure fuska yana kallonta yace "haka zan fideki kaman yanda ake fede akuya yau" wani irin nishi take kaman kirjinta zai fashe, kafeta yay da ido yanda take breathing heavily tana zazzaro ido tana kallonshi, ahankali yasake ijiyesu ya dauko biggest surgical blade din cikinsu ya nuna mata yace "kinga wannan dashi zan fede duka fatocin ki uku na ciki, ur 3 layers duka zan barke" wani irin nishi takeyi hawaye na bulbulowa daga idonta ganin kaman zata sume yasa yace "fedeki zanyi namiki operation da wayan nan wukaken duka" azabure ta mike ta diro daga kan gado kaman mahaukaciya tama manta da ciwon datake fadawa jikinshi tayi ta kankame shi sosai da sauri ya ijiye wukar karya je ya yanka su, wani irin kuka tafashe dashi sosai kafin ta dago kanta dayake akirjinshi danya fita tsawo sosai, kanta ta daura hannayenta takama rigar theater dake jikinshi asaitin kirjinshi ta kalleshi da idanunta dasuka kumburu suna tsiyayar da hawaye tace "mene maka daka tsaneni haka eh?" fashewa tai da kuka sosai ta tace "kome menama ka, dan Allah kayakuri kayafemin, dan Allah karka sakamin wayanan wukaken ajikina, dan girman Allah, dan Allah kayakuri Ya Ayaan" tai maganan tana wani irin kuka tana kallon kwayar idonshi gashi dukta rukunkume shi yanda kirjinta ke bugawa kaman zai fashe tsabagen tsoratatar dayayi, ta maida kanta kan kirjinshi tana wani irin kuka mai tsuma rai tana furta "kayakuri kayakuri" agalabaice, ahankali yadan lumshe ido tareda sakin gajeruwan ajiyar zuciya.
[7/20, 12:30 PM] +234 803 238 4602: ♦♦ *SANGARTATTCE* ♦♦

Maman Abd Shakur

39 - 40

Ahankali yadaura hannayen shi akanta yana shafa manyan da kananun kitson dake kanta batare daya bude idanun daya lumshe ba, knocking kofar da akayi yasa yadan bude ido ahankali yace "common in" yay maganar yana saukar da hannayen shi daga kanta tareda gyara

bayan rigarta. Dr Ibrahim, Nurse Sameera da Anesthesiologist mai suna Moses ne suka shigo dukansu atare, da ido yama Moses alamu ya shirya alluran, hannu yasa zai cirota daga jikinshi amma taki sakinshi sai kuka take kasa kasa, daukar ta yay batare data sakeshin ba ya kwantar da ita akan gadon zai tashi takara rirrikeshi tanamai kukan dabaya fita sosai tana kallon fuskar shi, jin yanda kirjinta ke bugawa yasa yadan hadiye haushin kanshin dayake ji namata wani laushi ahankali yace "relax nafasa miki to, calm down" sake kama rigarshi tai gam gam kaman mai rada tace "dagaske" yana kallon yanda lips dinta sukai jajir tsakiyar ya gyada mata kai yakai hanunshi bayan rigar yadan bude daidai inda za'ayi allurar da Moses yagama hadawa batare data masan yayiba dan duk hankalin ta atashe yake da wukaken dayace zai fedeta, da ido yamai alamu yayi, sanan yadan kalli fuskarta yanda take kallonshi da idanunta dasuka kankance tsabagen kuka ga dogayen gashin idon duk sun jike sun mammanne da juna kaman tasa gum, iskan bakinshi ya hura mata akan idon hakan yasa ta lumshe idon da sauri, wani irin azaba dataji tabayan ta yasa ta bude ido tareda kara damke shi da karfi tana kuka sosai saikuma luuu ta komar da kanta kan gadon wani irin bacci yay gaba da ita batare data sakeshi ba, dan murmushin gefen baki yayi sanan yasa hanunshi yacire hannayenta dake kan rigarshi ya maidasu kan gadon ya ijiye tareda sake gyara mata kwanciya ya dauko wani zani yarufe tundaga kafarta har cikinta sanan ya bude daidai wajen ciwon yadau abun rufe hanci da baki yasaka tareda kunna wutar operation, samira data rike kwanon surgical blades din da tagama kirgasu tace "Sir daga gani wanan patient din is very special sai kappa kappa kake da it..." wani irin kallo daya mata yasa tai shiru bata karasa ba, wani abu kaman marker Dr Ibrahim ya mikamai nan yay layin daidai saitin inda zasu yi aikin, sanan yakara mika hannu aka sakamai wani surgical blade akai, ahankali yadan kalli fuskarta kafin yasaukar dawani labule daya raba tsakanin su, sanan yama Moses magana yakara sakko da wutar kasa sosai yanda zasuga cikin da kyau, wukar ya dauka ya yanka fatar wajen Dr Ibrahim na share jinin dake zuba.... Nan dai operation ya kankama.

Akan kujera dake hanyar wurin theater din duk suka zauna Mami, big Mummy da Baaba dasuke ta bata baki dan kuka take ganin yanzu kusan awa uku kenan ba'a gamaba balle a fito, Abba da Baba Sulaiman suna tsaye suma addu'an samun Ipy ta suke.
Anyi anyi Baaba tazo atafi gida taki tafiya wai ita sai taga anfito da Bilkisu tukunna zata tafi.

Sai wuraren 12:50 nadare suka gama operation din tatas, sai kallon appendix din daya cire mata suka saka awani kwalba yake yanda yay girma sosai dan gab yake daya fashe, inda kuma yafashe da mutuwa zatayi wlh. Da kanshi ya gungurota daga gadon dan kaita dakin hutu yana fitowa kam yaga su Abba dasu Baaba sun tatashi suna kallonta, Baaba ta fashe da kuka tana tattaba fuskarta ganin bata motsi, dan murmushi yay yace "Ipy ta lau bacci take zata farka, operation din was successful" Alhamdulillah duk suka ce, yace "bari nakaita dakin hutu" wani daki ya bude kofa ya shiga da ita dakin mutum dayane ga gado ga tv harda fridge sanan akwai bayi aciki, ahankali ya dauketa sabida dinkin ya daurata akan gado yadan sake kallon fuskarta kafin yajuya yafita dan zuwa dauko wani rigan asibiti danna jikinta duk yabaci da jini, tsayawa chak yayi yay folding hanunshi akirji jin yanda Abban shi ke tonamai asiri a hospital.
Dariya Nurse Sameera da Dr Ibrahim harma da Moses sukayi, Nurse Sameera tace "habawa no wonder naga Dr was extra careful sai lallabata yake kaman Kwai shida baya wani lallaba

patients, ashe matar shi ce" Abba yawani kara washe baki yace "biki ma har yana neman wata biyu" Dr Ibrahim yace "lallai nema shine koya fadama" daure fuska yay yazo zai wuce wajen ya shiga theater Abba ya fizgo shi, kaman zaiyi kuka yace "Pops kaga kadena badani a wajen aiki, ni kuma zo kutafi please" ya karashe maganan kaman zai mutu sabida haushi, Big Mummy tace "dont mind them boy kuzo mutafi" ta kalli Abba tace "mu barshi yay aikin shi da kyau gaskiya Alhaji". Kaman zaiyi kuka ahankali yace "stop calling me Boy in front of them big Mum" rufe baki big Mummy tai da sauri tanaso tai dariya aiko duka wajen aka kwashe da dariya, shigewa yay theater abinshi Abba ya kalli Baaba da Mami dake zaune suna yar dariya suma yace "mutafi gida ki huta ga mijin tanan ai xai kwana da ita" hakanan suka tashi sukaje driver yajasu sai gida

Sabon kayan asibiti ya dauka ya koma dakin ya ijiye kayan akan gadon yana kallonta yanda fuskar ta yay fayau tsabagen wahala da kuka gakuma santala santalan cinyoyin ta dasuka bayyana, dan gajeren tsaki yaja yay gaban gadon yadan zauna ta baki bakin kafin yasa hannu ya dagota ahankali, dan igiyan bayan rigan ya warware yana wani ciccije lebe, sakin igiyan yayi kafin yakai hanunshi ta gaban rigar yawani ja rigar kasa da sauri ya saketa tafada gadon bam dudda cikin bacci take saida tadan yatsine, runtse idonshi yayi da karfi kafin yadan mikar da hannu yana kokarin ya maida mata rigar inyaso yafita yakira Sameera tasamata, neman rigar yake wacce ya zameta takai kan cikinta, hanunshi dayaji ya sauka akan kirjinta yasa ya matsa baya da sauri har yana bigewa da kujera yace "f*ck!" fita yay daga dakin da sauri kaman ana ingiza shi, yay hanyar office dinshi daidai lokacin Nurse Sameera tafito daga dakin wata patent daure fuska yayi yace "kije ki chanza mata riga" ahankali tace "to Ango" wani mugun kallo dayamata yasa tabar wajen da sauri tana gimtse dariya, office dinshi yakoma ya shiga ya rufe kafin ya wuce bedroom din ciki, bayi ya shiga yay wanka abinshi yafito daure da towel fridge din dakin yabude yadau Vita milk mai sanyi ya bude yakoma kan gado yana sha, agogo ya kalla yaga har daya nadare yawuce ma tsaki yayi dan bazai iya kiran Meram ba is too risky hakan yasa ya ijiye bottle din yakoma ya kwanta sai bacci ba zancen salla.

Wuraren 8:30 yatashi da kyar, ya shiga bayi yayo brush yay wanka yay alwala, yadau mai ya shafa sanan ya shirya cikin dogon black jeans da soft cotton t-shirt maroon bakaramin kyau yamai ba color, ya shafa man gashin shi dake karasa gashin kanshi kyalli sanan yadau turaren shi mai kama jiki ya fesa kafin yahau dadduma yay sallan asuban yana idarwa ya mike yana kallon agogo dan baida lokacin yin azkar, takalmi ya zira sanan yadau lab coat yafita once ya zagaye ward yaduba patients dinshi da yarinyar chan gida zai tafi ya huta tun jiya baihuta bafa. Saida yagama duba patients sanan yawuce dakin datake tun kafin ma ya shiga yaji maganan su Abba, daure fuska yayi ya shiga dakin, Abba dake shirin fita shida Baba Sulaiman ya kalla yace "Morning Pops, morning Baffa" kanshi Abba yazo zai shafa da sauri ya doje dan bayason abinda zaisa yarinyar chan ta raina shi, Abba daya bishi da kallon mamaki saikuma yay shiru shida Baba Sulaiman suka kalli juna sukai murmushi Abba yace "muntafi office, anjima da yamma zamu dawo" daure fuska yasake yi yace "saikun dawo" murmushi Abba yay suka fita daga dakin Baba Sulaiman yace "daga zuwan matar shi yasoma girma bayason kana badashi, shiba yaro bane ba yanzu wayaga su Ayaan da iyali" dariya dukansu sukayi Abba ya gyara zaman babbar rigarshi yace "ai haka nakeso dama".

Sai alokacin ya kalli Mami da Baaba dake hirarsu, yadan saci kallonta tana zaune cikin riga da sket na material mai taushi dark blue sai dot din white ajiki, kanta rufe da white hula tazauna tana jingine da gado idanun nan sunyi jajir alamun bata dade dagama yin kuka ba, ga dan karamin cup da aka mata tea aciki tana deba da cokali tana sha dan kin yarda Mami tabata tayi, ahankali take sha bakaramin kyau taiba, dauke kai yasake yi ya kalli Baaba yace "ina kwana" kafin ta amsa ya kalli Mami da tunda tamai kallo daya bata sake kallonshi ba dan har yanzu basu shiryaba, yace "Good morning Mami" Baaba ce kawai ta amsa shi tamai ban gajiya da sannu sanan ta kalli Mami dake magana da Bilkisu kasa kasa tace "suruka nidai zomu zaga nagaji da zama wuri daya jikin tsufa kafafuna sunyi tsami" dan dariya Mami tayi ta tashi tana gyara zaman babban gyalen jikinta tabi bayan Baaban harara ta watsa mai dasuka hada ido da sauri ya dauke kai, saida ya waiga yaga sun fita sanan yawuce gaban drawer dake dakin yajawo yana kokarin ciro wani drip dake ciki ya juyo da kai ya kalleta fuska adaure ganin daga fitar su tasoma matsar hawaye yace "ke!" kin kallonshi tayi dan wlh kallonshi kadai tadamata da hankali yake barin ma dazu data tashi akace operation yamata ga wajen na bala'in mata zafi ganin su Abba ne yasa ta mugun daurewa. "ke!" yakara daka mata tsawa daidai lokacin ya matso wajen gadon, arude ta kallai hawaye na gangarowa daga idonta yawani daure fuska yace "agidan ku ba'a koya miki gaisuwa bane" da kyar ta iya bude baki heart dinta na racing tace "in ina kwana" tsaki yaja ya kalli cup din tea hanunta ganin ko rabin tea batayi ba yay tsaki yace "malama finish dis tea nasamu nabaki maganin ki inba hakaba inbar wajen dinkin yay tsami daga bayama ya rube" yakara she yana wani irin hararan ta kafin yajuya yafita daga dakin, pharmacy dinsu yaje dakan shi ya faffadi magungunan da xa'a kawomai ya ciro ATM card dinshi yabiya da POS sanan yadawo dakin, tadan sha tea dudda bata shanye ba, wani cup ya dauka yadebo ruwa a dispenser dakin na zafi ya sirka dana sanyi ya danyi dalam dalam ya mika mata yana dauke kai, ahankali hanunta har rawa yake ta karba zatakai baki tsawa yadaka mata "ke wai nace kisha ne, God she's so so dull" yay tsaki yadauko ledan ya ciro magungunan dazata sha kusan kala biyar, ya babbalo tablet da capsules din yasaka ahannu ya mika mata, ahankali ta mika hannu tana goge hawaye da bayan dayan hannunta ya saka mata, sosai take kuka wanan karan harda kara, tasa dayan hannunta tana kirga uban kwayoyin maganin daya bata tasha kaman zararra, guda goma shadaya, dago kai tayi ta kallai kafin tasake fashewa dawani irin mugun kuka mara sauti dan ko nishi mai karfi bata yi sabida ciwon, sai ta kalleshi ta kalli magungunan tafin hanun nata tafashe da kuka dan har ga Allah bama tasan ta yanda zata hadiye duka magungunan nan abakin taba ita bama tasaba shan kwayoyin nanba jike jike Baba kemata, dan murmushin gefen baki yay saikuma ya zauna akan gadon kusa kusa  da ita da sauri ta makale jikin bango, hanunshi yasaka akan hanun nata ya kwashi duka magungunan ya rike kafin ya ciro biyu ya mikamata, karba tai atsorace takai baki takai ruwa tana bata baki tasha, sake mika mata biyu yayi tasha, yasake mika mata biyu tahadiye, zai kara bata biyu tafashe da kuka tana girgiza mai kai, daure fuska yay hakan yasa ta karba ta hadiye da kyar ya mika mata ukun dasuka rage babu alamun wasa akan fuskar shi da kyar tasha kaman zata suma ya karbi cup din ruwan ya ijiye yana duba agogon hanunshi kiran Rolex, saida tai exactly 5 minutes sanan ya mike tsaye ya dauke cup din tea data rage ya ijiye akan table ya kalleta yace "ke kwanta inason na duba inda na fede" ko kallonshi batayi ba saima dauke kai datayi tana kokarin hadiye hawayen dake shirin zubowa, takowa yayi yadaura hannunshi akan kafadun ta da sauri ta kallai kirjinta na bugawa ahankali ya kwantar da ita ya daura kanta kan

filo batare daya janye idonshi daga kan fuskarta ba, runtse ido tai da sauri sabida wani irin azaban dataji, hannun ya cire daga kafadar ta ya dage rigar sama, bugawan da kirjinta yayi harsaida  yagani daga cikinta, wajen dinkin yabi da kallo kusan na 3mnutes kafin ya mike tsaye ya makala drip din daya dauko akan karfen makalasu yamata fixing drip din yadauko wasu allurai yay acikin ruwan 8sanan yadawo bakin gadon ya zauna yana kallon wurin aikin kafin yabi cikin gabaki daya da kallo yanda yay flat ga fatar looking fresh sai glowing yakeyi, ahankali ya mika hannunshi ya daura akan dan cibiyar ta, da sauri ta bude ido ta kallai atsorace ita shima yake kallo akasalan ce yace "wat?" shafa cibiyar yacigaba dayi ahankali kafin ya gangara da yatsar shi zuwa inda yay dinki yana zagaye wurin hanunta ta daura akan nashi tana wani irin wahalallen kuka, akaro nabiyu yakara kallonta murya kasa kasa yace "wat?" da kyar ta iya bude bakinta tace "zapi" hanunta data daura akan nashi yabi dawani irin kallo hakan yasa tai yunkurin janye hannun da sauri ya rike hanun yana kallon fuskar ta kafin ya maida dubanshi ga hannun, ahankali ya sa hanunshi ya shafa tsakiyar fatar hanun nata yana feeling yanda hanun keda wani irin taushi kaman hanun jariri, bin jajayen yatsun ta dasuka sha lalli yay da kallo kafin ahankali yakai yatsar wurin bakinshi yana kallon yanda idanunta ke fitar da hawaye.
[7/20, 12:30 PM] +234 803 238 4602: ♦♦ *SANGARTATTCE* ♦♦

Maman Abd Shakur

41 - 42

Ahankali yasa yatsar cikin bakinshi yana wani irin tsotsar yatsar kaman yasami minti, sosai takara karfin kukan ta sabida yanda takejin wani iri gashi yaki bata daman fizge hanun, knocking kofar akayi hakan yasa yacire hanun daga bakinshi ya maida ya ijiye yana kallon fuskar ta da idanunshi dasuka chanza launi yay hanyar kofar yabude wata Nurse ce Amina dan Sameera tagama night wanan tai taking over, gaidashi tayi batare daya amsaba yace "ki cema Dr Ibrahim ya dubata dan i will not be available today" yana fadin haka yasa kai yafice daga dakin office dinshi yakoma yadau car keys da wayarshi yafita daga office din bayan ya kulle, wajen parking yaje ya shiga motar shi yabar asibitin gidanshi ya wuce direct yay parking yafito ya shiga ciki, akan dogon kujera ya kwanta jin kaman ma zazzabi zazzabi na neman rufeshi, wayarshi ya lalubo daga aljihun wando yay dailing number Meram saida kiran yakusa katsewa ta dauka tai shiru, dan murmushi yay dan tunda taji labarin yay aure tadau zafi sosai, dan murmushi yay yace "ina jiran ki agidana now" zatai magana ya katse wayar tareda kara gyara kwanciya ya sanya hannayenshi abayan kanshi yana kallon POP, tashi yay zaune ya dunkule hannu ya daki iska angrily, kafin ya dafe kanshi, tashi yayi yawuce bedroom dinshi yafada kan gado ya lumshe ido. Wajen 30min Meram ta dauka kafin tazo tana sanye cikin wani open neck white top me spaghetti hand sai strap belt long skinny pant navy blue, braids ne akanta masu tsawo babu dan kwali tafito daga motar taci uban hill tai cikin gida bayan tai parking rike da yar jakarta na Louis Vuitton tana taku daidai ta shiga gidan tana tauna cingum ta mugun daure fuska, ganin baya sitting room yasa tai bedroom dinshi yana kwance idanunshi biyu saidai duk sun kankance tsayawa tai daga kofa tana kallon shi yanda maroon t-shirt din jikinshi ya mugun

yimai kyau tai kewanshi bakadan ba itama tasani amma maisa zai yi aure aboye bayan yasan yanda take sonshi, dan juyo dakai yay ya kalleta sabida yanda jikinshi yabashi ana kallonshi, kafeta shima yay da ido batare dayace mata ta shigo ba, dauke kai tayi daga kallonshi cike da basarwa tace "why are u calling me? Bani ka yaudara ba kana using dina sanan kaje kai auren ka, ancemin ma yarinya kaje ka auro, very decent ba irinaba, ni kawai am just ur machine ko, u use me as u pleases, hmmm har ka gaji dacin amarcin ne ka kirani dama..." "Ke!" ya daka mata tsawan dayasa tai shiru, tashi yay ya zauna abakin gado da idanunshi dasukai jajir ya nuna mata kofa yace "out" bude ido tayi tana kallonshi cike da mamaki yasake nuna mata kofa yace "i said out kema kinsanni bana rokon abu, are u expecting me na lallaba ki dannai aure, dama chan ni saurayin kine? Okay is over Fita daga nan, i don't need u as well rubbish" yaja tsaki rai abace, fashe mishi tai da kuka ganin yanda yaci serious tafado jikinshi tana kuka ta kankame shi tana kissing face dinshi tace "am sorry Ayaan please karka rabu dani, naji na yarda i will be ur side chick, have me" ta wurgashi kan gado yanda jikinshi yay laushi ne yasa yatafi shima luu, nan ta shiga aika mishi da sakkonni kafin ya biyemata dan dama yana cikin sananin bukata.

Tunda ga ranan bai kara komawa hospital dinba kiran Abba ma yayi yace "yatafi wani conference meeting a Abuja" daganan ya kashe wayarshi dukama dan bayason damu. Dr Ibrahim ke kula da ita bayan 5 days ya sallameta aiko taji dadi dan tagaji da asibitin ga dinkin ya fara warkewa dan jikinta nada kyau sosai da kanta zataje bayi tai alwala tai wanka kawai dai bata daukan abu mai nauyi ne kwata kwata, gidan su Abba aka wuce da ita sabida takara warkewa kafin akaita gidan mijinta idan yadawo.

Yau satin ta daya agidan taji sauki sosai yanda Abba da Mami keji da ita ita abinma har kunya yake bata.
Tana kwance hadadden adakin ta lullube da bargo ta daura kanta akan cinyar Baaba daketa fama da Mami ita gaskiya zata koma yau Mami namata dariya, sallama Abba yayi ya shigo Mami tace "yauwa Alaji kajifa wai tadage tafiya zatayi yau" kaman Baaba zatai kuka tace "to Alaji taji sauki dan Allah kubari natafi nabar Muji shi kadai agida" itadai lumshe ido tayi kaman tana bacci dan batason Baaba ta tafi dan ita take gani takejin dadi, Alhaji yace "to to to shikenan ai, amma ki shirya" ya kalli Mami yace "muje mu kaita taga gidan yarta ko anjima inmun dawo sai nasa driver ya kaiki zaria" washe hakora Baaba tayi Alhaji yafita yana dariya, tashi tayi tana kallon fuskar Bilkisu data lumshe ido ta kalli Mami tace "kinga kasar nan ashe bacci tayi ana hira" dariya Mami tayi tace "yata ba kasa bace kibarta tai baccin ta tunda fita zamuyi" hijabi Baaba ta dauka suka fita da Mami tare suna hira a down stairs suka hadu da Abba da big Mum da itama ta shirya duk suka shiga mota Alhaji yajasu suka fita daga gidan. Gidan yarage daga ita sai yan aiki.

Wani ubansu gida Abba yakai Baaba, sakin baki kawai tayi tana kallo dan gani tayi gidan ma yafi gidan su Abban kyau, horn Abba yayi gateman yazo yabude suka shiga, babban compound ne da aka bi bangon da flowers, sai runfan parking motoci sukai parking suka fito, bayan gidan suka fara zuwa wani ubansu garden ne daga gefe daya kuma wani hadadden swimming pool ne, ta kofar kitchen dake garden din sukabi suka shiga kitchen Baaba dai kasa rufe baki tayi

yanzu Bilkisu tane zata zauna awanan gida irin gidan shugaban kasa lallai Bilkisu akwai goshi, fita daga kitchen din sukayi sukai parlor komi white and sky blue harda kujeru, center carpet da labulayen, ga gefe kuma wani babban fish bowl ne kifaye sai wasa suke aciki yanda Baaba ta dinga yi yasa suka dinga mata dariya sukai upstairs inda wani parlor ne awurin sai dakuna uku na farkon suka shiga komi off white ne, sai kuma dayan dakin da akai brown and milk dayan kuma akai brown zalla, kafin su kara komawa wanda akai brown and milk akwatunan ciki guda 24 Mami da Big Mummy sukahau bude mata shikuma Abba yakoma kasa danyi waya, sai kallon akwatinan Bilkisu take tana mamaki, Mami tace "dazaran yadawo daga Abujan zasu tare in sha Allah" nan fa Baaba ta bingile da ciro kaya tana dubawa tasami na bada labari a zaria.

Ahankali tayaye bargon data lullube dashi dan takasa baccin, suna fita taji gidan yamata wani iri duk ba dadi, mikewa tai tsaye tana sanye da soft jersey drape skirt black sai pink crop top daya dan saukan mata kasa amma bai rufe cibi ba sabida ma ance tadinga barin wurin dinkin nashan iska ne yasa Mami ta siyo mata irin kayan yakin, skirt din yabi jikinta sosai ya fito da shape dinta dudda bai wani kamata ba, rigar kuma tamata chachas ajiki tareda kara bayyana kyan surarta, dan black hulane akanta wanda yadan zame baya gashinta da aka tsefe aka gyara mata ya bayyana duk ya kwanta yana shining, wayarta tadauka tasaka bathroom slippers white daya bayyana fararen dogayen yatsun kafarta tafito tana tafiya ahankali harta sauko down stairs babu kowa afalon gashi bata iya kunna makeken tv bangon suba, dan tsaki tayi tai hanyar fita daga dakin tafito tsakar gida sai kalle kalle take ganin babu kowa sai uban motocin dasuke apake, ahankali take tafiya tana dan yatsine fuska dan rabon ta da tsakar gidan tun randa aka sallamota daga asibiti, ahankali take ta tafiya tana zagaye gidan harta ganta a garden, bin wurin tai da kallo yanda flower din wurin sukai kore yirr ga watering can akasa, cigaba da tafiya tayi tana shafa flowers din tana murmushin dake lobar mata da dimple, karan katca dataji yasa tadan daga kai ta kalli saitin inda taji karan wani worker gidan ne dake sanye da uniform yana bama wani dan biri haka dake sanye da kaya ajikinshi jeans da riga ayaba, an daure burin ajikin bishiyan mango da chain, ware ido tayi cike da mamaki harda dan saurin ta takara so wajen ta kalli mutumin dayake ta kallonta sanan ta kalli birin dake kallonta shima yanacin banana, ta nunashi da hannu tace "laaa monkey dama da monkey agidan nan, monkey wayene?" murmushi mutumin yayi yana barema birin wani ayaban yace "na oga ne wlh, bakiga yanda yakeson monkey nanba, shima monkey haka yake sonshi kome yace yayi saiyayi" murmushi tayi batare data matso ba dan tsoron biri take tunda aka taba labari a school wai biri nason mata yanxu ma dan taga akulle yake da kacah ne saisa tazo tana kallonshi, ganin yanda aka samai kaya masu kyau harda sarka awuya sai abin yabata dariya ma, mai aikin yacigaba da kallonta yana bama birin ayaba yace "amma ke ba yar gidan nan bace ko, bakuwa ce dan bantaba ganin kiba wlh" gyadamai kai tayi batare data janye idonta daga kan birin daketa dambe da ayaba ba, shikuma mai aikin sai binta yake da kallo daga sama zuwa kasa yana wanan kyakkyawan fa haka aranshi. "kai!" atsorace daga shi har ita suka juyo sakamakon wani irin tsawa daya dakama mai aikin, yana sanye da white singlet daya kama jikinshi sai neon Beach floral 3 quarter, fuskar nan babu alamun wasa, da hannu yamai alamu yazo, da sauri jikinshi har rawa yake ya karaso gabanshi kanshi akasa yace "good morning si..." wani wawan mari Ayaan ya dauke shi dashi azuciye kafin yanunamai hanyar barin garden din yace "u are fired, out" ganin babu alamun rahama afuskar shi yasa guy din yabar garden din da sauri, arude

sumi sumi jikinta har rawa yake tazo zata wuce ta gefenshi ya damko hanunta ya maida shi tabaya ya lankwasa ihu tayi "wash Allah na wai mena maka ne nikuma?" juyo da ita yay takusa fadawa jikinshi da idanunshi dasukai jajir yace "are you trying to seduce my workers" kallonshi tayi da idanunta dasuka cicciko da kwalla tama kasa magana ya daka mata tsawa. "am talking to you" hannu tasa ta taushe kunenta sabida yanda dodon kunenta ya amsa tafashe da kuka sosai fizgan hanunta yy takusa faduwa yajata har side dinshi wanda shine ke tare da garden din kofar ya bude ya jata ciki wani kamshi da sanyi sukai mata sallama wurgar da ita yay akasa tafashe da kuka ya maida kofar ya rufe, arude ta mike tsaye tana waige waige, ganin ya dumfarota da idanunshi da suka chanxa kaman banashi ba yasa ta shige bedroom da gudu kafin ya iso ta kulle kofar, key data gani ajiki tasaka ta kulle tacire key tana komawa da baya tana kuka sosai, buga kofar yayi azuciye yace "ke kibude kofar nan tunda ba gidan ubanki bane, kibude nace" komawa baya tadinga yi harta jingina da jikin wardrobe ta sulale kasa ta kama kafafuwan ta tana kuka tana kuma addu'a Allah dawo dasu Mami.

Key dataji yasaka a kofar yana murdawa yasa ta mike tsaye da sauri kirjinta na bugawa bude kofar yayi yawani bugo da gudu ta kwasa zatai bayi taku daya yay ya damkota yajawota jikinshi tana kokarin fizgewa amma saida ya hadata da kirjinshi ya matse, yanda take nishi kaman zata mutu ne yasa yace "ke" abakin gado ya zauna har lokacin kanta na kirjinshi tana kuka, cirota yay daga jikinshi yana wani irin hararan ta, kin kallonshi tayi saima bayan hannu datasa tana share kwallan daya zubo mata, yanuna ta da yatsa da kakkausar murya yace "wlh duk randa kika kara fitowa tsakar gida ahaka saina zaneki da belt mara hankali kawai" murya chan ciki tace "niba mara hankali bace saidai kai" bakinta dayaga yay motsi yasa ya kama hanunta atsorace ta kallai yace "me kikace?" dauke kai tayi ta turo baki tareda zame hulanta daga kai tana goge hawayen daya bata fuskarta tace "ni bance komiba" dogon jelar gashin ta yabi da kallo kafin ya maida kallonshi kan fuskar ta ganin kokarin fizge hanunta take batare data kallai ba, murya chan kasa yace "hau gado na duba ciwon ki" ko kallonshi batayi ba tace "ai ya warke baya zafi" dan murmushi yayi ya kalli cikin inda akai aikin kafin yamike tsaye daukar ta yay hakan yasa ta fasa uban ihu kaman zata tsaga gidan, buge bakinta yay da sauri tai shiru ya kwantar da ita akan lumtsetsen gadonshi shi da sauri tai yunkura zata tashi ya dakamata tsawa. "ki natsu" ba karamin tsoron yanayin fuskarshi tajiba hakan yasa ta kulle idonta kam kirjinta na bugawa, fuskar yadan kalla kafin ahankali yakai hanunshi gun ciwon yadan taba kadan sanan yacire hannu, flat cikin nata yabi ya kallo kafin ya sauke idanunshi akan kirjinta dake cikin rigar ya kafesu da ido, jin baya taba cikin yasa tabude ido ahankali karaf suka hada ido da sauri ta janye nata ganin yanda ya cika mata ido ta tashi zaune ta sauka daga kan gadon duk yana kallonta, hanyar kofa tai da sauri zata bude tafita, da kakkausar murya yace "ubanwa yabaki izinin fita" da sauri ta juyo idanunta sun cicciko da kwalla, mai matsalar mutumin nan da itane wai, da yatsa ya nunamata gadon yace "dawo inda kike" ahankali tafara tafiya tadawo kan gadon ta zauna nesa dashi tana goge kwalla, mikewa tsaye yayi yaje gaban fridge din dakin ya bude yaciro farm fresh yogurt ya cika glasscup sanan ya mayar cikin fridge yadau laptop dinshi dake kan kujeran dakin yadawo bakin gadon ya kalleta yanda taketa share kwalla, wani irin mugun kallo yamata yace "matsa ciki ke" a tsorace ta matsa cikin gadon ta jingina da bangon gadon azaune tana share kwalla kirjinta sai bugawa yake, ajiye glasscup da yogurt din ke ciki yayi akan bedside drawer ya kwanciyar zama yasa pilo akan kafarshi yadaura laptop akai

tareda gyara zaman kanshi a filo biyu daya hada yana daddana laptop din batare daya kalleta ba yadauko yogurt din yana sipping kadan kadan yana danna laptop da hannu daya, sosai take share kwalla duk hankalin ta yatashi takara makewa ajikin gadon gashi sanyi takeji sabida yanda ya kara Ac sosai. Yakai kusan 10mins yana abinda yakeyi kafin yajuyo dakai ya kalleta har lokacin share hawaye take da bayan hannu ya daure fuska yace "ke" kaman bata jishiba haka tai hakan yasa ya dakamata tsawa. "ke" arude ta kallai, glasscup din yogurt din da har yanzu ko rabi bai shaba ya mika mata alamun tazo ta karba girgiza mai kai tayi wasu hawayen na zubowa, yanda ya kafeta da ido babu alamun wasa yasa taji gabanta yafadi ahankali ta rarrafo zuwa inda yake ta karba tana kuka mara sauti zata koma inda take yace "ke anan zakisha" gyada mai kai tayi duk ta rude dan bata saba ganin namiji a singlet ba, kaiwa bakinta tayi tafara sha duk yana kallonta da gangan yakara daka mata tsawa ganin zata shanye. "ke nace ki shanye duka ne" da sauri tacire cup din daga baki tana girgiza mai kai ta mikamai cup din, karba yayi yana kallon yanda yogurt din yama sama lebenta layi kaman gashin baki, zata koma inda take ya harareta yace "karki sake ki tashi" zama tayi dukta rasa inda zatasa kanta sai goge kwalla take da bayan hannu, glass cup din yakai bakinshi shima yanashan Yougurt din data rage yana kallon fuskar ta ya tura hanunshi a aljihu yaciro handky ya mikamata yace "clean ur mouth" karba tayi ta share bakinta batare data share inda Yougurt din yabata ba ta mikamai handky din tana kokarin boye hawayen dake shirin zubo mata, karba yayi tareda ijiye cup din akan bedside drawer ya kalleta da lazy eyes dinshi murya chan ciki yace "baifita ba zo na share miki" yay maganar yana daura hanunshi abayan ta, arude ta kallai tareda sakin kukan dayake cinta, hannayen shi biyu ya daura a bayanta ya jawota zuuuiiii tazo jikinshi janye hanunshi yay daga bayanta lazy eyes dinshi akan lips dinta inda Yougurt yabata, hada goshin shi yay da nata da sauri tasake kallonshi suka hada ido azabure tafara kokarin mikewa amma baibata damar ba, hannunshi daya yakai ta bayanta ya janyota ya hadata da jikinshi da kyau shikuma yay relaxing bayan shi ajikin bangon gado, yasa dayar hannun yakamo habarta yana kallon yanda ta runtse ido gam tana kuka jinkinta har barbar yake, matso da kanshi yay sosai saitin fuskar ta dan sunajin numafashin junan su kafin ya fito da harshen shi ahankali ya daura akan saman upper lips dinta yafara lashe yogurt din.

*inhar kasan baka biyaba ka karanta ban yafeba, dan novel din kudine*

In kanason littafin nan chat me up tanan 07012181461
♦♦ *SANGARTATTCE* ♦♦

Maman Abd Shakur

43...

Kokarin juyar dakai tafara jin wani irin zirr zirr da jikinta keyi har kunnuwanta, yasaka hannayen shi biyu yay cupping fuskarta kafin yakara fito da harshen yafara lasan yogurt din ahankali ahankali kaman yana tickling dinta har yagama lashewa yakara resting fuskarshi akan nata yana kallon idonta yanda ta runtse su ta kankame su gamgam hawaye na bubbuluwa ta gefe,

kirjinta na mugun bugawa, dogon hancinshi ya daura akan nata dogon hancin yadan jujjuyar da kanshi hakan yasa hancin suka bugi juna, tsayawa yay batare daya raba fuskokin suba ya kafe lips dinta da ido, ahankali ya gangaro da bakinshi ya daura akan lips dinta da sauri ta mayad dasu ciki ta daure bakinta gamgam tana nishi kaman mai asma, murmushi yay ya saukar da hannunshi daya yakai gefen cikinta dakeda Ipy yamata chakulkule da sauri tasaki bakin zatai ihu ya kamasu, wani irin kiss ya shiga mata tana mutsu mutsu iya karfin ta ta kwace bakinta amma takasa kara janta jikinshi yay sosai ya saka hannun ya tunbuke ribon din data kama gashin kanta dashi ya hargitsa mata gashin gabaki daya, sosai take kuka kaman zata mutu saidai ba kara sabida bakinta daya kama, mirginowa yay yana kokarin juyawa dauke da ita ajikinshi sukaji karan laptop bam yafadi akasa, karan yasa ta daddage ta fige bakinta dayake neman katsawa da kyar tana mugun kuka shikuma ya juya da kyar ya kalli laptop dinshi dake kan jikinshi daya fadi warwas akasa, dan sakinta yay batare daya cireta daga jikinshi ba ya mika hannu daya kasa yana kokarin daukan laptop din yaduba dan akwai a whole lot of patient records aciki, fizge jikinta tai wup da gudu tafita daga dakin tana haki ganin hularta ga gashin ta duk abarbaje tai waje ahaka yasa ya mike tsaye da kyar yabita, tsaye yaganta tana falo tana faman murda handle tana kokarin bude kofar yaki buduwa yana gab da isota tasamu tabude tafice kafin tafita daga balcony din ya cimmata ihu tabude baki zatayi ya daura hannunshi akan bakinta yana hararan ta tareda jawota jikinshi, tafashe da kuka duk jikinta na rawa ya kafeta da ido, daidai lokacin Mami da tundazu suka dawo sai nemanta suke basu ganta ba ta tambayi yan aiki sunce basu ganta ba hakan yasa hankalin ta yatashi tafara zagaye gidan, kaman ance ta daga kai ta hangosu tsaye Ayaan na kokarin sakamata hula, da sauri ta juya Ayaan daya dago kai ya ganta yace "gud afternoon Mami na" arude tafara kokarin fita daga jikinshi jin yana gaida Mami, sakinta yay ta fizge hularta kanta akasa sabida kunya, dan juyowa Mami tai ta kallesu sau daya kafin tacigaba da tafiya abinta tace "saukar yaushe, daughter kizo kiyi sallama da Baaba" ta wuce abinta da sauri tabi bayan Mami tana saka hular duk arude, bin yanda take tafiya yay da kallo kafin yay dan murmushin gefen baki ahankali yace "she has special lips, soft skin, soft hand" dan tabe baki yayi kafin ya koma ciki ya dauko black shirt yakasa yafito yay garden dan dubo monkey shi.

Saida ta tsaya ta gyra hularta tamaida gashin ta da kyau ciki kafin ta shiga bangaren kanta akasa sabida wani irin kunya datake ji, babu kowa afalo hakan yasa tai stairs tafara hawa daidai lokacin big Mummy itama tafito daga dakin Baaba rike da bowl din fruits da fork tanaci "sannu da zuwa Mummy" wani irin faduwa gabanta yayi harsaida bowl din fruits din hanunta ya bare da sauri Bilkisu ta tsugunna tana kokarin tattare fruits din tace "subhanallah" bayanta big Mummy tabi da kallo ta rasa mesa duk idan taji muryar Bilkisu kokuma ta kalli fuskarta sai gabanta yafadi, dan murmushi tayi ta dagota tace "ki barshi keda bakida Ipy, wuce kitafi wurin Baabar ki gatachan ta shirya" badan tasoba tatafi.
[7/20, 11:39 AM] +234 803 238 4602: ♦♦ *SANGARTATTCE* ♦♦

Maman Abd Shakur

44 - 45

Ahankali ta turo kofar, Baaba ce kadai tanata faman daddanna touching screen wayar da Abba yasai mata tana ganinta ta ijiye tace "zonan tawaje na" harda dan gudun ta tafada kan Baaba sai kuka, cikin kuka tace "Baaba dan Allah karki tafi ki barni, dan Allah mukoma gida tare banason mutumin nan" girgiza mata kai Baaba tayi fuskarta ba alamun wasa tace "da auren akan ki, ai auren kenan, kifara zama dashi kafin ki tantance ko bakison shi yaron me halaye na gari haka, hakanan zaki daure kindaiga iyayen mijinki yanda suke sonki saiki bisu sau da kafa, kima mijinki biyayya inya kiraki kije karna karajin kince bakison shi" nan ta shiga yimata wa'azi mai shiga da ratsa jiki. Mami ce tashigo dakin da sallama tana murmushi ganin yanda Bilkisu ke kuka ta kankame Baaba tace "wanan kuka haka daughter kiyakuri kinji bagamu nanba" tashi Baaba tayi tana tureta tace "kinga sakeni nafara latti banison nai dare fa ahanya" tafita da sauri dan batason tai kukan da takeji, tashi tayi Mami tarike mata hannu tafashe da wani kuka sosai, hannu Mami tasa ta share mata hawayen tana murmushi tace "daughter nafa jaruma ce, dena kukan zomuje mumata rakiya" hijabi ta dauka tasaka suka fita sai uban kuka take mara sauti har waje, tsaye yake kusada Baaba sai magana suke wanda bata iyaji amma fuskarshi dauke da lallausar murmushi, budema Baaba kofar bayan mota yayi da gudu taje ta kankame Baaba tana wani irin kuka cirota Baaba tayi daga jikinta tana lallashi tanuna Ayyan dayay kaman bai gantaba tace "baga mijinki nanba kikema mutane kuka, ke dalla rabu dani karna makeki" Mami da Big Mum duk suka mata fatan alheri ancika boot da kayan atsaraba takaima yan zaria, ta kalli Bilkisu data kasa daina kuka ta shafa kumatun ta tace "Allah bada zaman lpy ki rike abinda nafada miki kinji" ta shiga motar da sauri tana boye kwallan daya zubo mata Ayaan yarufe motar yanama driver alama yatafi, tanaji tana gani Baaba ta tafi abinta tabarta. Batare daya sake kallonta ba yay wucewar shi wurin big Mum yace "big Mum yunwa nakeji" murmushi tai cike dajin dadi tace "muje nabaka abinci my boy" sukai wucewar su sukabar Mami daketa lallashin ta saida tai shiru sanan suka wuce part dinta.

Apalor suka zauna kanta akasa Mami ta kunna kallo tasa mata zee world tana janta da hira sai asanan tadan saki jikinta ganin haka yasa Mami tai sama dan akwai kiran datake so tayi. Kallonta take dudda rabin tunanin ta na gida, dan bawani gane kan film din takeba, yadade tsaye abakin kofa kafin ya shigo dakin fuskarshi adaure yana tafiya cike da izza, kamshin dataji yasa ta daga kai da sauri tana ganinshi ta mike tsaye da sauri zatai stairs da hannu ya nunamata kujeran data tashi gabanta na faduwa takoma ta zauna, Apple yadauka dake kan hadadden bowl asaman dining table sanan yadawo cikin falon shima akan kujeran ya zauna yadau remote din da Mami ta ijiye mata akusa da ita ya chanza channel zuwa na wrestling kafin ya kwanto ya daura kanshi kan cinyarta yana gutsuran apple din dake hanunshi yanaci, dudda yanajin yanda jikinta ke rawa hakan bai hanashi gyara kwanciya da kyau ba yanacin apple dinshi batare daya kalli fuskarta ba, stairs ta kalla dan ko kadan bataso Mami tazo ta gansu ahaka sanan ta kalli fuskarshi ta fashe da kuka tana share kwalla ko kallonta baiyiba, ahankali Mami ke saukowa daga stairs bayan tagama wayar datake yi da Ummu Haneef tsayawa tai chak hango Ayaan yanda ya daura kanshi akan cinyar Balkisu yana kallo abinshi girgiza kai tayi tajuya da sauri rashin kunyan Ayaan ya girmi tunanin ta wlh, bari baban shi yadawo yauyau dinan zata bashi matar shi sutai gidansu.

Kallon agogon dakin tayi ganin karfe uku kuma tun kafin azahar take dakinshi bataga yay sallaba yasa ahankali tace "anyi sallan azahar fa" sai a lokacin yadan birkito da kanshi ya kalleta ya daure fuska tamau yace "ke nakema sallan dama?" girgiza kai tayi atsorace yace "gud, to banga damar yiba nd u shut d f*ck up kona natsar dake" "daughter" daga sama Mami ta kwalamata kira ahankali tace "na'am" sanan ta kalleshi ganin baida niyar dagata yasa ta daura hannuwan ta akanshi ajiyar zuciya ya sauke wanda yasa ta tsorata ta janye hannuwan dan tazaci dukanta zaiyi, jin Mami takara kiranta nabiyu yasa yadagata tareda lumshe ido da sauri tamike tai sama da gudu yabita da kallo yana murmushin gefen baki, dakin Mami ta shiga da sallama kanta akasa, cup Mami ta mika mata tace "shanye wanan ina zuwa" karba tayi Mami ta tashi tafita daga dakin ahankali ta kafa cup din abaki ta shanye ta zauna akasa tana jiran shigowan Mami, ba'a jimaba tadawo da dan babban bowl dauke da farfesun kaza dayaji magani ajiye mata tayi tace "zoki cinye kafin ya huce" murmushi tayi dan wlh tanason kaza kafin akunyace tazauna akan gadon data ijiye mata tafara ci ahankali Mami kuma nawaya har taci iya cinta taji tai dam, Mami batare data yanke wayarba ta kalleta tace "idan ya isheki toki shanye roman tass" gyadakai tayi ta shanye roman kafin ta mike tsaye tafita daga dan kai plate din kitchen hada ido sukayi da sauri ta dauke kai ganin har lokacin wrestling yake kallo kenan la'asar ma baiyiba wanan wani irin dan iskan mutum ne, astagafurullah tace ta shiga kitchen ta ijiye kafin takoma sama dakinta ta shiga kasancewar bata salla yau tai zaman ta tana wasa da wayarta.
Koda daddare bayan Abba yadawo da Mami tasame shi da maganan abama Ayaan matar shi sutafi gida bakaramin murna da dadi yajiba, waya yadauka yakira Ayaan dake Part dinshi yazo itakuma Mami takoma ta shirya Bilkisu cikin wani hadadden lapaya maroon sanan tahada mata magunguna datace tadinga sha kullum kafin tarike ta takaita falon Abba, hadasu Abba yay yamusu wa'azi sosai sanan yakara bama Ayaan amanar ta, big Mummy ma tamusu Mami ma tamusu sanan suka rakosu har mota sai uban kuka take itadai yau tabanu Mamin datake gani taji dadi ma yanzu tafiya zatayi ta barta kuma gidan wanan mutumun, a motar shi suka sakata ya kunna motar yabar gidan yana murmushin keta. Ganin tana neman kashemai dodon kunne da kuka yasa yawani irin taka burki akan hanya arude ta dago kai da kakkausar murya yace "wlh koki natsu kona wurga ki kan titin nan na takeki na wuce" gum tayi ko tari bata karayiba harsuka kai gidan yay horn mai gadi ya bude mai ya shiga yay parking ya kalleta yace "wuce kitfita ke" adan tsorace tabude kofar ta fito tamaida mai tarufe hararan ta yayi sanan ya kunna motar yama mai gadi horn yana budemai yafita da gudu dan sauri yake club zaije su Fawaz tun dazu da Pops keta maganganun shi suke kiranshi, takai minti shabiyar a wurin kafin tai hadadden flat din da tagani ahankali ta bude kofa ta shiga tana kallon ko ina yanda yamata kyau yanzu itane agidan nan da wanan mutumin dako salla bayayi itadai rayuwa bata mata adalci ba wlh. Upstairs tayi tanata waige waige koda takai tarasa gane wananne dakinta saida taga akwatunan aure a saman wardrobe yasa tagane wanda take cikine nata. Ahankali ta zauna abakin gado tafashe da wani irin kuka zuciyar ta namata zafi maisa Isyaka zaimata wanan abin, ita yanzu bama fasa auren nata yake mata ciwo ba abinda yafi mata ciwo shine hadata da wanan mugun mutumin da akayi, dama taimako kan zama haka? Sosai take mugun jin kewan Baba su Raiyana da Layla Umma da mama, kankame filo tai tana kuka ga wani tsoro tsoro datake ji ahaka bacci yay awon gaba da ita.

Wuraren biyar ta farka sabida kiraye kirayen salla na farko dataji, bayin dakin ta shiga ta tsaya tana kallon ikon Allah gadai pampo amma bataga inda zata danna ruwa yafito ba tace "kodai sun manta ne basu sakaba" tabe baki tayi takoma wajen shower din shima haka babu inda zata danna ruwa yafito, kaman zatai kuka tafito ta zauna akan gado tana tunanin yanda zatayi, tafi 2min azaune kafin ta mike tsaye takara komawa bayin ta dudduba tap din ta lelleka jikinshi irin kodai itace take kauyanci bata iya budewa ba amma bataga abinda zata danna ko murda ruwa ya zuboba, shower ta koma tana dubawa shima bataga wani abu dazata danna yafito ba karkashin shower ta shiga dan taduba huji hujin ko wani abune halan kawai taji ruwa feesss ya sakko daga shower yana jikata batare data danna komiba wani irin ihu tayi tafito daga bayin tareda fita daga dakin gabaki daya tai stairs tana ihu har tana bigewa, tsaye yake a kitchen gaban coffee machine dagashi saidan garen wando daya tsayamai a cinya yana jiran coffee yayi yazuba a cup yaji ihunta da sauri yafita daga kitchen din, bama ta lura dashi ba ihu kawai take tana kallon bayanta tazo zata wuceshi tai hanyar fita daga falon yariko ta da sauri, ihu tai tareda kulle idonta gam tana kuka sosai tace "wayyo Allah na fatalwa ne agidan nan ko aljanu ku" ganin kaman ma bata hayyacin ta yasa ya fizgota yahada ta da jikinshi ya zauna akan kujera yana jijjigata kaman karaman yarinya ahankali yace "ke open ur eyes nine" hannu takara daurawa akan fuskarta tarufe da karfi jikinta ko ina na rawa, hannunshi yakai yacire hannayen nata daga fuska yace "nine bude idonki kigani babu kowa anan" ahankali ta bude idon ta sauke su akanshi saikuma tafashe ta kuka ta ririkeshi tana nunamai stairs waigawa yayi ya kalli inda take nunamai murya chan kasa yace "menene maiya jikaki haka?" kara fashewa tai da kuka tana kallon stairs din tace "aljanu ne adakina, na shiga bayi zanyi wanka naga ba'a gama gyaran bayin ba ansa tap but babu abin kunna tap din, shower dinma babu abin kunnashi shine danaje kara duba shower din da kyau kawai naji ruwa yafeso da mugun gudu akaina" tunda take maganan tana kuka yake kallon bakinta, dan dariya yay kadan kafin ya saukar da ita daga jikinshi shima ya mike tsaye ya kamo hanunta ya rike yace "zomuje ki gani" make mai kafada tayi cikin kuka tace "ni bazan kara komawa saman nan ba  da aljanune" wanan karan sosai yay dariya yana kallonta kafin yakara janyota yahada ta da jikinshi ya dauketa atsorace take kallonshi tana kuka sosai abayin ta ya direta yana dariyan yanda takara karfin ihun datake dataga sun shigo bayin tsayawa yay wajen wash hand basin din ya jawota yahada ta da jikinshi ganin zata kara fita ya nunamata tap din yace "proximity sensor tap ne" hanunshi yakai karkashin tap din saiga ruwa yafito yana janye hanunshi ruwan ya tsaya baki tasaki tana kallonshi, dan murmushi yay ya lakaci hancin ta yakoma wajen shower yana kara hanunshi karkashin shima ruwa yafito yace "kin gani ba aljanu bane, dazaran yay sensing abu nakusa dashi ruwa zai fito" dan murmushi tai a kunyace ta dauke kai dan sai yanzu ma ta lura baida kaya ajiki, dimple dinta ya kafe da ido kafin yadan matso kusada ita saikuma yay tsaki yawuce yafita, kulle bayin tayi harda saka makulli tai wanka ta wanke baki sanan tafito ta shirya cikin lace shirt white tasanya leopard water color maxi skirt bakaramin kyau tayiba, tai parking gashin ta donut tasaka dankun round bakaramin kyau tayiba jin yanda takejin yunwa yasa ta sauko kasa batare data tsaya shafa hodaba, afalon ta ganshi yana zaune kan kujera yana daddana laptop kallo daya tamai ta dauke kai dan bataga alamun yay salla ayanda ta ganshi dazu ahaka yake ma yanzu, kitchen ta shiga amma sai takasa abinda yakawo tai shiru kafin tafito kuma saida tafara hawa stairs incase idan yabiyota sanan ta tsaya batare data juyoba tace "lokacin salla yafara wucewa" "wat" yafada yana kokarin ture laptop din jikinshi ya mike tsaye da gudu

tai sama ya nunata da yatsa saikuma ya daki iska yace "hmm". Sama yakoma yay wanka yana shirin fita saikuma yakasa sabida yanda tambayar ta keda ringing aranshi, bayi ya shiga yadauro alwala yazo yay sallan asubahi sanan yadau car keys yafita.
[7/20, 11:39 AM] +234 803 238 4602: ♦♦ *SANGARTATTCE* ♦♦

Maman Abd Shakur

46 - 47

Bata sake haduwa dashi ba tunda ga ranan itadai kullum Mami na aiko mata da abinci taci takoshi abinta ciwonta ya warke rass ko kadan batajin ciwo.

Zaune take yau lahadi adakinta ita kadai tana gyaran kumba da nail cutter, tun asuba takejin tashin music daga dakinshi tanata mamaki wanan wani irin mutumne, tana sanye cikin doguwar rigar atampa na poker dot blak da pink, straight gown akamata dashi  akasa aljihu agefen rigar, sai kamshin turaren da Mami tahada mata takeyi, kanta ba dankwali tadaiyi parking gashinta ta kitse bakin daya sakko har bayanta takama jelar bakin da hair clip pink, wayarta ne yay ringing da sauri ta dauka ganin Mami ce bakaramin kewanta tayiba ahankali tace "ina yini Mami" daga dayan bangaren Mami ta amsa tareda tambayar lafiyanta sanan tace "tun dazu nake kiran Ayaan awaya amma number shi akashe ki kaimai wayarki zan kira nan bada jimawa ba" ahankali tace "to Mami" gabanta na faduwa kafin ta mike tsaye tabude kofar tafita daga dakinta rike da wayar, tsayawa tai abakin kofarshi tana sallama amma babu amsa, to ta inama zaiji wanan uban speaker dake tashi haka na waka, ahankali ta bude kofar dakin batare data shigaba wani sassanyar kamshi da sanyin Ac ne yamata sallama baki tabude cike da mamaki yanda taga ya tsaya gaban tv dakin ga home theater agefe yana tika uban rawa hanunshi rike da glasscup dake dauke da juice aciki, dagashi sai dogon wandon crazy  jean daya zazzago kasa da belt ke jiki, babu riga ajikinshi ga jikin nan amumurde sai kace wani commando, rawa yake yanabin wakan dake tashi na Burnaby da zlatan gbese yana irin rawan, dayake yajuya mata baya saisa baigantaba baki abude take kallonshi dan tunda take a duniyar nan bata taba ganin namiji na rawaba to a inama zata gani makarantar datayi mata zalla ne, ganin yanda yake chashewa abinshi yanayi yana shan juice din hanunshi yasa ta daura hannu akan baki tareda sake kwalalo ido dan dariya ke cinta ganin abun bambaram, kaman ance yajuyo ya juyo cikin rawa karaf suka hada idanu ko kulle belt din wandon baiyiba kunen nan makale cikin daimond dankunne sai shining suke, ga wata sarka a wuyarshi dake kyallin bala'i, kirjinnan kaman zai rabe biyu tsabagen yanda yaciko, numfashin ta yakusa daukewa sabida yanda suka hada ido ta juya da gudu zatabar wajen ya dakamata tsawa. "ke come back here" juyowa tayi amma takasa shigowa sabida yanda taga babu alamun rahama akan fuskarshi, wani irin kallon daya mata yasa ta shiga ciki da sauri tazo gabanshi ta tsaya kanta akasa tana kakkama rigarta tsabagen yanda tarude. "uban me kikeyi anan?" yamata tambayan dawani irin murya dayasa taji cikinta zai fara murdawa, girgiza kai tayi ta mikamai wayarta tana kokarin hadiye kukan datake ji tace

"Mami tace nakawo ma wayar wai zata kiraka" wayar ya kalla kafin ya watsa mata harara ya nunamata gaban tv stand yace "keep it there" da sauri ta ijiye wayar jikinta har rawa yake tajuya zata tafi taji yariko hanunta fashewa tai da kukan datake kokarin hadiye wa ta juyo atsorace cikin kuka tace "to menayi kuma" hadata yay da jikinshi ya watsa mata harara kafin ya daura hannunshi akan lips dinta alamun tamai shiru hadiye kukan tai da kyar ta share fuskar tass sanan ya saketa yabarta anan tsakar dakin yadau remote yadawo kan kujera yadaura kafa daya kan daya ya chanza waka zuwa wakar Mayorkun da kizz Daniel True ya daure fuska ya kalleta yace "dance" atsorace ta ware ido ta kallai ganin yanda yay da fuska yasa ahankali muryan ta har rawa yake tace "wlh ban iya rawaba" belt din dake jikin wandon shi yafara zarowa yace "kokiyi rawa ko kici dukan bala'i" yanuna mata belt din tare kara maida wakar tafara daga farko yakara volume dakin sai daukar duma yake shikuma yana kurban juice dinshi hankali kwance yana dan kada kafa, kaman zatai kuka ta daura hannu takama kwankwason ta sanan tadaura yatsu biyu agaban goshin ta tafara mai rawan yan fillo tana moving jikinta ahankali hawaye na zuba.

Wani irin kallo yake binda dashi yanda take wining tiny waist dinta, tun yana murmushin gefen baki har yay dariya daya bayyana duka fararen hakoran shi, ajiye glasscup din yayi akan hannun kujeran yataso rike da remote cikin murmushin dabaima san yanayi ba ya jawota jikinshi ya rungumeta tareda duko dakai ya daura kanshi akan gashin ta yana murmushi still ganin yanda take kuka ajikinshi, ahankali yace "you don't know how to dance bari na koyamiki" chanza wakar yay yasaka wakar ed sheeran perfect wakar soyayya ce, ahankali ya cirota daga jikinshi yana murmushi ganin yanda duk ta tsure yawani irin juyata kafin ya kwanto da bayanta jikinshi ya hade hannayensu ya budesu, sanan ya saketa ya juyo da ita tareda saka hannayenta akan wuyanshi ya daura hannayen shi a waist dinta yana wani irin tafiya da ita ahaka, ita wlh tsoro ma yake bata nishi kawai take tana ganin yanda yakebin wakar yana wani jujjuyata kaman yasami yar tsana, jin fuskarshi a wurin wuyarta yasa ta bude idanun data lumshe da sauri daukarta yay yawani shillarata sama kafin ya cabeta asaman yafara juya da ita sosai tafara ganin jiri hakan yasa ta rirrike jikinta ta dafe hannayenshi, sakinta yay kaman zata fadi hartai ihu saikuma yarike ta suka zuba akan center carpet din dake kasan dakin yana dan dariya, ringing da wayarta yayi yasa yatashi ya dauka tareda kashe wakar ganin Mami ce yay picking call din yana gaisheta, tashi tayi dudda uban jirin datake gani tazo zata tsallake kafarshi ta fita daga dakin taji yarike hanunta juyowa tayi ta kallai hada ido sukayi ya daga mata gira daya kafin yacigaba da wayarshi abinshi, dayan hannunta tadaura akan hanunshi tana kokarin bambare hanun kawai ya fizgota tafada kanshi matseta yay sosai ko numfashin kirki bata iyayi hakan yasa tai lamo hawayen wahala na zubo mata. Yana magana da Mami anatse ahankali, kadan kadan ma takeji meyake fadama Mami ahaka har bacci baccin wahala yasoma dibanta tana takure ajikinshi, "ke" tsawan dataji yay mata yasa tafarka afirgice tana neman sauka daga jikinshi amma baibata daman ba saima kara manneta da jikinshi dayay da kyau yana kallon fuskar nata. Tashi yay zaune har lokacin tana jikinshi tana sossosa ido da yatsa sabida gashin idon daya shigan mata, hannunta daya kama yacire daga idon yasa ta kallai da idanun dasuka kankance shima ita yake kallo hakan yasa ta janye idanunta ta sauke su kasa, tashi tsaye yay rike da ita kafin yadauke ta chak da sauri ta kallai itama shiyake kallo, jikinta na rawa ahaka har suka fito yasauka downstairs kitchen taga sun shiga saikuma ya bude kofar baya sai gasu a garden wurgata cikin swimming pool din da bama ta lura dashi ba yayi kawai, wani irin ihu tayi

Da gudu Munari tafito ta tara da Big Mummy turus agaban kofa ta dafe kai tace "waye ya jimu?" cikeda bacin rai Big Mum tace "mayyar matar shice, ban wayana da sauri kafin ta batamin plan" da sauri Munari ta koma sama Big Mum kuma takoma cikin falon tasaka hannu tadau glass bowl din decoration dake kan center table ta buga shi akasa ya tarwatse, runtse ido tayi da karfi ta sanya kafar haggun ta akai ta taka wani karami aiko ya yanketa saiga jini da sauri ta zauna akan kujera tana runtse idon azaba, daidai lokacin Munari ta sauko daga kan bene tana ganin jini tace "saratu kinada hankali kuwa" murmushi mai ciwo tamata tace "trust me i know wat am doing" karban wayan tayi tai dailing number Ayaan har lokacin busy yake yana driving yana magana da Dr Ibrahim sunma kusa gida, Bilkisu dukta damu yagama wayar sai kallonshi take, saida suka shigo anguwan su sanan ya katse wayar ya ajiye akan cinyarshi yadan kalleta suka hada ido kafin ya maida hankalinshi kan hanya yay murmushin gefen baki yace "ke kallon fa" kaman zatai kuka tace "dazu danaj..." wayarshi tai ringing big Mummy daya gani a screen yasa yace "1min" daukar wayar yayi daga tacan bangaren big Mummy tai wani irin murya tace "Boy kana ina?" dan murmushi yayi yace "gani nan a anguwan mu bama mukarasa gidaba, missing me already" yanda yay maganan yasa ta gane bai riga yasan komiba wani irin nishi tayi da sauri yace "menene are u okay" Munari ta kanne ma ido hakan yasa Munari ta fizge Wayan cike da tashin hankali Munari tace "Ayaan hawan jininta yatashi jiri ya dibeta ta fadi afalo yanzu hakama kafarta jini yake ta taka katoton kwalba, she's seriously bleeding, ka ajiye matarka agida kazo da wuri dan Allah" arude yace "okay okya, ki danne wajen try and stop d bleeding kafin nazo" katse wayar yayi daidai yakawo kofar gida yay horn mai gadi ya bude ya shiga ciki adan rude ta kallai tace "ina zaka i want to talk to you" fuskarta ya kalla saikuma ya matso yama lips dinta kiss murya chan kasa yace "ina zuwa, sauka ki shiga gida big Mum bata da lpy" da sauri ta girgiza mai kai, tsayawa yayi yana kallonta ganin zatamai kuka yasa yace "ke" a tsorace ta sauka yatada motar yafita daga gidan, yana fita wayarshi takara ringing ya dauka Munari tace "kataho kuwa yafaki tsayawa jinin" ahankali yace "nariga nataho inama hanya yanzu, idan akwai ice a fridge ki dauko kisa" da sauri ta katse wayar ta kalli Big Mummy tace "yariga yabar gida yafara zuwa" hannu Big Mummy tamika ta karbi wayar batare datama damu da kafarta da ke jini ba, wani number mai suna Bala naga tai dailing ringing daya ya dauka, anatse tace "ka kwashi boys dinka yanzu yariga yabar gidan kuje ku dauko yarinyar koma tayaya ne ku kaimin ita warehouse, tariga tasan secret dina baniso ta tonamin asiri, idan kun daukotan karka kirani kamini text" shiru tayi tana sauraron meyake cewa kafin ta katse wayar.
Tafi minti goma a wurin kafin tai cikin gida ahankali tana goge hawayen idonta, yanzu dama big Mummy dake sonshi haka dama bason tsakani ga Allah bane, dama itace ta haukatar dashi lallai duniya abin tsoro, dama anacewa makashinka yana tare dakai, kuma ma sabida dukiya take son kashe shi dukiyar banza, to yanzu idan tafadamai ma zai yarda da ita, da tunane tunanen nan takai dakinta ta shiga bayi tai wanka tafito ta shirya cikin rigan baccinta na doguwar riga mai kauri tai addu'an bacci ta kwanta tanata tunane tunane toko tamai text? Tunanin hakan yasa ta tashi zaune tsaki taja tunawa da jakarta dake dauke da wayarta na cikin

motar shi.

Da sauri ya shiga part din big Mummy rike da first aid box tana ganinshi tawani baje a kujera tana nishi ga kafarta na didduga da jini kadan kadan Munari na fititata. "subhanallah sorry Big mum" kafarta ya dauka yay treating kafin ya mike tsaye yadan duko saitin kan big Mum din yace "ina zuwa bari naje side dina na dauko abin auna BP" yana fadin haka yafita.

Har bacci yafara daukarta taji karan bude kofa sake shigewa tai cikin bargo tai lamo sosai kaman tana bacci dan karya mata komi ko yazo, taku dataji daban daban sanan anata bude kofofi yasa tadan bude ido dan wanan ba tafiyan mutum daya bane toko dai dawani yazo ne, wani irin bugo kofar dakinta da akayi yasa takara bude ido atsorace, Maza ne guda biyar sanye da bakaken kaya da bakake mask sun rurrufe fuskar su. "hasbunallahu wa ni'imal wakil" kawai take maimaitawa ta runtse idonta da karfi dan gani take kaman mafarki take yanda suka tsatsaya sun zagaye gadon suna kallonta da idanunsu tacikin mask, Babban cikinsu ne yawani irin fizgo hanunta hakan yasa ta fasa wani irin uban ihu wani irin mari ya sakin mata abaki batare dayace mata ko kala ba, aiko baki sai jini fashewa tayi da kuka tana tirjewa tace "dan Allah ku sakeni wlh ni banda kudin baku amma kudau kome kukeso" wani irin finciko hanunta dayayi saida hanunta yay kara yajata tana tirjewa yafita da ita daga dakin sauran hudun suka rufa musu baya, ihu take sosai. "na shiga uku Ya Ayaan, Wayyo Allah Babana" tutturjewa take yanajanta akasa hanunta yaja plate din dake kan center table din falon saman daidai sunkai wurin stairs zai sauka yana janta ta daddage ta mike ta kifamai kwanon akan hanun daya riketa dashi hakan yasa tai wuf zata koma daki daya daga cikin hudun da suke bayansu yasa kafa yawani irin tokareta aciki da baya tayi luuuuu tawani irin mugun faduwa a stairs wani irin wahalallen kara tayi kafin tafara tumble tumble tumble har takusa kai kasa sai kuma kanta yay wani irin landing da buguwa a karfen stair case din, ko kara bude idonta batayi ba tasume warwas sai jini dakebin kanta yana zuba a stairs din.

Daidai lokacin ya shigo part din big Mum rike da abin auna Bp dan yadade yana nema baisan inda ya ijiye ba, wani irin faduwa gabanshi yayi da baisan lokacin daya saki abin auna BP hanunshi ba yafadi akasa, daura hanunshi yay akan kirjinshi yay shiru, Big Mummy tadan dago dakai ta kalleshi kaman mara lafiyan gaske tai magana ahankali tace "Boy lafiya zoka dubani man" sake danne zuciyar shi dake bugawa sosai  sanan ya kalli Big Mum, abu yaji yana gangaro wa daga hancin shi ahankali ya kai hannu yataba yaga jini, da sauri big Mummy tace "ur nose is bleeding boy" kirjinshi yakara tabawa dake bugawa sosai yace "Big Mum she's not fine, i can sense it, my heart is telling me" da sauri ya juya yace "am coming" da saurin shi yafita daga dakin Big mum na kiranshi ya shiga mota yay horn yafita daga gidan dawani irin azababben gudu hancinshi na jini.

Dayan daya rikota ne tun farko ya fizgo wanda ya tokaretan sai a lokacin yay magana yace "dan uwarka ance mutaba tane?" tureshi yay da karfi ya sauka suna biye dashi abaya, daukarta yayi ya sabata akafada gatanan kaman mara rai kanta na diddiga da jini suka fita daga dakin ya wurgata acikin bakar van din dasuka shigo da ita compound din, daya daga cikin su yay gudu yaje yabude musu gate yana kallon mai gadin da har yanzu yake asume suna fita ya bisu ya

shiga motar sukabar anguwan da mugun gudu gate din gidan abude.
[7/25, 9:18 PM] 0mmer Farouk: ♦♦ *SANGARTATTCE* ♦♦

Maman Abd Shakur

61 - 62

Ko parking bai gama yi da kyau ba awaje yafito yana kallon gate din gidansu dako rufewa ba'ayi da kyau ba, runtse idonshi yay da mugun karfi kirjinshi na wani irin bugawa kaman ba gobe, da kyar ya iya daga kafan shi daya mugun yimai nauyi ya shiga ciki, da mai gadi yafara cin karo azube kaman baya numfashi ga fuskarshi dukta kumbura sabida naushi, wani irin bugawa kirjinshi yayi ya karasa ya tsugunna ya sauri yana duba pulse dinshi ganin he's still alive suma ne kawai yasa yay reviving dinshi sanan da gudu yay cikin gida, jinin daya gani a stairs yasa heart dinshi ke wani irin mugun racing da mugun gudu, yay sama yana kallon plate dake kasa sanan ga dakunan su duk abude, dakinta ya shiga da gudu babu kowa, wani irin mugun bugawa kirjinshi yayi kaman zai fashe da sauri yabude bayi ya shiga nan ma ba kowa, da gudu yasake fita kaman mahaukaci ya shiga dakin shi da bayin shi bakowa yasake fitowa da gudu ya shiga dayan dakin bakowa, yafito yay kitchen ba kowa ya shiga store bakowa, yafita yay garden bakowa, dawowa falo yayi yana jujjuya wa yana kallon ko'ina amma bakowa, kanshi yawani irin rike da hannu biyu kafin da bude baki da karfin bala'i yace "Bilkisssssss" yawani irin zube akasa ya rirrike jikinshi dake wani irin mugun rawa kaman mai farfadiya, da gudu yafita yay inda mai gadi yake arude ya dauko ruwa ya yayyafa mai hakan yasa yabude ido gabaki daya da sauri ya dagoshi da idanunshi dasukai jarababen ja muryan shi har bata fita da kyau tsabagen bala'i yace "me..me..meya...meya faru?" Mai gadin da biyu biyu yake gani da kyar yace "wasu mutane su biyar sukazo amota sun rufe fuskokin su, suka dakeni sukai cikin gida daga nan bankara saning meya faruba daga nan ba" Gabaki daya jikinshi rawa yake kokarin ma saita yanda zuciyar shi ke bugawa yake sabida karya samu heart attack, da kyar ya mike tsaye yana dafe zuciyar shi yana runtse ido kanshi na juyawa da kyar ya iya ya lalubo waya bama yagani da kyau ya lalubo number Abba yakira ringing biyu Abba dake kan dadduma yagama shafa'i da wuturi ya dauka yace "Boy" da kyar ya iya bude baki yace "p...pops kazo" zumbur Abba yamike daga kan dadduma jin yanda muryar shi ke fita da kyar tana breaking, Mami dake kwance ta bishi da kallon mamaki, arude yace "Boy are u okay, menene, talk to me Boy, u don't sound like u, menene?" da kyar yace "Pops Bilkis, an, ban..ban ganta ba..an dauke..." tsabagen yanda jikinshi ke rawa ma wayar tazame tafadi akasa ta tarwatse, Abba yace "boy, boy" kallon wayar yay yaga ta yanke, Mami tace "menene ba yanzu nan yabar nan ba bayan yay treating kafar hajiya baima tsaya ya auna BP taba fa haka Munari takece min" girgiza kai Abba yayi yace "sako hijabi ki sameni akasa, Boy doesn't sound gud something is wrong" yana maganan yana fita Mami tadau babbar hijabin ta saka ta bishi abaya, Big Mum suka gani tana dingisawa tana zuwa sanye da hijabi hanunta rike da plate tana ganin Mami da Alhaji tace "ina zaku haka nida nazo na debi fruits a fridge nawa ya kare" Mami tace "ga Alhaji nan shinake bi wai Ayaan ba lpy" arude big mumy ta kalli Abba tace "meya sami Boy Alhaji? Mutafi mutafi mugano danmu" gaba Abba yayi suna biye dashi Big Mum ta kalli Mami tace "kedai wlh Allah wadaran halinki

Ayaan baida Ipy ne shine wai Ayaan" direba Abba yakira ya shiga duk suka shiga aka jasu sai gidan Ayaan.
Yanayin parking motar Ayaan dasuka gani awajen yasa Abba yacema driver yay parking duk suka sassauko Abba ne yafara shiga tsakar gidan ko lura damai gadi ma baiyi ba sai Ayaan daya hango a tsugunne jikinshi nawani irin rawa uncontrollably, da sauri Abba yay kanshi yana "Boy, Boy" dago shi Abba yay yay cupping fuskarshi, hanun Abba yakama gam gam yarike da kyar ya bude baki yace "Pops where is mah wife?" hanunshi Abba yakama ganin kaman ma baya hayyacin shi yay cikin gida dashi yana binshi luuu su Mami suka bisu abaya hankali tashi, shikuma direba ya taimaka ma mai gadi ya shigar dashi dakinshi ya kwantar dashi yanamai sannu.
Zaunar dashi Abba yayi yana kallon jinin daya ga a stairs bakinshi na furta "innalillahi wa innalillahi raji'un" Big Mum tafashe da kuka sosai ya kalli Mami datai shiru tana kallon Ayaan da jikinshi ke wani irin rawa hancinshi jini na zuba yace "ban ruwa Firdausi, mara sanyi" da sauri Mami tai kitchen ta dauko goran ever mara sanyi ta bude ta mikamai Abba ya karba da hannu daya dayan hanun nakan kafadar Ayaan yakai goran bakinshi yana tofamai addu'o'i, Kukan da big Mum keyi yasa Abba ya dakama ta tsawa akule yace "ke kokimana addu'a kokiyi shiru" yasama Ayaan goran abaki ya tsiyaya mai ruwan da kyar yasha sanan yadawo kusa dashi ya zauna ya kwanto dashi yadaura kanshi akan cinyarshi yana kara  tofamai addu'an ko jikinshi zai dena rawan, kafin yaciro wayarshi daga aljihu number governor kano yakira gabaki daya, ringing biyu gwamna da kanshi da dauka, Abba yamai explaning abinda ke faruwa.

Within 15 good minutes karan motocin police kakeji suna shigowa anguwa, ansace matar da tilo ga Abdulrasheed Gwanaye ai dole gwamna dakanshi ya turo polisawan, tundaga waje CP yafara saka team dinshi bincike wasu na interrogating mai gadi daya farfado kafin yazo da kanshi har bakin kofa yay sallama Mami tabashi izinin shigowa shida wasu manya police guda uku suka shigo ya tura biyu dake tareda shi sama bincike sanan ya zauna kusa da Abba dake ma Ayaan dahar lokacin bai dawo daidaiba addu'a, saida Abba ya idar sanan ya nisa yace "Alhaji naga akwai CCTV camera a compound din" sai a lokacin ma Abba yatuna yace "harda ma falon nan akwai" IG yace "ina computer to zanzo mu kalla dan musan meya faru" da kyar ya mike tsaye Abba ya rike shi yace "Boy" gyada ma Abba kai yayi da kyar alamun zai iya, Abba yarike shi sukai sama IG nabiye dasu abaya, Mami da big Mummy ma suka bisu, wani daki sukaje nan suka tariyo computer har zuwa daidai inda goons din sukazo sukai horn mai gadi yafita waje dubawa sai gashi daya daga cikin su sanye da mask ya shigo da mai gadi yana dukanshi kafin ya sumar dashi ya bude musu gate bakin van din ya shigo, pursing video IG yayi ya rubuta plate number motar down sanan ya danna play suka cigaba da kallo gashi sun shigo sun fiffito daga motar sunyi cikin gidan sun bude kofa sun shiga falo sukai upstairs, dayake babu CCTV a sama basu ga maiya faru ba saidai ihunta dasuke ji da lokacin datake kiran Ya Ayaan, runtse idonshi yay da karfi wasu hawaye masu bala'in zafi suka zubomai da sauri ya share, saikuma inda daya daga cikin su yasa kafa yatokare mata ciki tafado ta fasa kai wani irin dunkule hannu yayi zai daki computer da sauri IG ya rike shi calmly yace "be strong Man, i know how u feeling, zamu kamasu idan ma kidnappers ne dan basuyi kama da yan fashi ba, inda yan fashi ne da sata xasuyi, indai har kidnappers ne zasuyi contacting dinku, so u people should stay alert zasu iya kiranku kowani lokaci, yanzu dai one good thing is zamu nemo motar

nan tasu ta hanyar plate number nan koma ina motar take a fadin kanon nan, sanan Alhaji" ya kalli Abba yace "yakama ta yanzu akwai body guard dazasu dinga yawo da family ka most especially ur son, yanzu dai zan koma office zan zuba team dina akowani hanya da express way na barin garin kano zamu kamasu da izinin Allah, one last thing is i need hoton ta, dan nan CCTV footage fuskar ta is not clear sosai dan musa a media incase idan wani yagan ta" Da sauri Abba ya kalleshi yace "kanada hoton ta Boy kabamu?" saida yarike hanun Abba sanan ya iya magana da kyar yace "yafashe" Abba ya kalli Cp yace "wayarshi tafashe dazu amma zasu samo hoto bari yadawo daidai tukun" ajiyar zuciya cp ya sauke yace "shikenan we will use dis for now, please take care of him he doesn't look good" yanuna ma Abba Ayaan sanan yawuce yafita daga dakin, da taimakon Abba suka fito sabida jirin dayake ji sosai suka zauna afalon sama ya daura kanshi akan kafadar Abba shi kadai yasan yanda yakeji, Abba sai addu'a yakemai jin yanda zuciyar shi kewani irin rawa, tashi Big Mum tayi ta kalli Mami datai wani irin tagumi daurewa kawai take danji take kaman tai ihu tace "bare na shiga bayan gida" gyda mata kai kawai Mami ta iyayi tai shiru tana tunani abu kaman mafarki Bilkisu da dazu dazun nan tana tare da ita, da dingishi Big Mummy ta shiga dakin dake kusa dana Bilkisu ta maida kofar ta rufe, bayi ta shiga ta rufe sanan tafito da wayarta daga zani wacce tuntuni ta maidata silent, message din Bala tagani da sauri tabude;

“hajiya mun dauketan muna warehouse din saidai fa, Ahmad ya bugeta sabida gardaman dataso tamana kanta yafashe har yanzu bata farfado ba”

Da sauri big Mummy tamai reply

“Bala bakace min gobe zakaje Bauchi ba, inaso da daddaren nan kudau hanyar Bauchi kunemi wani daji achan ku karasata kuyar, sabida yanzunan za'a baza police ako ina agarin nan, banason ko gawanta su tsinta agarin nan, ka tabbatar bata numfashin daga yanda nake ganin yaron ma dazaran ta mutun shima rayuwar tashi karewa zatayi, ka tabbatar kunbar garin nan yanzu, yanzunan zakaji alert din kudi, kudin aikin ka kuma saina tabbatar kai komi da kyau sanan zan biyaka miliyan goma, kubar garin nan yanzu, i repeat yanzu! ". Tura mishi dubu dari tayi sanan ta kashe wayar gaba daya ta wanke fuskarta tafito daga bayin tadawo ta dayan gefen Ayaan ta zauna tana tofamai addu'a tana matse kwalla, ahankali Mami ta tashi ta dauro alwala ta shiga daya daga cikin dakunan tafara salla.

Bala na ganin text dinta ya kinkimeta yasata amota sauran ma suka shiga suka bar gidan.

Shigowa dakinshi Abba yayi dauke da cup din coffee da Mami tahada mai, yana zaune ya jinginar da kanshi a bangon gado ya lumshe ido, lokaci daya wani irin hadadden zazzabi ya sauko mai, zama kusa dashi Abba yayi yana dafe kafadar shi tareda ijiye tea akan bedside drawer ahankali yace "Boy" fadawa yay jikin Abba murya chan Kass dake rawa sosai yace "Pops please bring her back, Pops dan Allah kace sudawo min da ita konawa suke so zanbasu or they should take me instead" ba karamin tashi hankalin Abba yayiba bayason abinda zai tabamai Ayaan, Ayaan nada mugun rauni akan abinda yakeso wanan tun yana karami yasan da haka, wlh koma su waye suka dauke Bilkisu sai yasa hukuma tamusu hukuncin daya dace dasu, daga kanta bazasu sake marmarin dauke wani arayuwar su ba. Ahankali yace "i promise u, Boy i promise you, ko ina ma suka kaita saimun nemota, even if it takes nai hiring private

investigator, even if it means putting all i habe at stake saina nemo ma matarka, i promise u Son, don't worry wanan alkawarin baban kane" sake kankame Abba yayi sosai saiga hawaye shar sun zubo da kyar yace "Pops they hit her, she's hurt, kanta yafashe, Pops he dare hit mah wife wlh saina ka.." hawaye yahana shi karasawa, yafashe da kuka ahankali yana shesheka ajikin Abba, bakaramin damuwa Abba yay ba rabon daya ga kukan Ayaan tun yana grade1, haka yadinga lallashin shi, ranan yanda sukaga rana haka sukaga dare dan wani irin ciwo ne da mugun zazzabi yarufe Ayaan sosai, koda gari yawaye baya gani da kyau tsabagen zafin zazzabin Mami takira Dr.

Wuraren biyar na yamma suka shigo garin bauchi sundanyi tafiya mai nisa kafin suyi parking agaban wani daji, wani babban buhu daya daga cikin su ya dauko yazo inda take kwance kaman matatta dan sunma dauka ta mutu ne, ya bude bakin buhun da kyau biyu daga cikin su suka ciccibeta suka sakata aciki suka kulle bakin buhun sanan wanda ke tukin yafito yazo tabaya ya bude musu suka daukota da sauri sukai cikin dajin da ita da saurin bala'i. Jogging din daya sabayi kullum da yamma tunda yazo farm house din Abban shi hutu yauma yafito yanayi, sanye yake da singlet din sport mai ruwan toka da dogon wando shima mai ruwan toka kafanshi sanye da bakin sport shoe sai kanshi acikin head phone yana jogging abinshi tunda idanunshi suka sauka akan bakin van yaji baida natsuwa, barin ma lokacin dayaga sun fito dawani babban brown sack sunyi cikin dajin dashi hakan yasa yaji bai yarda dasuba, labewa yay abayan wani bishiya har suka fito duk yana kallon fuskar su kafin yaga sun shiga cikin van din sun tada sun tafi, da sauri yay cikin dajin daidai ta inda yaga sun fito yasa hannu ya janye headphone din daga kanshi ya maida wuyanshi sanan ya cigaba da tafiya da sauri sauri yana shiga dajin yana kalle kalle amma baiga buhun ba har yay giving up yana shirin ya juyo yaga buhun akan wani babban dutse da sauri yay wurin yana addu'a, ahankali yay bismillah ya daura hannunshi akan buhun yana tattabawa jin kaman mutum yasa yay maza ya kwance daurin bakin buhun da kafafun ta yafara cin karo, ahankali hanunshi na rawa yay bismillah ya daura akan feet dinta kafin yadan dago takan ya zare buhun gabaki daya daga jikinta, yabi jinun daya bata goshin ta da kallo, da sauri ya kamo hanunta yana checking pulse dinta ganin akwai yasa yagane da ranta, da sauri ya ciccibeta yana kallon fuskar ta kaman yay kuka yafita daga dajin da mugun gudu baxai ma iya komawa farm house ya dauko car ba hakan yasa ya tare wani me machine din dake zuwa yahau kai yace kai ni town hospital. Yana zuwa hospital wani babban abokin shi mai suna Dr Ameenu ya karbeta aka taru akanta.

*Kano*
Ayaan fa gashinan gashinan ne, kaman zararre kaman lafiyayye baida aiki se sumbatun kiran sunan Bilkisu kokuma yadau filo yarike yanama filo magana, Abba yay yay dashi sukoma gida yaki ya makale adakin Bilkisu anan yake kwana yarike kayanta gam ya rungume yana fadin am sorry, am sorry, please come back. Big Mum dadi kaman zai kasheta har addu'a take Allah sa bakin cikin rashinta yasa yama mutu gabaki daya yanda dazaran Alhaji shima yamutu ta rike dukiyar gam gam.
Babu wanda yataba kawo tanada hand abacewar Bilkisu, anjira anjira yan kidnappers din sukira

amma shiru.

Yau satin ta biyu a hospital din, kullum Guy din daya kawota yake zuwa dubata duk wani kudi da akai bukata na treatment dinta zai biya.
Yauma kaman kullum misalin karfe biyar yay parking motar shi a parking lot din asibitin ya fito yana sanye da farin lallausar yadi daya haska chocolate fatar shi, sai uban kamshi yake yay cikin asibitin yana taku daidai yana kada key mota daya rike yay office din Dr Ameenu kai tsaye, Dr Ameenu na ganinshi ya nunashi da yatsa yace "kaiko Aaman sai shegen gayu babu matan aure tuzurun banza kawai" tabe baki yayi tareda fizge cold bottle water dake hannu Dr ya zauna akan kujera saida yadan sha ruwa kadan sanan yaja tsaki yace "sabida kadanyi aure last month ne zaka faramin iskanci, lallai muma Allah bamu masu sonmu" yay magana yana shafa dan gajeren gemunshi sanan yaja wata yar siriruwar tsaki agajiye yace "ya patient dina har yanzu bata tashi daga coma bawai" gyara zama Dr Aminu yayi yace "i think rashin tashin ta has something to do with buguwan kanta, but once ta tashi we will conduct some special test akanta, but let's just wait till then" ahankali yace "okay" kafin ya mike tsaye dauke da ruwan goran a hanunshi yace "bari naduba ta" yafita daga office din dakin dayasa asata na mutum daya yaje ahankali ya bude kofan ya shiga yana kallonta har yanzu tana kwance as usual cikin kayan asibiti da nurses suka saka mata bambamcin kawai yau babu oxygen din da aka saba samata, kanta nannade da bandeji, kujera yaja ya zauna yadan kalleta nayan mintina kafin ya jingina goran ruwan daya dauko a jiki ya tura hanunshi acikin aljihu ya ciro wayarshi yana daddannawa. Motsin dayaga bargon da aka lullube dashi nayi yasa ya tsaya da danna wayar dayake yi ya dago kai ya kalli fuskarta, motsin dayaga saman idonta nayi yasa yadan matso da kujeran shi kusa da gadon yana kallonta batare dayace komiba, motsin data fara sosai yasa yay magana cikin calm voice dinshi yace "Hey open ur eyes, u are safe now" motsi tacigaba dayi kafin ahankali tabude idonta suna rawa harta bude duka ta saukesu akan fuskar wani mutum data gani yana kallonta ga cool murmushi akan fuskar shi, dakin tabi da kallo tana jujjuya kai tana wani irin fir fir da ido kafin idanunta su sauka akan goran ruwan data gani akan jikinshi da sauri ta yunkuru zata tashi da sauri ta dafe kanta tasaki wani irin kuka, da sauri yadan matso yace "careful" da karfin tsiya ta tashi zaune ta fizgo ruwan data gani ajikinshi tana dambe da ruwan tana kokarin budewa amma takasa hakan yasa ya tsaya yana kallonta, fashewa tasake yi sosai da kuka tana dafe kanta dake mata zafi, ahankali ya mika hannu ya karbi ruwan zata fizge ya girgiza mata kai ya bude marfin ya mika mata, karba tayi da sauri ta kafa abaki wani irin mugun kishi takeji, daidai lokacin aka bude kofar dakin afirgice ta saki ruwan hanunta tai wani irin ihu da yasa ya kalleta da sauri dan dama kofar ya kalla sanin either Dr ko nurse ne zasu shigo, tsalle tayi ta diro daga gadon ta labe abayan shi tafashe da kuka tana bobboye wa, da sauri Dr Aminu ya karaso da murmushi kan fuskarshi yace "wow alhamdulillah at long last yaushe ta farka Aaman?" matsawa yayi sabida Dr ya ganta da kyau tasake biyoshi ta labe abayan shi, ahankali ya juyo hanunshi daya cikin aljihun shi ya nuna Dr Aminu yace "he's ur doctor zoki zauna" ya koma ta wurin gadon da sauri ta sake bishi ta tsaya a inda ya tsaya tana tana kallon fuskarshi hakan yasa yama Dr Aminu kallon irin wats wrong with her dinan, singnal da hannu Dr Aminu yamai hakan yasa yakara kwantar da murya ya nuna mata gado yace "sit" makemai kafada tayi, hakan yasa ya zauna abakin gadon da sauri itama ta zauna tana kallon fuskarshi, dan murmushi yay mata yace "sunana Barrister Aaman Muhammad, nina ganki

lokacin wayansu sun shigar dake daji acikin buhu sun yar, now i need you to tell me who you are sabida mu kira iyayen ki suzo su dauke ki, Ya sunanki?" tunda yake maganan ta kafeshi da ido ko motsi batayi, anatse yace "ya sunanki?" nuna kanta tayi akaro na farko tai magana cikin siririyar muryarta tace "ni?" gyada mata kai yayi ahankali tace "nima bansani ba, ya sunana?" ta wurgamai tambayar itama tareda tsareshi da ido tana kallon fuskarshi, da sauri ya kalli Dr Aminu, dan matsowa Dr Aminu yayi hakan yasa ta matsa kusa da Aaman da sauri hartana neman bigeshi da sauri ya matsa, ganin haka yasa Dr ya tsaya batare daya karaso ba ya kalleta yace "fadama na waye baban ki to" da sauri ta nuna Aaman, kallan kallo daga Aaman har Dr Aminu sukayi hakan yasa Dr yace "wanan bashine baban kiba, waye Maman ki to?" sake nuna Aaman tayi, ahankali Dr ya kalli Aaman yace "muje office" yay gaba Aaman ya mike tsaye da sauri itama ta mike ya kalleta yace "jirani ina zuwa" makemai kafada tayi kaman yarinyar tafashe da kuka da sauri ya kalli Dr Aminu daya tsaya ya kallesu yace "wai meke damunta ne?" ajiyar zuciya Dr Aminu ya sauke yace "inhar abinda nake tunani hakane inaga nin sanadiyar injury data samu akai yasa tasami shafewan kwakwalwa, ma'ana she lost her memory saisa kaga kaida tafara gani tasani take yarda dashi, yanzu u are her everything kai zaka koya mata sabawa da yarda da mutane for now kafin mu dubata musan wani treatment zamu daurata akai".
♦♦ *SANGARTATTCE* ♦♦

Maman Abd Shakur

63 - 64

Dan juyo dakai yayi ya kalleta nayan sakanni yana nazarin abinda Dr yafada, gashi tawani labe abayan shi tana wani zazzaro ido, yujawa yayi ya kalli Dr Aminu yace "Man come and examine her please" ya matsa gefe da sauri tasake binshi kaman zata shige jikinshi hakan yasa ya juyo da niyar mata masifa ganin yanda take kallonshi yasa yakasa ya nuna mata bed yace "sit" make mai kafada tayi kaman zatai kuka tana shafa cikinta tana kallonshi da sauri ya dauke kai yace "menene?" da kyar tace "yunwa" juyo dakai yayi ya kalleta yace "sit lemme get food for you" zama tayi ya juya zaiyi wajen Dr Aminu daketa kallonsu da gudu ta mike ta bishi hakan yasa ya tsaya chak tareda juyowa, shagwabe mai fuska tayi Dr Aminu yace "u know something, sata ta zauna na dubata tukun" baice mata komiba yay wurin gado ya zauna abakin gadon da sauri itama tabiyo shi ta zauna abakin gadon tana haki, Dr Aminu yadau stethoscope daya ijiye akan fridge din dakin ya maida wuyan shi yana zuwa wurin su, ihu tayi ta koma kusa dashi sosai ta rikemai riga da hannu daya tana nuna Dr da hannu daya, ahankali yasa hannu ya fizge rigarshi data rike da kyar yace "hey calm down" ya mika hannu ya riko Dr Aminu yace "he's my friend, babu abinda zai miki, Dr kine so don't be afraid okay" gyadamai kai tayi tana kwalalo ido tana kara mamatso wa kusa dashi, saida ta rike hanun rigarshi gam gam sanan tabari Dr Aminu ya dudduba tareda cire mata bandejin kanta ya chanza zuwa plasta yasa adaidai wurin ciwon sanan yay mata murmushi ganin yanda take yatsine fuska alamun zafi yace "wai Barrister zaka

sha aiki anan wlh" yadau byro yana rubuce rubuce sanan ya mikama Aaman, fizge hanunshi yayi ya mike tsaye da sauri itama ta mike ya karbi takardan, Dr Aminu yace "zaku iya tafiya da ita na sallame ku, memory loss dinne dai banda haka brain dinta yabugu dan haka zakaga tana abubuwa sai ahankali, yanzu dai ran Wednesday zaku dawo ranan ne likitan brain din asibitin nan ke zuwa zai dubata nasan zai mata memory loss test sabida ya gane if long term memory loss ko short term ne, tasamu daganan saiya daurata akan medications in sha Allah she will be fine, but u need take extra care of her gaskiya" shiru Aaman yayi yana kallonshi ko motsin kirki yakasa, ahankali Dr Aminu ya dafashi turo baki tayi tasa hannu ta ture hanun Dr Ameenu daya daura akan kafadar shi dukansu atare suka kalleta, turo baki tayi tana kallon Dr saikuma ta kalli Aaman ta washe mai hakora da sauri ya dauke kai ya kalli Dr, Dr Aminu yace "i know wat u are thinking amma karka damu duk mai taimako baya tabewa, dazaran ta warke saika kaita wajen iyayen ta kaga yanzu idan ka barta wat if mutanen dasuka so kasheta sukazo suka karasa ta? Gwara ka tafi da ita chan farm house din for now inyaso ai zaka iya kiran gida chan Abuja Ummy tazo hutu, nasan kuma Abba zai barta tazo, in yaso saita tayaka kula da ita idan zakaje site, u can go now buy this drugs for her kabata abinci taci kuma she need it" dan ajiyan zuciya ya sauke saikuma ya kalleta yanda dogayen kitso guda biyun da wata nurse tamata sabida ciwon dake kanta ke lilo tana kusa dashi takara washemai baki da sauri ya dauke kai ya kalli Dr yace "ina zamu samu hijabi" shiru Dr yayi kaman mai tunani sai chan yace "i think inada hijabin Maryam a office dina bari na dubo na kawo muku" da sauri yafita hakan yasa tawani irin juyar dakai ta harari kofar tana turo baki ta gefen ido ya kalleta abinma mamaki ya bashi, zama yayi akan gadon yaciro wayarshi yana daddana wa, da sauri ta zauna tana kallon wayar, hannu tasa ta fizge wayar da sauri ya dago kai ya kalleta nunamai wayar tayi saita boye abaya tana makemai kafada, abinma dariya yadan so bashi hakan yasa yay mata murmushi 4 d first time, ware ido tayi saikuma ta ijiye wayan akan gado ta mike tsaye tana tafa hannu sosai tace "yeeeeee" dan girgiza kai yayi kawai yace "funny" yadau wayar ya maida aljihu, ana bude kofa ta dawo kusa dashi ta zauna da gudu, Dr ne ya shigo dakin rike da maroon hijab ya mikama Aaman ganin yanda taketa murguda mai baki, karban hijabin yayi yace "thank u" ya mika mata hijabin da sauri ta karba tana jijjiga hijabin tana dariya kaman taga kayan wasa, ganin batama san meba yasa ya fizge ya warware ya saka mata kallon kanta ta dingayi tana jajjjan hijabin tana kokarin cirewa hakan yasa ya girgiza mata kai yace "No karki cire" da sauri takara tambayar shi "karna cire?" gyada mata kai yayi itama da sauri ta gyadamai kai, slippers yabata tasaka sanan yay hanyar fita Dr nagaba, da sauri tabishi suka fita a pharmacy ya tsaya ya saimata maganin duk tana kusa dashi tana kallon fuskarshi sanan suka wuce har wurin mota ya bude mata ya nuna mata ta shiga, ta shiga ya rufe ya zagaya duk tana binshi da ido sanan ya ahigo ya tada motar sukabar asibitin.

Cikinta ta rike ta hijabi tana shafawa tana tabe baki kaman mai shirin kuka tana kallonshi, ganin hankalinshi nakan tuki yasa ta kece dawani irin shegen kuka da sauri ya juyo ya kalleta yace "menene?" wani sabon kukan takara kecewa dashi tace "yunwaaa" da sauri yace "okay okay dena kukan, zakici apple?" gyadamai kai tayi hakan yasa yay parking abakin hanya daidai wajen masu saida fruits yasai mata apples dayasa aka wanke mata ya biya ya mika mata karban ledan duka tayi da sauri ta ciro daya tafara ci tana murmushi, kallonta yayi da sauri ta dago dara daran idanunta ta kallai washe mai baki tayi tasa hannu taciro katoton data balla

yake cikin bakinta taciro ta mikamai da sauri ya girgiza kai yace "no bazan ciba" wani irin ihu tayi, ta kece dawani irin kuka da sauri ya mika mata hannu yace "okay okay, sorry karki yi kuka bani to" sakamai tayi ahannu tana washe baki kaman ba ita take ihu da kuka yanzun nan ba, ya karba yana dan murmushi kafeshi tai da ido tana jiran yaci tareda shagwabe fuska ahankali tace "ci" kallon Apple din yayi yanda yay dama dama da miyau sanan ya kalleta yanda ta tsareshi da ido, dan murmushi dole yasake yimata yay yunkurin kulle hannun, wani irin ihu datayi wlh saida ya firgitashi dan mutum ne shi marason hayaniya tawani irin fashe da kuka tace "ci" baisan lokacin daya hadiye apple dinma, tafashe da dariya tana kallonshi tacigaba dacin apple dinta shikuma ya kunna motar ya cigaba da tafiya har gidan gona, bishiyoyi kala kala da shuka ne daban daban, ta gefe kuma wani flat ne kwara daya babba sosai, parking yayi yafito ya zagayo ya bude mata da sauri tafito tana waige waige rike da apple dinta ahannu, gaba yayi hakan yasa tabishi da sauri ya bude kofa ya shiga, babban palour ne dayasha kujeru sai tv bango akan dogon kujera ya zauna hakan yasa itama ta zauna kusa dashi da sauri tana kallon fuskarshi, shima ita yake kallo saikuma yaciro wayarshi yay dailing number wani mai kula da kajinsu ahankali yace "Umar dan Allah turomin Zainab" katse wayar yayi ya ijiye ya tashi, da sauri itama ta tashi dan juyowa yay ya kalleta saikuma yay Jim yacigaba da tafiya abinshi, kitchen ya shiga tana biye dashi tea yahada mata mai kauri a cup yadau slice bread ya shafa mata butter ya daura mata akan plate ya dauko ya juyo ya kalleta ganin yanda take kallonshi tana kallon abincin yasa yace "zaki ci?" da sauri ta gyadamai kai yace "okay to muje kici" yajuya yafita daga kitchen din da gudu tabiyoshi falo suka shiga ya ijiye mata cup din tea da plate din akasa da sauri ta zauna tana kokarin cire hijabin takasa saita dago kai ta kalleshi ganin ita yake kallo yasa ta kwaye fuska tace "yaki fita" daidai lokacin wata yarinyar yar budurwa haka doguwa sanye da hijabin ta ta shigo bakinta dauke da sallama tace "gani Uncle" murmushi yamata yace "yauwa Zainab dan tayani cire mata hijabin nan" murmushi tayi ta shigo dakin tace "Uncle bakuwa kayi" kwanciya yay akan kujera yace "yeah bamata da lpy ne" daidai lokacin zainab takaraso gabanta da sauri takoma baya ta make ajikin kujeran dayake kai tanason tai kuka, ahankali yace "hijabin xata cire miki karki damu she's my sister" kallonshi tayi idanunta sun ciko da kwalla ya gyada mata kai tareda nuna idonta ahankali yace "don't cry, bari tacire miki" ya kalli Zainab yamata alamun datazo, zuwa tayi da kyar ya samu tabari zainab tacire mata hijabin sanan ya dauko mata tea ta tacigaba da sha, saida tagama sha, nan ma bakaramin daru yasha da itaba kafin ta bari zainab ta kaita ciki dantai wanka da kyar yasamu ta yarda suka shiga bedroom, suna shiga yadau key yafita dan zuwa yasiyo mata kaya sanan yayo take away danshi bai iya girki ba.

Ko minti talatin baiyi ba ya dawo ya paka motar shi a tsakar gidan, tun daga waje yakejin kukan ta girgiza kai kawai yayi ya bude bayan motan ya dauko katoton babban leda daya siyo mata kayan sawa na mata, sai kuma ledan take away ya  dauko yay hanyar cikin gida dashi da sallama ya bude kofan ya shigo falon da gudun ta tafito daga uwardakan tana sanye da doguwar rigar atampa ja daga gani zainab ce ta bata kayanta, tazo da sauri tana kuka ganin shirin fadawa jikinshi take yasa ya juya da sauri yay facing kujera yana daura ledokin akan kujera hakan yasa ta tsaya abayanshi tana goge kwalla, ahankali ya juyo ya sauke idanunshi akan fuskarta yanda hawaye ke gangarowa yanabin kuncinta, anatse yace "mesa kike kuka" hanyar uwardaka ta nunamai daidai lokacin Zainab tafito tana kokarin saka hijabi kayan jikinta

duk sun jike, yace "ita ta jikaki haka zainab?" dariya zainab tayi tazo wajen tace "ihu tadinga yi wai bazata yi wankan ba dana hada mata ruwa shine ta dinga zubamin da kyar dai tayi, Uncle wlh tanada kyau bakuwar nan naka ya sunanta?" da sauri itama Bilkisu ta kallai tanuna kanta tace "ya sunana uncle?" dauke kai yayi dan idanunta namai wani irin ya zauna akan kujeran yadau leda daya na take away ya mikama zainab a kunyace ta karba tana godiya, da sauri ta zauna kusa dashi harda leka fuskarshi dago kai yayi ya kalleta hakan yasa ta washemai fararen hakoran ta, dan murmushi yamata yana mamakin ta, tuntsirewa tayi da dariya takara matsowa kusa dashi tace "ya sunana?" Ahankali yace "kinaso na baki suna?" da sauri ta gyadamai kai tana washe baki lumshe ido yayi kafin ya budesu yakara daurasu akanta yace "okay dagayau sunanki Ameerah" da gudu ta mike tsaye tana tsalle "yeeeee Ameerah, Ameerah" ta kalli Zainab data tsaya tana kallon ta tana yaba kyanta aranta ta murguda mata baki tare da hararan ta turo baki tace "sunana Ameerah ko Uncle" daga mata kai yayi Zainab tace "Uncle natafi" kudi yabata taki karba tafita da sauri.
Ahankali yabude dayan ledan dayan take away yaciro jellof rice ya kalleta inda take tsaye tanata kiran kanta da Ameerah tana juyi ahankali yace "Ameerah" da sauri ta dago kai ta kalleshi tareda washemai baki abincin ya nuna mata hakan yasa tazo ta zauna kusa dashi yasa mata spoon yabata tafara ci saida taci kusan rabi ta ture tana yatsine fuska, maganin ta yabata da ruwa tasha da kyar tasha sanan tadau abincin tanaci tana wasa dashi shikuma chatting yake a watsapp da Dr Ameenu, kanta dayaji ya kwanto akan kafadar shi yasa ya dago kai ya kalleta tai bacci ga takeaway akan cinyarta shinkafan dukya zuzzuba akan rigarta yakai kusan 5 minutes yana kallon fuskarta kafin ahankali ya janye kafadar shi ya gyara mata kwanciya akan kujeran tareda karbe take away ya kakkabe shinkafar jikinta acikin roban yawuce yakai kitchen sanan yadawo ya zauna kujeran nesa da ita yana kallon fuskar ta, addu'a kawai yake ko ina iyayen ta suke Allah ya bayyana su.

*kano*

Ahankali Abba yay sallama ya turo kofar dakin Bilkisu wanda Ayaan ya mayar nashi, abu dayane ke fitar dashi daga dakin shine salla ko wani irin zazzabi yake saiya tashi yana dafe bango yatafi masallaci. Mami itama ta tare gidan dan kula dashi, Big Mummy kuma takoma gida sabida bakuwar ta Munari wacce yanzu take neman kusan sati hudu da zuwa kenan amma dai kullum saitazo ta duba Ayaan. Shigowar Abba kenan bayan ya raka Dr Ibrahim dayazo dubashi dan anyi anyi dashi yaje asibiti yaki.
Ahankali Abba ya zauna kusa dashi akan gadon hanunshi rike da tray na abinci dan yau throughout yakicin komi, dafa goshin shi Abba yayi hakan yasa yadan bude idanunshi da sukai jajir, gashin shi da gemunshi sunyi busu busu, hannu Abba yasa ya taimaka mai ya tashi zaune ya jingina da gado, Abba yace "zoka ci abinci Boy so kake ka kashe kanka wai, dare da rana police nakan case dinan, nasa amana rokon Allah, in sha Allah, Allah zai bayyana mana gaskiya, da kansu zasu dawo da ita" Abba yay maganan yana mika mishi bowl din pepper soup, ture bowl din yayi da hannu ya dau pillow ya rike muryan na rawa yace "bazan iyaci ba, tana

chan hala ma basu bata abinci ba halama sunata dukan tane yanzu haka, kullum da tunanin ta nake wuni na tashi Pops..." yanda muryan shi ke rawa yasa Abba ya jawoshi jikinshi yana bubbuga bayanshi kafin ahankali ya ciroshu yama forehead dinshi peck yace "za'a ganta da izinin Allah yanzu dai ko 3 spoon ne kasha kaga zaria zani inaso naje nasami mahaifin Bilkisu, yakamata susan wats going on, idan bamu fada musu ba bamuyi adalci ba" dafe kanshi dayakeji kaman zai fashemai yayi Abba kaman zaimai kuka yace "sannu Boy oya sha sha saika sha magani" da kyar ya bude ido ya karbi coffee da Mami tasamai madara, saida yasha sanan Abba ya lullube shi da bargo yafita baitaba sanin haka Boy keson Bilkisu ba, driver yajashi sai zaria.

Kiran sallan la'asar ya farkar dashi daga baccin wahalar daya dauke shi da kyar ya sauko daga gado ya shiga bayi yaje ya dauro alwala yafita daga dakin a  stairs ya hadu da Mami ta hado abinci a tray zata kawo mai da sauri ta ijiye tray akasa ta rikeshi ganin kaman zai fadi, kaman zatai kuka tace "ina zaka ahaka Ayaan kana layi?" da kyar ya ware idonshi ya kalleta yace "masallaci zani Mami" girgiza mai kai tayi tace "Ayaan no mukoma daki kayi achan u don't look good, baxaka iya zuwa masallaci ba" ahankali yace "zan iya Mami please ki barni nasan nama Allah laifuffuka da yawa, cikinsu harda rashin sonyin salla, amma yanzu in sha Allah ba ciwo ba koma me saina je masallaci" ahankali ya zame hanun daga nata yana tattaba karfen stairs ya sauka kasa Mami tabishi da kallo da sauri ta share hawayen daya zubomata suna ganin jarabawa.

Koda aka idar da salla yafi minti talatin azaune shi kadai amsallacin dan duk an watse sai shi baima da karfin tashi, dafashi dayaji anyi yasa ya dago kai limamin masallacin ne daya shigo daukar wayan shi daya manta dashi yace "baka da lafiya ne na taimaka maka na kaika gida" dago kai yayi ya kalli Imam kafin ahankali yace "tambaya nakeda shi" yanda yay maganan kaman zararre yasa Imam ya zauna ya lankwshe kafa, jingina kanshi dayamai nauyi yayi ya kalli Imam da idanunshi dasuka kankance ahankali yace "a Austria na girma, achan nai secondary school har nazama likita, am a very bad boy, idan nace bad i mean bad baddest, d only thing danasan banayi shine shaye shaye but zuwa clubbing, daukan mata, saka sarka, dan kunne, rashin salla duk nine, bayan nakare karatu na tattas na dawo harna fara aiki a asibitin abokin Pops dina inanan da halina even though Mami na da Abba suna kokarin su barinma Mami suga na dena amma naki, bansan meya sameni ba sai akace na haukace, ranan dai dana farka na ganni cikin kaya masu datti, awaje mai datti da bola ga wari, sanan gani kusa dawata yarinya wacce ita ta taimakeni da ina hauka hawaye duk sun bushe a idonta, ba karamin wulakanci namata ba har ina marinta a fuska amma kasan wani abu Imam?" yatambayi limamin yana bude ido kadan dan idanunshi a lumshe suke Imam yace "ina jinka" cije leben shi yayi cikin jin azaban da kanshi kemai yace "bayan na koma gida dudda fuskar yarinyar data taimaken nata bijiromin koda kulle ido kuwa nayi amma nai shiru naki fadinma babana harsai randa babana ya tamabye ni ya akayi na warke, na fadanmai, shine muka shirya mukaje zaria neman gidansu, bazan taba manta ranan" ya dafe kanshi yana wani irin murmushi yace "kafarta nafara gani da dogayen yatsun kafar dan batasa takalmi ba, kafarta na cikin jan lalle dayay wani irin kyau ta shigo dakin baban nasu da muke ciki tana sanye cikin pink hijabi mai hula, yanayin yanda take magana da komi nata sainaji ta shiga raina sosai, bantaba son wata mace aduniyar

nan ba, banma san ya ake so ba amma saina ji ita ta tsayamin arai sosai, kome nakeyi saita fado zuciya ta, bantaba nunama kowaba saidai duk lokacin dazan hadu da ita saina mata wulakanci, naci xalin ta, nasata kuka, ranan da mahaifiya ya bijiromin da zancen aureta ranan banyi barci ba sabida farin ciki amma ban nunama kowaba saima kekashe ido danayi nace banison ta, ni mamakin kaina nake nine keson karaman yarinya haka yar talakawa, aranan da mukaje gidansu mahaifin ta yace mana ansa mata rana bikinta saura sati daya zuciyata takusa bugawa, da gangan nai karyan waya nake nafito ko zan ga wani almajiri ya nunamin waye isyakan da akace zata aura, ina fitowa naganta tana hira da shi jinai kaman na kashe isyakan wlh Imam, luckily sainaji yana fada mata inda zashi koda muka tashi tafiya saiban bisu munkoma kanon ba, adayake nai wayau nadau hoton isyakan saina turama wayan su kanin abokina dake zaria yana karatu a ABU da abokanshi hoton Isyakan nafada musu inda naji yace zaije, haka suka je basu ganshi ba suka fadamin saina cemusu to suzo layin su yarinyar su jirashi, suna zuwa suka kamomin shi aka kaishi hotel din dana sauka, kaga dukan danami kuwa wlh nakusa harbeshi sabida tsananin kishin yanda na gansu tare suna hira harda wani wai yasiyo mata ice cream, to saikuma na kwabi kaina akan kissan kai ba halin da musulmi yakama ta yanayi bane, saina bijiro mishi da ranan biki awajen daurin aure yace yafasa aurenta sanan namai kyauta sosai namai warning daya tsorata yaron ainun, shekaran jiya saida nakira shi na rokeshi ya yafemin bansan ko harda alhakin shi yake binaba yanzu ba, yace ya yafemin yanzu ma yay aure sanan ya bude shago dakuma makaranta da kudin dana bashi" sai yay shiru Imam yace "ina jinka" ahankali yace "Imam inason Bilkisu sama da yanda kake tunani amma inhar zan hadu da ita sau dari saina sakata kuka sau dari da hamsin, inci zalinta in gaya mata bakar magana, har muka tare agidan mu, yanzu haka yan kidnappers sunzo har gida sun dauke min ita, i think Allah na hukunta nine akan laifuffukan dana mishi" hawayen daya zubomai ne ya share da sauri yana sauke ajiyan zuciya ahankali yace "na tuba Imam, bazan kara koma ma aikin alfahasha ba, dan Allah katayani rokon Allah yadawo min da farin cikina Bilkis, ya tsaremin ita duk inda take, yadawo min da ita cikin koshin lpy, wlh na tuba, na tuba, na tuba, nai nadaman duk abubuwan danai ada, I love my wife more than life itself, Imam mezanyi Allah ya yafemin yadawo min da Bilkis?".
♦♦ *SANGARTATTCE* ♦♦

65 - 66

Sassanyar murmushi Imam yamai yace "Allah gafurur Raheem ne, kadage da addu'a kadinga tashi cikin dare kana rokon Allah, kana gayama Allah bukatun ka, matar ka zata dawo, da izinin Allah zan tayaka da addu'a banda hakama duk inda take Allah ya tsare maka ita ya kare maka ita" ahankali yace "Ameen" Imam ya mike ya mikamai hannu yace "tashi na taimaka ma katafi gida" ahankali yamika ma Imam hannu da taimakon shi ya mike tsaye suka fita daga masallacin daidai wajen masallacin suka hadu da securities din da Mami ta turo azo adubo mata shi dan tajishi shiru, mika musu shi Imam yayi suka  tafi dashi gida.

Suna shiga cikin gidan idanunshi suka sauka akan motar shi dake parking lot, wajen motar yayi da taimakon su ya bude, idanunshi ne suka sauka akan jakar Bilkisu daya karba ranan dazata bata hakan yasa ya mika hannu ya dauko, ahankali ya rungume jakar sosai ajiki yay cikin gida rike da ita, a parlor ya zauna yana zazzage jakar babu komi ciki sai wayarta da lace dinta da sauri yadau wayarta yana duddubawa amma akashe take ba chaji, da kyar ya mike yay sama ya shiga dakin ya makala wayar achaji, tana dan yi 10% ya kunna da sauri, gallery ya shiga da saurin bala'i kaman mahaukaci nanko yaci karo da hoton ta guda biyu kacal wanda tai selfie daya tayi shine kwance kan gadonta daga ita sai yar rigan bacci kusan rabin kirjinta waje rungume hoton yayi wasu hawaye masu zafi suka zubo mai sai kuma nabiyun tana sanye da doguwar rigar atampa afalo kan kujera tai hoton azaune, murmushin daya dade baiyiba yayi ahankali yakai bakinshi ya sumbaci hoton yace "i love yhu wifey" hanunshi ya tura cikin aljihu ya zaro sabon wayan da Abba yabashi sabida fashewar da tashi tayi, dailing number Cp yayi yana dagawa da kyar yace "an samu hoton ta kazo" yana fadin haka ya katse wayar yasake kwanciya anan kasan dakin ya rungume wayar sosai, kanshi dayaji ana shafawa yasa yadan bude ido kadan Mami daya gani ne akanshi yasa zai bude baki ta girgiza mai kai ahankali ta zauna ta daura kanshi akafafunta tana mai head massage.

Abba yadade yana magana da Malam a zaure kasancewar dalibai sunje bara saida yagama Malam ya nisa fuskarshi dauke da murmushi yace "da izinin Allah ankusa ganin ta" Abba kaman zaiyi kuka yace "zamu shiga cikine na fadima mahaifiyar ta?" girgiza kai Malam yayi yace "a'a banaso suji komi kasan mata da sa zance arai, yanzun nan saisu iya shiga damuwar dazai haifar musu da ciwo, bari in shiga gida namusu sallama zan bika na dubo Ayaan sanan akwai addu'a danake so namai sanan nayi agidan da aka dauketan, in sha Allah kwann nan zata dawo".

Ba'a jimaba malam yafito dauke da wata yar jakan malamai Abba ya mike suka shiga motar driver yajasu.
Cp na zuwa kasancewa yay bacci Mami ce tabashi hoton ya karba yace "za'a watsa hoton duniyar yanar gizo da gidan talabijin da sauran kafafun yada labarai hakan zai taimaka sosai.

Wuraren 9 nadare suka shigo gidan sabida go slow daya rikesu akano, bakaramin tausaya wa Ayaan dake bacci Baba yayiba.

*Bauchi*

Yau kusan satin ta biyu kenan agidan tun washe garin ranan datazo kanwar shi Ummy wacce yan makarantar su suke cema Ummy fingers tazo Buchin, yarinyar badai kyau da iya gayu ba, da kyar da kyar yasamu tana dan yarda da Ummy harma su kwana daki daya amma dudda haka saita ga dama take kula Ummy gashi Ummy na sonta bana wasaba.

Dafe zuciya Ayaan yayi yana wani irin nishi, kirjinshi na zafi sosai yama rasa ina zaisaka kanshi yaji dadi, kanshi kaman anzubai wuta, da sauri Mike yafita ya dauko mai cold water, CP ne ya karba ya bude ya samai abaki da kyar ya kurbi kadan ya saukar dawasu tagwayen ajiyar zuciya kafin ahankali ya dago jajayen idanunshi ya kalli inspector yace "inaso kayi contacting headquarter police din zaria azuba jami'an tsaro a anguwar su Bilkisu gabaki daya right now please" yanda yakara she maganan yasa CP yace "calm down" ya kalli babban inspector dake tareda shi yace "kira officer saminu na zaria ka sanar dashi, Ayaan bamu address din gidan" ahankali Ayaan yabasu address din shikuma CP yadau waya yakira headquarter dan atura police suje Amina kano international Airport tayanda bazasuci sa'an ficewa da Abba daga airport dinba bayan sun iso, sanan ya kalli Ayaan dake dafe da zuciyar shi yace "tashi muje masallaci daganan muwuce headquarter dan ayi tracking phone number ta" da kyar ya tashi suka fita daga dakin yana ganin jiri jiri.
Saida sukai salla sanan suka wuce police headquarter number wani police yazo ya karba ana kokarin tracking shikuma yabi bayan CP zuwa dakin da ake interrogating yaran Big mum din, CP ya shiga dakin shikuma ya tsaya ta gaban glass din waje yana kallon yanda ake questioning dinsu, Sosai suke kuka tsabagen azaba daya daga cikin su yace "wlh, wlh, mu bamusan hajiyar ba ogan mune yasan hajiyan, ogan mu Bala" da sauri Ayaan yakara gyara tsayuwa yana kallonsu yana maimaita sunan Bala aranshi, "Bala, Bala a ina ma yataba jin ko ganin sunan nan?" hanunshi ya goya abaya yafara zagaye wajen chak ya tsaya yace "yes! Wanan letter, awanan letter naga sunan Bala dama number shi" daidai lokacin CP yafito yana gyara hanun rigarshi daya tattare kafin ma yay magana Ayaan yace "inada number Ogan nasu Bala ta hanyar wani sako da aka turamata dana karba naga number shi da sunan shi akasa" gyadakai CP yayi yace "good good" daidai nan suka bude kofar wani daki da ake tracking number Big

Mum, tashi mai tracking number dake gaban wasu computers yayi yasarama CP yace "sir bamu iya samun location dinta ba is as if ta karya sim dinne" da sauri Ayaan yace "bari naje na dauko wasikar saina turo muku number ayi tracking Ogan dan duk inda Bala yake nasan yana tareda Big mum, CP ya wayan da sukaje airport by now yakamata ace Pops sunyi landing" asanyaye CP ya dafe kafadar shi yana girgiza mai kai yace "team dina sunce har yanzu babu any jet daya sauka banda haka ma basuga any suspicious person ba, yanzu dai abinda nakeso dakai Ayaan shine kaje ka boye Bilkisu inda matar nan bazata taba ganota ba, zakuma muhadata da police da zasu tsare ta, hospital dinka is not safe tanada men dazata iya saka wa suje su daukota, kaje idan kaje yanzu ka turamin number Bala koma yaya ake ciki zandinga sanar dakai" gyada mai kai kawai yayi ahankali yajuya yafita daga office din yana kiran sunan Allah aranshi shi kadai yasan yanda yakeji aranshi ya shiga mota yatada tunani kawai yake ina zai iya boye Bilkisu dan duk wani gidajen Abba da nashi babu wanda bata saniba, wani zubin sai big mum tasan wani abu nashi Mami ma bata saniba, lumshe ido yayi wasu irin hawaye masu zafi suka zubomai ahankali yace "Ya Allah please take care of my Pops and Mami" baida matsala gidan su Bilkisu dan yasan babu ta yanda zasu iya wuce jami'an tsaron da aka zuba suje dauko wani, saidai in Big Mum takashe shi dan wlh bazai taba bada matar shi da batada lpy ba, bazai taba badata bane, yanzu a ina zai iya boyeta, ya killace ta, dan ko kadan brain dinta bayason damuwa yanda take last stage of recovery dinan Aaman! Zuciyar shi takira, da sauri ya rage saurin gudun dayake amota gudun karyay hatsari, to wama zai kira dole shine, yakula da ita bayan ya tsinceta batare dayaci amanar taba gashi ko godiya baimai ba lokacin ashe yanada rana, to yanzu ina zaima sami number shi? Da sauri yace "Pops log book" kwana yay da sauri akan titi yadau hanyar dazai kaishi gidansu, ko parking din kirki baiyiba yafito polisawan dake gadin gidan na gaishe shi baimabi ta kansu ba yay cikin gidan da mugun gudu, dakin Abba yayi bayan ya bude drawer shi yaje yana fiffito da takardar du da kyar yaga littafin, zama yay anan kasa yana duddubawa page by page arude, tsaki yayi ya jefar da book din akasa yace "sh*t" jingina yay da drawer ya dafe kanshi dake wani irin bugawa da karfi ahankali yace "Allahumma ajirni fi musibati" haka yadinga maimaita wa kusan sau biyar kafin ya dago kanshi ahankali ya kafe littafin da pages din keta buduwa sabida iska ido, da sauri ya rarrafa ya dauko book din yadawo ya zauna yana bi page by page yana dubawa yana wani irin nishi tunda yake arayuwan shi baitaba sanin tashin hankali haka yakeba saiyau, lokacin Bilkisu shi wanan bamaya hayyacin shine, harzai ijiye littafin idanunshi suka sauka akan sunan Aaman, da sauri yaciro wayar shi ya kwashi number yay dailing ya kafa a kunne  har yagama ringing ba'a dauka ba yasake dailing akaro nabiyu harya cirerai saiya ga anyi picking da sauri yace "A...Aaman, Barister Aaman" daga ta dayan bangaren anatse Aaman dake kwance kan doguwar kujeran mom dinshi yatashi zaune yace "yes nine, waye ke magana" ahankali yace "Dr Ayaan, amm mijin mijin wacce ka taimaka, mijin wacce ka dawo mana da ita kano u and ur friend" shiru Aaman yayi baisake cewa komiba dan yagane shi daga explanation din dayayi, shiru shima Ayaan yayi zuciyar shi nawani irin mai zafi, ya lumshe ido saikuma ya budesu ahankali muryan shi nadan rawa yace "am sorry Man" dan murmushi Aaman yayi yace "bakomi, why is ur voice like dat is everything okay?" girgiza kai yayi wasu irin hawaye sun taru a idonshi muryan shi narawa yace "please taimakon ka nake nema wayanda suka taba kiddaping wife sunyi kiddaping Pops dina da Mami and my step Mum ce" zumbur Aaman ya mike tsaye yace "subhanallahi" "and tace abasu Wife in exchange inba hakaba bazata saki su Pops ba and.."

kasa magana yayi sabida kukan da tun dazu yake dannewa yazomai, runtse ido Aaman yayi sabida radadin da zuciyar shi tahau yi, ahankali ya budesu ya kalli agogo 8:40 nasafe ne yanzu ahankali yace "Dr be strong man, ina Abj ne, amma yanzu nan zanbi flight nazo kano before 10 I will be there, text me  address din inda kake, be strong Man babu abinda zai sami Dad da Mom da izinin Allah" gyadamai kai Ayaan yayi yama kasa magana ya katse wayar yamai text din address din hospital sanan ya mike tsaye bayin Pops ya shiga ya wanko fuskarshi ya share da towel sanan yawuce yafita ya shiga mota yadau hanyar hospital.

Parking yayi a parking space sanan yafito daga motar jiki asanyaye idanunshi sunyi jajir, dark shade dinshi ya dauka yasaka sanan ya kulle motar yay cikin asibitin, tun daga bakin office dinshi yakejin kukan Bilkisu da sauri yabude kofar ya shiga ya mayar ya rufe yay cikin bedroom din bayan ya cire glasses din ya ijiye akan table ya bude kofa ya shiga, ajikin kofa ya tsaya ya kafeta da ido yanda take zaune akasa ga abinci a gabanta na Mrs Biggs sai uban kuka take Nurse Sameera da tsabar karfin kukan ta baima barta taji alamun shigowan mutum ba sai faman lallashin ta take.

Yafi minti biyu kallonta yake wani irin sonta na ratsa kowani jijiya na jikinshi, dan gyaran murya yayi da sauri daga Nurse Sameera har ita suka dago kai suka kallai da gudu ta mike tana kuka tafada jikinshi ta kankame shi tsam tsam tana kuka sosai da sauri Nurse Sameera ta mike kanta akasa tana murmushi tace "tundazu ta tashi takicin abinci nazaci na dakin ne bata so na aika aka siyo mata a Mr biggs shima takici sai kuka takeyi taki cemin komi kuma, tunda kadawo bari natafi" dan murmushi yayi yace "thank you so much nurse Sameera" murmushi tayi tace "bakomi Dr" tabude kofa tafita daga dakin ta rufo musu, sai alokacin yay hugging dinta back tightly kafin yafara tapping bayanta alamun tai shiru, dago kanta tayi daga jininshi ta kafeshi da jajayen idonta dake tsiyayar da hawaye, ahankali ya bude ido shima ya kalleta, dukan kirjinshi tahauyi tana kuka sosai, da kyar ya daga hannu yakama hanunnata yahada da nashi yana girgiza mata kai yama kasa magana, shigewa jikinshi takara yi sunkai 2min ahaka sanan yaciro ta daga jikinshi yaja hanunta sukai cikin dakin akan gado ya zauna ya zaunar da ita a gefenshi, hanun yasa ya share mata hawayen dake zubowa ya girgiza mata kai ahankali yace "am sorry nabarki nafita ko, stop crying zokici abincin ki" abincin ya dauko ya daura akan jikinshi yadau spoon ya debo yakai bakinta budemai tayi tana kallon idonshi tanaci haka yadinga bata fuskarta kadai nasa shi kwanciyar hankali, saida ta koshi ta karbi spoon din daga hanunshi da sauri ta debo itama ta kaimai baki tana washe mai baki, bude mata yayi ahankali yana kallon fuskar ya karba yaci dan yasata farin ciki amma ko kadan bayajin dadin abincin abakin shi, da sauri tasake debowa tana wani irin washe baki tsabagen murna takaimai bakinshi tana kallonshi, wani irin zuciyar shi keyi, kasa bude baki yayi hakan yasa tasake matsowa tana budemai bakinta alamun yabude baki tasaka mai, wani irin rawa zuciyar shi tafara na kuka sake tunamai da Pops datayi dan dayana yaro haka yakemai in yana rashin lafiya yakicin abinci, da sauri ya ture spoon din ya jawo ta yasaka ta ajikinshi ya fashe da wani irin kuka, da sauri tafara kokarin fizge jikinta daga nashi jin yana kuka hakan yasa yasaketa ahankali, kallon fuskarshi tayi ganin yanda yake kuka yasa ta kwaye fuska zatai kuka itama cike da damuwa, da sauri ya girgiza mata kai yana goge hawayen dayake, da sauri ta zauna akan cinyarshi tasa hannu kaman yanda yamata dazu ta share mai hawayen duktai wani irin da fuska rungume fuskarshi tayi

hawaye nataru wa a idonta tana shafa kanshi nakusan 1min saikuma tasake shi ta dago kanta ta kalleshi dan tabbatar daya dena kukan, murmushi yamata asanyaye, sake washe mai baki tayi tasake rungume shi saikuma tasake shi ta sauka daga kan jikinshi ta mike atsaye agabanshi tana kallon fuskarshi shima ita yake kallo a sanyaye, hannayen ta ta daura akan kafadar shi tana washemai baki ta dugo da kanta ahankali tana kallon kwayar idonshi shima ita yake kallo kaman yau yafara ganinta, daura lips dinta tayi akan nashi da sauri ya chapke tareda rungumota jikinshi sosai yana wani irin sauke ajiyar zuciya, daukar ta yayi chak ya kifata a gado yasa hannu ya zuge mata zip din doguwar rigan ya cire doguwar rigar ya yar shima cire kayan jikinshi yayi yahayo gadon, da sauri tafada jikinshi ta kankame shi sake hada bakinsu yayi yana wasanni da ita kafin ya shige ta yana yanda yaga dama da ita.

Wuraren goma ya shigo garin kano, taxi ya dauka ya bashi address din hospital din da Ayaan yatura mai, goma da kusan 15 minutes taxi yay parking a hospital din, ya shiga yana kalle kalle ahankali yaciro wayarshi yay dailing number Ayaan amma ba'a dagaba akaro na uku ya dauka murya chan kasa yace "please kabani 10min am coming" bai kawo komiba Aaman yace "okay ina reception" , dagata yayi yakaita bayi wanka yamata agurgurje yafito yana tsane gashin kanta da towel sai kallonshi take, dan murmushi yamata, yamata kiss a kumatu yace "thank you, Allah miki albarka kin sa nasami natsuwa" hanunta ya daura akan towel din ya dauko mata wani bakin doguwar rigan Abaya ya shiryata tsaf yasaka mata dogon hijabi daya kai mata guiwa pink, yasaka mata loafers sai kallonshi take sanan shikuma ya shirya cikin Jean da riga white yasaka takalmi yadau jakarta da magungunan ta yadawo yarike mata hannu yace "let's go" fita sukai daga dakin, a reception yaga Aaman zaune yana danna waya, kaman ance ya dago kai ya gansu suna tahowa hanunta cikin nashi da sauri ya kori abinda kemai yawo a ranshi ya mike tsaye yana dan murmushi.

Hannu Ayaan yamika mai suka gaisa da ido yamai alamu suje waje, wajen motar shi sukaje, ahankali Ayaan yace "duk duniyar nan a yanzu kai kadai nai trusting, koda yau na mutu nasan tana good hand, please ga wife inaso kabar garin nan da ita harsai naci nasaran kubutar da iyayena bazan tsaya jiran police ba" bai jira mezaice ba yajuyo ya kalli Bilkisu da shi taketa kallo, cupping face dinta yayi ahankali yace "Baby follow him he's going to take care of you for me kinji, be a good gurl, I love you so so much wife" lumshe ido yayi da sauri, patting kafadar shi Aaman yayi ahankali yace "I can stay with you lemme help you Bro, inada wata sister dake aure a garin nan zamu iya boyeta a gidanta" girgiza kai Ayaan yayi yace "kai nakeso ka kulanmin da ita, I want her out of kano, I don't want to risk her life in anyway tana last stage na recovery ne, please please take care of her for me" da sauri yay wurin motar shi baya ya bude yasaka jakarta ya rufe yadawo yana mata murmushi yakaita gaban mota yace "kibishi zanzo na daukeki don't cry okay" washe mai baki tayi, ahankali ya sumbaci gaban goshin ta yasaka ta aciki ya kullo yadawo inda Aaman yake a tsaye sai binshi da kallo yake hanunshi Ayaan ya kama ya saka key mota da magungunan ta yace "once kakai kabata magungunan nan twice a day ne bacci yake sata, ga key kayi parking motar a Airport leave d key with security, I will never forget dis favor" da sauri ya juya zai wuce Aaman ya kama hanunshi, ahankali ya tsaya chak batare daya juyoba zagayowa ta gabanshi Aaman yayi yay hugging nashi yana buga kafadar shi yace "all d best, I promise to take care of her, Allah yabaka sa'a, ya kubutar dasu" Ameen

Ayaan yace yana kokarin hana kanshi kallon motar, ahankali Aaman ya sakeshi yajuya ya bude motar ya shiga, da sauri ya juya baya bayason ya kalleta dan kuka zaiyi, Aaman yaja motar sukabar asibitin.
♦♦ *SANGARTATTCE*♦♦

Maman Abd Shakur

86 - 87

Har suka shiga titi waige waigen shi take hartazo tadena ganinshi, kuka tafara mara kara ahaka har sukakai airport yay parking motar yaciro jakanta ya zagayo ta inda take kukan ta ya bude mata kofar yana kallon ta, ahankali yace "fito" fitowa tayi tana kallen wajen tana kuka saikuma ta kalleshi tafashe da kuka sosai, girgiza mata kai yayi cikin muryan lallashi yace "stop crying gashinan zuwa, zomuje, goge hawayen" share hawayen tai da sauri, yabama security key suka shiga cikin airport din booking yay musu kafin suwuce departure hall dan, in 15minutes time jirgin su zai daga, zama sukayi yaje yasiyo mata popcorn yakawo mata karba tayi sai jujjyawa takeyi tana kalle kalle saida aka fara boarding sanan suka wuce suka shiga jirgin, jirgin yadaga sama.
Sha biyu daidai na rana jirginsu ya sauka a Abuja Ummy ne tazo da Mota daukan su tana ganin Bilkisu da gudu tazo ta rungumeta tureta tayi tanason tafara kuka ya harari Ummy yace "ke kirabu da ita batada lpy, ban key" mikamai key motar Ummy tayi bayan ta kama hanun Bilkisu dahar tafara kuka, karba yayi ya shiga gaban motar Ummy tabude musu baya suka shiga ta rufo sukai gidansu dake wuse. Hadadden gidane babba sosai koda sukakai baiwani sha wahalan shawo Kan Mum dinsu ba, bakaramin tausayi Ayaan din ya bata ma tai musu addu'a sanan ta lallaba Bilkisu da kyar taci wani abu Aaman yakawo maganin ta Mum tabata tasha Sai kuka take, sanan Ummy takaita dakinta cikin minti biyu bacci yay awon gaba da ita, fitowa Ummy tayi hakan yasa Aaman yace "where's she" zama tayi kusa da Mum tace "tai bacci" Dan ajiyan zuciya ya sauke sanan ya kalli agogon hanunshi yatashi ya kalli Mum yace "bari naje, zan kai Usaida hospital zamuje muyi blood test su genotype and d rest" murmushi Mum tayi tace "saika dawo son" ficewa yayi daga gidan bayan ya Kira Usaida yace mata ta shirya.

**************

Da saurin shi ya shiga office dinshi yana share kwalla wani irin kewanta da shaukin ta ke shigan shi sosai, gadonsu ya kurama ido dan gani yake kaman zai ganta, kayan jikinshi yacire ya shiga bayi yayo wanka yana fitowa ya shirya cikin wani bakin riga bodyhug da bakin wando bakaramin kyau yayi ba kayan sun fito da hasken fatarshi sosai, sneakers yasaka yadau wallet da waya yafice daga office din bayan ya kulle, taxi yatare ya shiga.

******************

Babban gidane da ba'a gama ginewa ba, dan Mami bataga hanya ba sabida wani bakin yadi da big Mum tarufe mata fuska dashi, zaune take akan kujera tun isowan su ahaka take an daure mata hannayenta tabayan kujera da kafa, an taushe mata baki sanan anrufe fuskarta da bakin kyalle, muryan big mum kawai takeji dawasu maza, addu'a kawai take aranta Allah ya kareta daga shairin big Mum sanan ubangiji Allah ya karemata Ayaan da Bilkisu, alamun tafiya mutane dayawa taji ana shigowa inda take batasan meke faruwa ba tadai ji Big Mum na cewa ku kulle shi da kyau, saikuma wuf aka yaye bakin abin daya rufe fuskarta, haske ranane bau awajen ahankali tabi wurin da kallo gini ne babban gaske da ba'ai plasta ba kawai block ne saikuma katakwayen roofing sama da aka jera kaman ana shirin saka kwano ne saikuma ba'a sakaba, ahankali ta juyo da kanta ta kalli Big Mum dake zaune kan wata kushin ita da pilot din Abba tanamai murmushi, kwalalo ido Mami tayi tanason tai magana amma ba halin yi sabida taushe mata bakin da akayi, wani irin mugun kallo Big Mum ta watsa mata saikuma ta kalli Bala dake tsaye shida wasu samari guda biyu tace "budemai fuska ya ganni Bala naga ya farka yana motsi da kafa" da sauri Mami ta kalli gefenta kirjinta na bugawa wakuma aka kamo ko Ayaan ne, Alhaji! Tafada aranta tana wani irin salati da sallallami tana sanar da ubangiji halin dasuke ciki, kwalalo ido shima Abba yayi yanaso yay magana ganin yanda aka daddaure Mami amma ba hali kaman daga sama yaji muryan big Mum tace "Alhaji" da sauri ya juyo dakai ido da ido sukayi da big Mum da pilot dinshi suna wani irin kallon juna, murmushi Big Mum tayi tawani lashe baki tace "dan ka yazaci yanada wayau yasa polisawa suncika airport yazaci anan zaku sauka ne? Hahaha, karkai mamaki fa, bawani abu yasa nai hakaba sai dukiya, dukiyar ka kawai nake bida, nariga nafada ma danka ya maida duka dukiyoyin ka sunana sanan ya saki yarana da aka kama na uku kuma yabani Bilkisu na kashe dan itace taja asirina ya tonu haka bazan taba yafe mata ba, ayanzu dai nabashi awa ishirin da hudu ko my man" tai maganan tana shafa gemun pilot dake sanye da uniform yana kallonta, girgixa mata kai yayi tareda fuzar da iska yace "hajjaju ta aganina awa ashirin da hudu sunyi yawa fa, ko Ina neman mu ake Kuma kinsan atsakiyan filin daji nai parking koda yaushe wani abu kan iya faruwa, ki rage lokacin, shidan yamma nayi ki kirashi yabamu abinda mukeso muje mu shiga jirgi mubar garin nan. Gyada kai tayi ta mikama Bala hannu alamun ya bata wayanta, kawo mata wayar yayi Abba duk yanabin su da kallo da idanunshi dasukai jajir kokarin magana yake amma ba hali, kunna wayan tayi bayan tasaka wani sabon layi ya sanya mata nashi, number Ayaan tai dailing daidai lokacin Ayaan da CP sun shiga dakin da ake tracking number, wayar yaciro yana kallon number da sauri yay picking yasaka a speaker yanama me tracking din alamu da ido, dan hakanan yaji aranshi big Mum ce, picking yayi yasa a hands free wani irin dariya tayi tace "bazaku taba iya kamani ba duk sim din dazan kiraka dashi dazaran nagama magana nake ballawa, nakira ne nafada maka nafasa baka awa ashirin da hudu karfe shidda daidai zan kira nafada maka inda zakaje ka ijiye Bilkisu" katse wayar tayi da sauri Ayaan yay wurin computer inda CP ke tsaye akan me tracking number yace "how far" girgixa mai kai CP yayi alamun ba'a samuba tsaki yayi hankali atashe, fita yayi yawuce masallaci alwala yayi ya shiga yabi jam'i yay azahar yana fitowa motar shi ya shiga ya zauna yaciro wayar shi number Bala dayariga yay saving yaciro yay dailing akashe, wani irin ihu yayi ya daki kujeran motar, kunna motar yayi ya wuce MTN

office wani abokin shi ne babba awajen hakan yasa ya wuce upstairs direct knocking yayi ya shiga abokin shi mai suna Musa na ganin shi yay dariya yace "Dr ana ganin ka dama" dan murmushi kawai yayi ya zauna Musa yace "why is ur face like this" girgiza Mai kai yayi yace "I need a favor" wayar shi ya ciro yajawo wata yar memo dake gabanshi da byro ya rubuta Mai number Big Mum, da number Bala ahankali yace "please track this two numbers for me in hakan baiyuba inaso kabani any other number da masu layin suke amfani dashi sanan amin tracking dinsu" yanda yake magana yasa abokin nashi yatashi da sauri ya bude yar fridge din office dinshi ya dauko bottle water yadawo ta gabanshi ya bude yabashi, kasa karba Ayaan yayi saima kafe goran dayayi da ido yakasa karba dudda yanajin kishi, hanunshi mutumin ya kama ya saka goran ruwan aciki ahankali yace "Dan Allah kasha abokina" kafawa abaki Ayaan yayi yasha kadan sanan ya ijiye, ahankali mutumin yace "tashi muje adubama dudda dai kaki gayamin mecece matsalar" fita sukayi daga dakin, wani office suka kara shiga, Musa ya mikama wani dake aiki takardan yace "binciko mini wayan nan numbers din" karba yayi ya kwafe number yana danne danne a system din sai yace "sunan layi daya Saratu gwanaye dayan kuma Bala Mubarak, banda wanan layin Bala nada layi biyu kuma daya bude da sunan nan" da sauri Ayaan yaciro wayar shi yace "kiramin numbers din please" kira mishi akayi ya kwasa yajuyo yace "please ku gwada min tracking din numbers din konawa ne zan biya please, zan tafi yanzu once kunyi kutaramin address din tawaya na" yanda yake maganan ne yasa Musa yace "wats happening Ayaan?" dauke kai yayi sabida hawayen dayake ji ahankali yace "anyi kidnapping su Abba ne" da sauri yafita daga wurin bakaramin tausayin shi Musa yaji ba Ayaan mutum Mai kirki tun kafin yasami aikin nan lokacin da matarshi ke labour Ayaan yamata CS kyauta sabida baida kudi, da sauri ya kalli Yaron yace "don't rest saika samo location dinsu" yafita daga office din dukya damu.

Ahanya ya tsaya yay la'asar kafin ya wuce gidan su, gashi nan kawai kaman zararre, parking yayi a compound ya wuce shashin big Mum, hargitsa dakinta ya shiga yi yana neme neme ko zai sami any clue, daga bayama rigarshi yacire yay hanging akofa yazo ya daga katifar ta ya daga gado yana dube dube, yakoma wajen drawers din bedside yahau bubbudewa, wardrobe dinta yakoma yana ciccciro kayanta yana wurgawa kasa kaman zararre, kaman da kayan yake fada, finciko kayan ya dinga yi yana yarwa dan kara dayaji akasa yasa ya kalli kasan da sauri, wayansu kayane daya zubar hade dawani file babba, da sauri ya tsugunna ya dauko file din ya bude takardu ne daban daban, ahankali yakoma gefen gado ya zauna yana duba takardu falle falle yawancin su takardun gidajen Abba ne da papers din filaye wanda duk yasan da zamansu, idanunshi ne suka sauka akan wani takardan owernship din gida wanda sunan hajiya Saratu ne ajiki, da sauri ya cigaba da budewa yana going through d content, rufewa yayi yana dan tunani yaushe which house is this? Address din gidan ya duba hakan yasa ya saki file din anan kasa yaja rigarshi daga kofa yasaka yafice harda dan gudun shi, yana shiga mota kiran CP na shigowa wayarshi da sauri ya dauka yana driving, daga ta dayan bangaren CP yace "Ayaan kazo headquarter sabida dazaran takira ka mu samu muyi tracking dinta down, this is five thirty kai sauri all team dinmu damuka zuba babu wani vital information, munje gidan da yaran damuka kama sukafada mana suna zama suda Bala amma ba'anan suke ba, hurry up karta kiraka kana hanya".

Yana shiga office din da ake tracking number kira na shigowa wayarshi alamu CP yamai dayay picking hakan yasa yay picking yasaka a handsfree, cikin kakkausar murya Big Mum tace "am not going to repeat myself Ayaan ko abar tracking wayar nan kona harbi baban ka, ka ganni nan gani gashi sai kallona yake yana son yay magana amma na kulle mai baki" tai maganan tana wani irin zagaye Abba tana goga mai bakin bindiga awuya, juya ido tayi tace "au bakaji ba kenan, stop tracking my phone, tusss" Big Mum ta harbi Abba akafan haggu tasa hannu ta tunbuke tsumman da aka kulle bakin Abba dashi, wani irin ihu azaba Abba yayi har cikin zuciyan Ayaan yaji ihun dafe zuciyar shi yayi ya kalli CP amugun rude yace "stop, I said stop tracking d Goddamn number zata kashe min Pops" kafa yasa yawani irin tarwatsa laptops din jikinshi na rawa yana karajin yanda Abba ke ihu, dan kafa Big Mum tasa ta take inda ta harbai sabida yay ihu da kyau Ayaan yaji, Mami kam sumewa tayi ganin yanda big mum ta harbi Alhaji.
Wani irin dariya big Mum tayi ta mikama Bala dake kusa da ita bindigar ta zauna akan kujera ta daura kafa daya kan daya tana kallon fuskar Alhaji yanda wahala yau yasa tsufan shi yafito sosai dan da baka wani gani sabida cin dadi dakuma kudi, maganar Ayaan ne ya katse mata tunani, sosai muryan shi ke breaking yace "Big Mum please, please don't kill my Pops, andena tracking din kome kikeso I will do it amma kifara hadani dashi inji muryan shi if he's still alive shida Mami na sabida nayarda baki kashemin su ba, Pops" ya kwalama Abba kira ta wayan arude, Abba da kaman ya suma tsabagen azaba jin muryan Ayaan yasa yadan bude ido yana bin wurin da kallo, wani irin murmushin keta Big Mum tayi ta mikama Bala wayar bayan ta karbi bindigar tace "sashi awaya" karban wayan Bala yayi yawani finciko kan Abba kaman zai karya saida Abba yay Kara ya kara wayan a kunen shi da sauri Ayaan yace "Pops are you okay, zan bata koma me take so am going to save u, Popsy be strong for me okay, Ina mamina, a ina ta har...harbe..k" yakasa karashe maganan sabida kuka jin yanda Abba ke wani irin nishi, kukan shi yasa wani jarumta yazoma Abba yay murmushi yace "is okay my Boy am fine, karka sake kabama makirar nan dukiyata, dakabata dukiyata gwara ka zuba musu petrol ka kona, karka sake ka bata Bilkisu stay with your wife, don't give her anything, dan koka bata kasheka zatayi, da abu yasaman min kai Boy gwara in mutu, idan wanan shine saduwar mu takarshe na yafema kome kamin aduniyar nan, ga Mamin kanan she's unconscious" sosai Ayaan ke kuka ya kankame wayar a kirji yanajin muryan Abba, CP kuma yadauko wani sabon laptop suna kokarin tracking, Bala ne yazo zai fizge wayar Big Mum ta hanashi tana murmushi tace "barsu suna bidding farewell ne shima yasan he's not leaving here alive" wani irin kallon ta Abba yake cike da tsana saikuma yakara wayan abakin shi da wani irin mugun sauri dakuma karfin bala'i yace "Boy muna wani uncompleted buildi...." tus tus Big Mum tamai harbi har biyu akafar daman shi amma dayace ta shige shi, Bala kuma ya zubamai wani irin naushi ahanci dayasa ya sume warwas.
Tashi tsaye Ayaan yayi kaman mahaukaci yana ihu a wayan "Pops Pops Pooooopsss" yawani irin ja sunan kaman wanda ya zare, maganar big Mum yaji ta wayan tace "nabaka 15 minutes take Bilkisu, documents, da yarana zuwa kasuwar kwari wurin yan kaji ka ijiye su anan kajuy.." Ayaan da zuciyar shi kaman tafashe ta fito yamata wani irin ihu a haukace da intonation dinshi daya koma nayan Austria yace "f*ck yhu mah nigga, I said f*ck yhu, f*ck yhu mah nigga, f*ck, f*ck you b*tch, I will kill you, I gonna kill yhu, u kill my pops I will gonna yhu wallah" dip big Mum ta kashe wayan jin yanda ya haukace mata kirjinta na wani irin bugawa, hannu yasa ya fizge

bindigar dake cikin jakar bindiga dake jikin CP azuciye yajuya zai fita daga office din rikoshi CP da polisawan sukayi awani irin zuciye ya turesu dukan su suka zube kasa yafita amugun zuciye yana share hawayen dayake yi, su CP suka biyoshi kafin su fito harya bide wajen da kura.
♦♦ *SANGARTATTCE* ♦♦

Maman Abd Shakur

88...

Address din gidan ta dayagani adakin big mum yake son yaje gashi chan karshen garin kano ne address din gidan, hakan yasa yawani kara gudun hauka yana cikin gudun wayarshi ta shiga kara, dauka yayi batare daya kalli screen dinba muryan Musa yaji yace "hello abokina can u hear me" da kyar ya Iya yace "uh" cikeda murna Musa yace "yanzun nan daya daga cikin number Bala was on call hakan yabamu daman tracking down d location, I will forward d address to you now" ya katse wayar cikin one minute sako ya shigo gangarawa yayi yay parking hanunshi har rawa yake ya bude ya karannta sakon yafi sau uku ganin address din gidan big Mum daya gani dazu a file dinta ne, yasa ya kunna motar gabaki daya kure gudun motan yayi, cikin 35 minutes yakai wajen, daji daji ne duk ba'a wani gina filayen ba, hakan yasa yay parking yafito yarufe motar yabude booth, baida any weapon tsaki yayi yarufe booth din ya shiga dajin yana karanto addu'oin tsari, bawani dajin kirki bane, bishiyoyi ne kawai da ciyayi, yana gama wucesu yadan shiga ciki kadan saiga wani gida daduk shukoki sunbi jikin gidan, labewa yayi abayan bishiyan yana kallon gidan dan har yanzu gari dadan sauran haske, samari biyu ne awajen gidan suna zukan wiwi, tunani yafara me zaiyi yanzu, waige waigen yafara yana neman dan makami dan bayason ya harbe su, wani babban ishe ya hango akan yar bolan da aka tara awajen, takawa yay ahankali ya dauko iccen ya koma inda yake da, tsugunnawa yayi yadau dutse ya rike a hannu yana gyara zaman bindigar shi abayan wandon shi, yakara lekawa akaro nabiyu daya daga cikin sune yaga yataso yana bude belt din wando yana zuwa ta inda yake yana zage zip alamun fitsari zaiyi da sauri ya koma bayan bishiyar kusa da wacce yake daidai lokacin shikuma ya iso yaciro yana fitsari yana shafa ciki, fitowa Ayaan yayi daga bayan bishiyar ya daga itcen yawani irin makamai akai da karfin bala'i sai jini ko numfashin bai kara ba ya sume, zai fadi akasa da sauri Ayaan yatare shi gudun karya mai kara ya kwantar dashi a wurin ahankali kafin ya shige, har lokacin dayan na wurin yana zukar da dayan ya barshi, da rarrafe Ayaan yay wurin ya labe abayan motar big mum dake pake a wurin, dan lekawa yayi dakai yana gyara dutsen hanunshi yana wullawa sama yana chabewa, daddagewa yayi ya jefamai dutsen sai akan idonshi ba karamin bugamai ido yayiba saiga jini, da gudun bala'i Ayaan yafito yay kanshi kafin yabude baki ya sakin mai wani irin gula a jijiyan gefen wuyanshi ko numfashi bai karaba ya sume, kifeshi Ayaan yayi ya mikar dashi kaman mai bacci ya labe abangon wurin yana sauke ajiyar zuciyar, muryan Big Mum yaji daga ta Chan ciki tace "Bala jeka kirasu mana su gama shan wiwin su suzo suje su siyomana abinci Garba na najin yunwa" da sauri Ayaan ya tsugunna jin alamun tafiyar mutum yana kara gyara rikon iccen hanunshi, tsaki Bala dake fitowa yayi yace "amma isuhu anyi baho kagama zuka saikai bacci awurin" fitowa yayi danya tadashi

kaman daga sama yaji saukan abu a kanshi dafe wajen yayi idanunshi na juyawa ya juyo suka hada ido da Ayaan kafin ma yay magana Ayaan ya daga iccen da duka karfin shi tunawa dashine ya sacemai Baby sai kan fuskar shi yasami bakin shi da hancin shi kafin ma yakai katsa hakoran shi guda uku sukai kasa ya fada kansu asume, wani irin gyara wuya Ayaan yayi harsaida yay Kas Kas, yawani irin dunkule hannu yawani irin bankare yana twisting jiki, kasusuwan shi Sai Kas Kas suke, jijiyoyin kanshi sun fiffito yay taking long breath kafin yasaki yay cikin ya shiga cikin gidan sadaf sadaf babu kowa afalon daya gani saida bathroom slippers din Mamin shi, yana cikin bin wurin da kallo Pilot din Abba yafito daga wani daki yana zage zip din wandon shi baima lura da Ayaan ba sai cikin shi dayake shafawa yace "Hajjaju ta yakama ta mukara kiran yaron nan mu karbi dukiyar mubar ka..." saukar abu yaji acikin shi yasa yay shiru, bugamai iccen yake ta ko ina azuciye, karan da Big Mum taji yasa tafito daga dakin dasu Abba suke aguje, ganin Ayaan yasa takoma cikin dakin da gudun bala'i tana kiran sunan su Bala ,"Bala Bala, isuhu Isuhu" wani irin jefar dashi Ayaan yayi yay dakin yana tafiya kaman zai fasa kasa tsabagen yanda foot dinshi ke kara ya shiga dakin daidai lokacin Big mum ta saita bindiga akan Mami da idonta biyu Ayaan data gani take kallo cike da mamaki, ahankali ya kalli Abba alamun numfashi daya hango ajijiyar wuyarshi yasa ya sauke ajiyar zuciya, ya sauke idanunshi akan kafafun shi dasuke jini duka biyun har yanzu hancin shima jini, dawo da kallon shi yay kan big Mum da itama shi take kallo, ta daure fuska tace "wlh one more step saina kashe uwarka, kadaiga na baban kako" wani irin kallo yake mata, idanun Mami daya gani ta zaro tana nunamai bayan shi yasa ya juya da sauri yana ciro bindigar bayan shi Bala ne yataho da sharbebiyar wuka zai cakamai harbi ya sakinmai akafada hakan yasa ya zube awurin yana ihu, juyowa yayi ya saiti big Mum da bindigar yawani irin daure fuska. "drop dat Gun Ayaan, drop it" ko gezau baiyi ba daidai lokacin kuma motocin police sukai invading surrounding din bakajin komi Sai kukan motocin su dudda basu iso gidan ba, sosai jikin big Mum yafara rawa jin kukan motar police ganin haka yasa Mami ta bangajeta da kujeran da aka daureta akai baya tayi zata fadi bindigar hanunta ya fadi akasa saita kafarta Ayaan yayi ya harbeta kafin ya Kara Kara mata wani a cinya ta fasa ihu ta zube akasa da sauri Ayaan ya shigo dakin yawani irin take hanunta danhar karan karairayewan kashinta kakeji yay kujeran da Pops yake ya warware kullin da akamai yana tapping fuskar shi Pops, kwance Mami yayi da sauri ta mike tsaye itama tazo wajen Abba, rigar jikinshi ya cire ya barka ya rabata biyu, daure inda ta harbeshin yayi gam gam sanan ya daura hanunshi ata wuyanshi Mami ma tama dayan hanunshi haka suka daga shi kaman kaman yamutu, a rude Ayaan yake cewa "Pops stay with me, Pops" sukai hanyar fita dashi daga dakin harsun kai bakin kofa kaman ance ya juya kai daidai lokacin Big Mum tai pulling trigger a saitin Abba dake tsakiyan su, wani irin tura Pops Ayaan yayi da mugun karfi hakan yasa Pops yafada kan Mami dabata san meke faruwa ba suka zube kasa bullet din sai cikin Ayaan, da sauri yawani irin dafe wurin yana kallon fuskar Big Mum yana kokarin magana amma yakasa, sake pulling trigger tayi ta harbeshi acikin akaro na biyu yawani irin bankare, zatamai na uku CP yay pulling Ayaan dake tsaye abakin kofan baya, Polisawa sukai rushing big Mum da bindiga.

Karan bindiga ya farkar da Pops daga suman dayayi rass ya bude ido yana kallon yanda Polisawa suka zagaye wani dake kwance akasa, tureshi da Mami tashiga yi dan gabaki daya kanta yafado da kyar ya matsa gefe ta tashi arude tace "Ayaan, Alhaji look our son" tashi tayi arude ta ture polisawan dasuka zagaye Ayaan da kanshi kekan cinyar CP, ko numfashi mai

kyau bata kara fitarwa ba ta sume, jan duwaiwai Pops yayi yazo wajen yana kallon Ayaan da idanunshi ke lumshe, ahankali yabishi da kallo sai a lokacin yaga yanda cikin shi ke bulbul yana zubar da jini, CP ya daura hanunshi da jinin ya wankemai a wurin yana kallon fuskar Dr dake kan Ayaan, girgiza mai kai Dr yayi alamun bashi, wani irin karfi ne yazo ma Abba tashi yayi ya tsugunna ya karbe Ayaan daga jikin CP gabaki daya jikinshi ya saki, sakashi ajikin shi Pops yayi yana tsaki yana kallon fuskar Ayaan kaman mahaukaci ya kalli wani police yace "kai dalla bani ruwa suma dana yayi, Boy bazai mutu yabarni ba Yanzu bako Boy, bazaka mutu karbani ba" rigar da Ayaan yasa ya kullemai harbin da akamai akafa ya cire ya taushe inda big mum ta harbai yana ihu yana jijjiga Ayaan yace "kubani ruwa, kubani ruwa nace, dan Allah badan niba kubani ruwa" wani police ne ya mikomai ruwan gora, budewa yayi ya zubama Ayaan a fuska amma ko motsi, murmushi Pops yayi yace "Boy tashi mana banason wasan nan" sake zubamai ruwan yayi yasa hannu ya share ruwan daga fuskar shi yana tapping kumatun shi. "Boy, mah Boy wake up" bakinshi ya bude yana kokarin zubamai ruwan amma hakoran shi sun datse, wani irin nishi Pops yafara yana girgiza kai yace "Boyyy, Boy, Boyyy, Boy tashi kaji my one and only, Ayaan!" Pops yawani irin kirashi kaman mahaukaci, ahankali CP ya dafa mai kafada ya cire coat din jikinshi ya rufe fuskar Ayaan dashi, wani irin fizge rigar Pops yayi ya yar yay ihu yana kankame Ayaan yace "m..my Boy is not dead kadena rufemin shi, Boy Boy Boy wa..wake ke up.. Boy ka..tas..shi" fashewa yay da kuka jin jikin Ayaan yadau wani irin sanyi.
♦♦ *SANGARTATTCE*♦♦

Maman Abd Shakur

89...

*Wanan shafin nakine kawata Fido Sodangi*❤

*Sangartattce group I love each and every single member ciki, I appreciate the love. Allah barmin ku*

*kekuma gwuididi dakike watsawa waje weldone woo beratu, hankaka mai kama da kikito Ayaan*

*inka karanta baka biyaba kaida Allah*

*ke wanan zankala kokin kaman TAMACEN JIMINA dakike turo min da sako lemme make this announcement loud and clear, DUK WACCE TABIYA 200, SHE PAID 200 TO GAIN ACCESS TO MY NOVEL, TO BE ABLE TO READ IT, BAWAI TASAYI NOVEL DINA BANE, IF I WANT TO SELL NOVEL BAZAN TABA SAIDAWA DAT AMOUNT BA*

Dawani irin ihu ta tashi daga nauyayyen baccin datake yi da magriba nan, cikinta dataji yana mata wani irin zafi ta shafa saikuma tafara waige waigen dakin da babu kowa sai ita saikuma

kiraye kirayen sallan magrib dayacika unguwan, wani irin jumping tayi ta sauko daga gadon tai hanyar kofa batare databi takan hijabin taba, sauka tai kasa tana wani irin kuka tana kalle kalle babu kowama afalon, kofa tabude tafice da gudu tana kuka tai gate kasancewar masu gadi basu santa ba basu hanata fita ba da gudu tai waje tana kuka tana kalle kalle tana gudu, tai saman layi hanyar dazai sadata da titi zata fita daga anguwan daga ita sai doguwar rigan jikinta da black hula ko slippers babu akafarta sai uban kuka take, adaidai tabakin layin Aaman ya sanyo kan motar shi ciki kaman daga sama ya hango Bilkisu yanda take gudu tana kuka tana kalle kalle kana ganin ta kasan batasan inda kanta yakeba, parking yayi da sauri yafito yasha gabanta ganin ko lura dashima batayiba yace "Bilkisu ina zaki? Bakisan ko ina agarin nanba, mutafi gida" bangajeshi tayi tana kuka sosai zata gudu da sauri ya riko hanunta tawani irin fasa ihu tanaso ta fizge hanun tana neman cizon shi, janta yayi da karfi da yaji yasata amota yarufe yajuya ya shiga yaja motar yana kaiwa gate Mum da Ummy harda mai gadinsu suma sun fito hankalin su duk atashe, awajen yay parking yafito, mum takara so wajen da sauri tana kallon yanda take kuka, Bude kofar inda take tayi ta duko ta shafa fuskarta tace "maisa kike kuka haka daughter harkika fita, kodan bakiga kowa bane, salla mukeyi saisa zomuje gida" hanunta Mum takamo tafito da ita, daura hanunta daya tayi akan cikinta sosai take wani irin kuka sukai cikin gida da ita, da kyar Mum tasata tayo wanka Ummy tafito mata dawani simple riga tasaka duk sun damu, abinci ma Mum da kanta tabata sanan suka sata tai salla kafin abata maganin dare tana sha ba dadewa bacci yay gaba da ita sai uban ajiyar zuciya take saukewa, Mum ta kalli Ummy dake zaune gefenta tace "ki zauna da ita karta kara tashi taga bakowa" gyada mata kai Ummy tayi hakan yasa ta juya tafita daga dakin abakin kofar dakin taga Aaman ya tsaya ya jingina da bango yay shiru kaman mai tunani murmushi tamai tace "don't worry tai bacci, oya muje kaban labari how did d blood test go" dakinta ta shiga yabi bayanta, bowl din slice fruits dayagani akan bed din Mum ya dauka ya rike fork yadebo yakai baki saida ya shanye sanan ya kalli Mum yadan yatsine fuska yace "Mum I can't marry her, am even waiting for Dad yadawo sabida yakira parents dinta, we both are AS, AS, gaskiya I can't marry her is way too risky, banison na haifo yara sickla suzo duniya suyita wahala kullum muna hanyar hospital, thank God sef bawani sabawa mukayi da itaba, itama she's very cool with our decision mun janye zanxen auren dama tanada wanda takeso" gyada kai Mum tayi saikuma tace "kaifa?" dan lumshe ido yayi yadaura kanshi akan kafadarta, hanun tasa ta shafa sajen shi, ahankali yace "Allah zai bani wata mesona tagari Mum in sha Allah, aure lokaci ne dazaran lokacin yayi ko bacci nake saikun mini" kumatun shi Mum taja hakan yasa yay dan kara zaiyi magana sukaji wani irin ihun Bilkisu har cikin jinin jikinshi saida yaji ihun nan kafin ma Mum ta tashi shiya rigata yafita daga dakin ya bude dakin Ummi ya shiga, tana zaune kan gado sai uban kuka take rusawa hanunta akan cikinta, Ummy namata magana amma ko kallon ta batayi, ahankali yakaraso ta wajen gadon ya tsaya Mum na biye dashi hanunshi zube acikin ajihu ya kafeta da ido, dago kai tayi cikin kuka tana ganin shi takara fashewa dawani kukan tana nunashi da yatsa cikin kuka tace "ina...in..y...ina yake?" takara she magana tana kuka sosai, sassauta murya yayi ya girgiza mata kai yace "okay stop crying in kinaso nakira miki shi, zakiyi magana dashi?" da sauri ta dagamai kai tana goge kwalla tana lumlumshe ido tsabagen baccin dake fizgarta ta jinginar dakai jikin gado tana kallonshi, wayar shi yaciro daga aljihu dan shima yadamu da yanda take kukan nan, number Ayaan yaciro yay dailing harya gama ringing ba'a dagaba, sake dailing yayi har yagama ringing nanma ba'a dagaba, Mum ta kalleshi alamun andauka girgiza mata kai yayi yakara

dailing akaro na uku nanma ba amsa, dan kallon fuskarta yayi ganin tai bacci yasa yadan sauke ajiyar zuciya yakalli Mum da shi take kallo, ahankali yace "Mum am feeling somehow I hope he's fine, bari naje namai addu'a Allah ya kubutar da iyayen shi" Ameen Mum tace, fita yay daga dakin Mum kuma ta zauna abakin gadon tana tofa mata addu'a tana kallon yanda ta sanya hanunta daya akan cikinta ta danne tana yatsine fuska cikin bacci.

************************

Sosai Pops ke kuka, dago kanshi yayi asandaren ya daura akafadar shi ya kankameshi sosai yafashe dawani irin kuka mai tabarai, cikin kuka yace "tun inada shekaru ashirin aduniyar nan nai aure amma ban sami haihuwa ba, babu wani irin asibiti daban leka aduniyar nan ba, da wanda zanje nikadai da wanda zanje nida matayena amma duk maganun da likitoci zasu fadamin daya ce bana haihuwa" Bude idanunshi dake zubar da hawaye yayi ya kalli sama, cike da mugun rauni dawani irin muryan ban tausayi yace "har na cire rai na fidda tsammani, na hakura nacigaba da rayuwa kaman kowa, inada shekaru arba'in da biyar a duniyar nan Allah kamin kyautan wanan Yaron, kanuna min ba kudina zaibani haihuwa ba, kaine keda wanan ikon kuma aduk lokacin dakaga dama, ka sharemin hawaye na, kanuna mini duk wanda ya mika lamarin shi gareka tabbas ka isar masa, kamini kyautar Ayaan, kabani Ayaan" hawayen dasuka zubomai ya share tareda dago Ayaan daga kafadar shi ya kwantar dashi akan cinyar shi, yahade hannayen shi biyu yayi alamun roko yana kallon sama yace "Ya Allah, bazan tabaja da ikon kaba kai ubangiji nane duk hukuncin daka yanke min daidai ne agareni, duk duniyar nan kaikadai zan gayama bukatuna kabiya min su, Ya Allah ina mai tawasilli da sunayen ka kyawawa, Ya Allah kaine Al ahadus samadu lazi lamyalid walamyulad walam yakullahu kufwan ahad, Ya Allah kaine Al Hayyu Al Qayyum, Ya Allah kaine AL mutasarifu maijujjuya al'amura, Ya Allah na, badanni ba badan halinaba Ya Allah ina mai tawasilli da dukannin ayuyyukan alhairi danai aduniyar nan sabida kai Ya Allah, Ya Allah karkasa Ayaan yamutu yanzu, Ya Allah karka rabani da kyautar nan dakamin yanzu, Ya Allah ka tashi kafadar shi, Ya Allah, Ya Allah, Ya Ubangiji na..." Sai kuka kuma ya sake daga Ayaan daga cinyar shi ya sanya shi a jikinshi, jikinshi yay sanyi sosai ya rungume shi tsam tsam yana wani irin kuka mai sosai rai, polisawan ma sunkasa cewa komai dan suma jikinsu yay sanyi sosai idanunsu tab da kwalla, ahankali Abba yaji saukar numfashin Ayaan a wuyanshi dan kadan kuma a mugun hankali, wani irin ihu Abba yayi yaciro shi daga jikinshi yace "Alhamdulillah, Alhamdulillah, Allah na godema, Allah banda abin godiya saikai, Ya Allah thank you Ya Allah, my boy is alive, yarona is alive, mutafi asibiti" da sauri likitan dake cikin polisawan ya dubashi ya kalli CP dake kallon su yace "yes he's alive muje asibiti baya numfashi da kyau" karban shi akai daga hanun Abba, polisawan na murna suna "ashe doguwar suma ce" aka fita dashi shima Abba da bakin shi yakasa shiru sai "Alhamdulillah, Alhamdulillah yake" aka kinkime shi akai waje dashi, Mami ma haka, sanan kuma Big Mum mayya mai taurin rai harbi biyu gareta a hannu, biyu akafa, daya a kafadar haggun, dagata wasu polisawan sukayi suka sakata a motar su itada su Bala da Ayaan ya raunatar sukai asibitin polisawa da ita.
♦♦ *SANGARTATTCE* ♦♦

Maman Abd Shakur

90 - 91

*Momma!! You're Special!! I love the you in you!! I admire your courage!! Remember Allah is with you, u are not alone in dis journey, so let's keep fighting and pushing, you u will definitely reach dat spot dat I picture you to be. All it takes is patient u will overcome this phase of life my Momma*.

Bayan 2 weeks.

Babban dakine acikin asibitin, yana kwance akan gado sanye da white singlet da aka nannade sama kadan sabida bandejin dake cikin shi daidai inda aka ciro bullet din, saikuma dogon wandon jeans, Abba ne zaune kusa dashi da sandar dayake dogarawa yay tafiya dan tunda aka ciremai bullet din baya iya tafiya saida taimakon Sanda, saikuma Malam wanda yazo duba Ayaan yauda safe shida Raiyana dan kuka tadinga yi zata bishi ta dubo Bilkisu zuwan suma saisuka tarar da sabon labari, saikuma Baba Suleman dake zaune akan doguwar kujeran dakin, gabaki dayan su barin ma Abba yafi ramewa sosai sabida rashin lafiyan Ayaan, bugawa zuciyan shi yayi abinda ma yahana shi tashi har yanzu kenan dan sosai zuciyar shi tabugu sabida tashin hankalin daya shiga, inda akamai aiki kuwa harya soma warkewa wanda yauko gobe ma za'a cire bandejin gabaki daya.

Hankalin Abba sosai yake atashe dan basuga Bilkisu ba kuma duk wani gidajen su saida yasa aka duba koya boyeta awurinne amma babu ita, saisa addu'a kawai sukeyi Allah ya tashi kafadar shi yafada musu inda Bilkisu take.

Big Mum kuwa bayan ancire mata bullets din datasha, hanunta da Ayaan yataka yamata wasu irin karairaya ne da aka kasa gyarawa saidai aka guntule hanun gabaki daya, bayan kwana biyu aka shigar da case din kotu bayan all d evidence da lawyer dake kare Abba ya gabatar a kotu nan Alkali yay sentencing life in prison na yunkurin kinsan kai, kidnapping dakuma sauran crime dinta, taci kuka kaman idanunta su fito da guntulallen hanunta, lawyer Abba ya mikamata takardan sakin da Abba yabashi ya bata saki uku takara rushewa dawani kukan, suma su Bala duk prison din aka kaisu sai tsine ma Big Mum suke Wai ita tasasu awanan wahalan shiko pilot kuka wiwi, yanada aikin shi gashi alhaji na kyautata mai yabiye ma big mum gashinan abinda tajamai, kuka kam ya Shahi haka aka tattara su akai gidan yari dasu.

**********************

